# Wannan shi ne MUSULUNCI

Nazari Mai Zurfi Akan Addinin Da Ya Fi
Sauran Addinai Saurin Yaxuwa A Duniya





Hoton Musulmai wanda aka xauka ta sama, yayin da suka fuskanci Ka'abah, wadda Allah ya umarci Annabi Ibrahim ya gina ta, kuma ya umarci musulmai su fuskance ta lokacin da zasu yi sallah a duk inda suke.

THIS IS ISLAM

# Wannan shi ne MUSULUNCI

## Nazari Mai Zurfi Akan Addinin Da Ya Fi Sauran Addinai Saurin Yaxuwa A Duniya

Fahd Salim Bahamam

**Bugu na Farko**
**2021**

Haƙƙen Mallaka na Kamfanin
***Ad-Daleel Al-Mu'asir ne***



- **Ashe bai kamata a ce,** ka damu da ka san addinin da aka fi yawan jayayya a kansa a kafafen yaɗa labarai da ke kusa da kai ba?..
- **Ashe bai kamata a ce,** ka ɗan tsaya kaɗan ba, don ka samu cikakkiyar masaniya kuma mai zurfin game da addinin da ya fi kowane addini, aka kuma fi yawan karɓarsa, kamar yadda ƙididdigar duniya ta nuna?..
- **Ashe bai kamata a ce,** kana jin wani irin daɗi ba, a duk lokacin da ka san wani abu game da ilimi, da wayewa, da al'adu, da falsafa da tsarin rayuwar wasu mutane da suke rayuwa tare da mu a wata duniya, da wani addini?
- **Idan haka ne,** me zai hana ka ɗan yi amfani da damar da kake da ita, ka karanta wannan littafi domin ka san tantagaryar abin da addinin Musulunci ya ƙunsa, na gaskiya, wanda aka cirato daga ingantattun tuwasu da asullansa. Sa'annan ka auna su da lafiyayyen hankali da tatacciyar basirarka. Me zai hana?

Idan kuma kana hangen haka ko akwai wani abu mai muhimmanci a cikinsa, ko mai ɗaukar hankali. To, wannan ko shakka babu wannan littafi zai ba ka agaji da gudunmawa ga biyan bukatarka.




**Daga Ina Alƙur'ani Ya Zo?** — 82


Wannan tambaya ce irin ta hankali, wadda kai tsaye takan bijiro ma ƙwaƙwalwa a duk lokacin da aka yi magana game da Littafin Musulmi mai tsarki, wato, Alƙur'ani, da Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, cewa: Wai me ya sa ya zama wajibi a kan mu karɓar riwayar Musulmi da ta zo a cikin Alƙur'ani, game da wani al'amari na rayuwa? Ashe bai kamata gare mu, yin wannan tambaya a kan wannan lamari ba?

# Abubuwan da Ke **Cikin Littafin**


**Tambayoyin da Sukan Hana mu Bacci..** — 12
- Addinin Musulunci
- Ma'anar Kalmar Musulunci
- Musulunci Addinin Annabawa

**Musulunci Addinin Duniya** — 16
- Kula da Yanayi Yanki ne na Imani
- Addinin Ilimi
- Musulunci ya Shafi Dukkan Rayuwar Mutun
- Addinin Haɗin Kai da Zumunci

**Mahalicci Ɗaya… Abin Bauta Ɗaya** — 30
- Bambanci Tsakanin Dokokin Ɗabi'a Da Dokokin Shari'a
- Bamu Mai Rabon Gafara a Musulunci
- Ko Akwai Wasu Dokoki na Musamman Don Shiga Musulunci?

**Su Wane ne Manzanni a Haƙiƙa?** — 38
- Mutuntakar Manzanni
- Matsakaicin Matsayin Manzanni
- Matsayin Musulunci Game da Manzanni

**Matsayin Musulunci Game Da Isa, *alaihissalam*** — 42

**Wa Ye Manzon Musulunci?** — 48
- Takaitaccen Bayani a Kan ko Waye Manzon Musulunci, Annabi Muhammad *sallallahu alaihi wa sallam*

**Muhammad Manzon Allah Ne A Mahangar Masu Adalci** — 54

Kaɗan Daga Cikin Ƙissoshin Manzon Allah Muhammadu Da Halayensa — 60

- Kankantar Da Kai
- Jinkayi
- Adalcinsa
- Haƙuri Da Juriyarsa
- Kyautatawa Da Karamcinsa
- Gudun Duniyarsa
- Cika Alƙawarinsa

Wasu Daga Cikin Zantukan Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* — 70

Alƙur'ani Mai Girma Shi Ne Dauwamammiyar Mu'ujizar Musulunci — 76

- Kalubalanta A Harda
- Gagarabadau ta Fuskar Bayani da Janhankali

Daga Ina Alƙur'ani Ya Zo? — 82


- Tuhumce-tuhumcen Yau Da Gobe
- Me Zai Hana Mu Ɗauke Shi A Matsayin Gwarzo?
- Ko Dai Waɗancan Littaafan Ne Ya Canza Ma Tsari?
- Tantagaryar Gaskiya a Tarihance
- Suratul Fatihah

Ibadoji Da Sirrin Ma'anoninsu A Musulunci — 92

- Rukunan Musulunci
- Me Ya Kawo Takalifi Da Jarrabawa?
- Sallah
- Zakka
- Azumi
- Hajji

Iyali A Musulunci — 108

- Musulunci ya ƙarfafi yin aure da samar da iyali, ta hanyoyi kamar haka
- Musulunci ya ba wa kowane ɗaya daga cikin iyali cikakkiyar girmamawa, namiji ne ko mace
- Haka kuma Musulunci ya kwaɗaitar a kan gina harsashin girmama iyaye maza da mata, da ba su kyakkyawar kulawa, da biyayya da umarninsu har iyakar rayuwa
- Sa'annan kuma Musulunci ya yi umarni da kiyaye haƙƙin 'ya'ya maza da mata da wajabcin adalci tsakanin su a ciyarwa
- Ya kuma farlanta wa Musulmi sada zumunta



**Iyali A Musulunci** **108**

Mafi yawan iyali a wannan zamani namu, suna nufin tarayyar wani rukuni na ɗaiɗaiku, da suke amfani da makullin gida ɗaya, da suke zaune a ciki.



## Zumuntar Addini da Hankali

**134**

Wasu suna ganin cewar addini yana cin karo da hankali, yana kuma takinsaka da ilimi, saboda a nasu gani, addini ba komai ba ne illa maɓuɓɓugar tatsuniyoyi da miyagun al'adu.


**Matsayin Mace A Musulunci** — 114
- Ga Kaɗan Daga Cikin Hukunce-hukuncen Da Ke Magana A Kan Mutunta 'Ya Mace
- Matan Da Musulunci Ya Karfafa Kulawa Da Su
- Babu Filin Jajayya Tsakanin Maza Da Mata A Musulunci
- Alaƙa Tsakanin Namiji Da Macce
- Ɗabi'ar Alaƙar Namiji da Macce A Musulunci
- Ka'idodin Alaƙa Tsakanin Namiji da Macce Ajanabiyya
- Me Ya Sa Musulunci Ya Shar'anta Rufe Jiki Ga Mace A Gaban Maza Ajanabai?

**Dokar Musulunci Game Da Ci Da Sha** — 124
- Alade
- Giya Da Sauran Kayan Maye
- Yaya Alkur'ani Ya Yi Mu'amala Da Kayan Maye?

**Zunubi da Tuba** — 130

**Zumuntar Addini da Hankali** — 134
- Abubuwa Masu Barazana Ga Lafiyayyen Tunani Kamar Yadda Alkur'ani Ya Bayyana

**Musulunci Addinin Zaman Lafiya** — 140
- Musulunci Shi Ne Addini Mafi Saurin Yaduwa A Yau
- Me Musulmi Suka Aikata Lokacin da Suka Kama Sabbin Garuruwa?

**Tsakanin Musulunci Da Halayen Wasu Daga Musulmi na Yau** — 146
- Wata Sabuwar Farfajiya



# Tambayoyin da Sukan Hana mu Bacci..

Babu wani mutum ɗaya daga cikinmu, da zai iya bugun ƙirji ya rantse da Allah bai taɓa ɗan yin tsit a rayuwarsa, ya tambayi kansa ba, cewa: Me ye matsayina a wannan duniya? Wa ye ni? Daga ina na fito? Ina kuma zan tafi? Mece ce makomata bayan wannan rayuwa? Wai don me ma aka samar da gaba ɗayan wannan gida na duniya? Meye ma wai amfanin duk wannan kaiwa da komowa a rayuwa ta duniya, idan ƙarshe za a ƙare, a mutu, a koma ƙasa; a nemi mutum a rasa, sama ko ƙasa?

To, ka sani su dai Musulmi da sauran mabiya addinan da Allah ya aiko da su daga samaniya, sun yi imani da cewa, duk mutumin da yake rayuwa ba tare da ya yi imani da cewa akwai wanda ya halicci wannan duniya da abin da ke cikinta ba; Adalin Sarki. Bai kuma yi imani da cewa, akwai wata rayuwa, wadda a cikinta, mai mugun aiki zai haɗu da mugun sakamako da azaba ba. Duk wanda bai yi imani da haka ba, to, rayuwarsa aikin banza ce, da babu wata ma'ana a cikinta. Sakamakon haka kuma, zai yi ta ne ya ƙare cikin azaba da raɗaɗi irin na banza; babu wani sakamako. Kuma ya yi aikin banza.

Ba ya kuma yiwuwa a fahimci hikimar da take cikin matsalolin rayuwa, da kukakuran da ake yi a cikinta, da dace a gefe ɗaya, da sauran wahalhalu, sai idan an yi imani da cewa wannan halitta tana da Ubangiji, mai hikima, da yake gudanar da al'amurranta; ya kuma ƙaddara wa wannan rayuwa ta duniya ƙarewa. A wannan lokaci ne kuma kowane mutum zai samu sakamako gwargwadon abin da ya aikata.

Kuma a wannan lokaci ne mutum zai fahimci zuzzurfan imani, da gaba ɗayan ɗabi'u, da tsa rin rayuwa irin na Musulunci, waɗanda muke kira zuwa gare su, kamar adalci, da ƙauna, da tausayi, da gaskiya, da haƙuri, da rahama, inda rayuwa za ta ga amfaninsu. A lokacin ne kuma za a fahimci ma'ana da hikimar da suke tattare a cikin ƙalubalen rayuwa, za a kuma ɗanɗana daɗin sakamakon ɗa'a da biyayya ga Allah Maɗaukakin Sarki, haƙuri kuma, ya yi ranarsa.

Alƙur'ani mai girma, littafin Musulmi mai tsarki, ya yi ishara ga irin wannan tunani da muke magana a kan sa, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya ba mu labarin ma'abuta hankali da tunani, da cewa: *{Kuma suna tunani game da halittar sammai da ƙasa, Ya Ubangijinmu! Ba ka halicci wannan don wasa ba, tsarki ya tabbata a gare ka.} (A-li-imran : 191 ).*

## Addinin Musulunci:

Mafi yawan addinan duniya an ambace su ne da sunan wani mutum, ko wata alumma, ko wani gari da aka saukar da su a ciki. Masihiyyah an tsago sunanta ne daga sunan Annabi Isa *alaihissalamu*. Yahudiyyah kuma an ambace ta ne da sunan ƙabilar Yahuza ɗan Annabi Yaƙubu, *alaihissalamu*. Buziyyah kuwa sai aka jingina ta ga wanda ya assasa addinin, wato, Búza. A yayin da ita kuwa Hindusiyya aka ambace ta da sunan ƙasar Hindu (wato Indiya), da saurarsu.

A yayin da shi kuma Musulunci, ba a jingina shi ga wani mutum na musamman ba, ko wata ƙabila, ko wani jinsi, ko wata al'umma, saboda ba addini ne na wata al'umma guda ɗaya kawai daga cikin mutane ba, balle a jingina shi gare ta. Ba kuma wani mutum ne ya ƙirƙiro shi ba, balle a ambace shi da sunansa. Saboda haka iyakar sunan da aka san shi da, shi ne 'Musulunci'

## Ma'anar Kalmar Musulunci:

Idan muka koma ga asalin Kalmar 'Musulunci' kuma a cikin harshen Larabci, to, za mu taras yana da ma'anoni da yawa, da suka haɗa da: 'miƙa wuya' da 'ƙanƙan da kai' da 'ɗa'a' da 'tsarkin niyya' da 'aminci' da 'natsuwa.'

Saboda haka Musulunci shi ne miƙa wuya da cikakkiyar ɗa'a ga Ubangiji Mahalicci kuma Mamallakin komai, da kuma kuɓuta daga kowace irin bauta ga wanda ba shi ba, *subhanahu wa ta'alah*.

Wannan ita ce ma'anar da Alƙur'ani ya ƙarfafa a cikin ayoyi da dama.

Alƙur'ani ya ba mu labarin cewa, duk wanda ya bauta ma Allah Maɗaukakin Sarki da zuciya, da kuma gaba ɗayan gaɓoɓinsa; ya miƙa wuya ya kuma ƙanƙan da kai zuwa gare shi, ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi, da nisantar abin da ya hana. To, haƙiƙa ya kama hanyar shiriya, wadda ba ta yankewa, ya kuma samu babban rabo. *(Luƙman:22)*

Kenan, Musulunci tsintsar bauta ne ga Allah, da kuma 'yantuwa daga ƙanƙan da kai da bauta ga wanda ba shi ba. Cikakken Musulmi kuma shi ne mutumin da yake bauta ma Allah da zuciya ɗaya, yake kuma rayuwa cikin aminci, tare da yaɗa shi a tsakanin jama'ar da suke tare da shi.

Amma, tambaya a nan ita ce: Shin Musulunci shi ne addinin da gaba ɗayan Manzanni suka zo da shi?

## Musulunci Addinin Annabawa:


Alƙur'ani ya tabbatar da cewa dukkan al'ummomi na zamuna daban-daban, an aika musu Manzo don ya sanar da su addinin Allah. Wannan zancen ya zo ne ga Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, a cikin Alƙur'ani: *{Lallai mu muka aiko ka da gaskiya, kana mai bushara mai kuma gargaɗi; kuma babu wata al'umma face mai gargaɗi ya je mata.} (Faɗir: 24)*. Don haka dukkan Manzanni sun zo ne da addinin gaskiya, wato Musulunci. Ba su saɓa da juna ba a cikin saƙon imani, da tushen hukunce-hukunce, da kyawawan halaye.

Musuluncin da cikamakin Annabawa Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya zo da shi fiye da shekaru dubu ɗaya da ɗari huɗu (1400) ci gaban saƙon da dukkan Manzanni suka zo da shi ne, domin Alƙur'ani yana umartar Musulmi su yi imani da Manzannin da suka gabata, kamar Ibrahim, Is'haƙ, Ya'aƙub, Musa, da Isa. *Alaihimus salam (Baƙara : 136).*

Wani abu mai muhimmanci kuma shi ne, irin yadda Alƙur'ani ya ba mu labarin wasicin da Annabi Ibrahimu, *alaihissalamu*, kakan Annabawa, ya yi wa 'ya'ya da jikokinsa, haka nan kuma Annabi Yaƙuba ga nasa 'ya'ya da jikoki, a lokacin da suka kai gargara, cewa: *'Ku sani Allah ya zaɓar muku addinin gaskiya. Saboda haka kar ku kuskura ku bar Musulunci har mutuwa ta zo muku.' (Baƙara: 132).*

Saboda haka Musulunci cigaban addinin gaba ɗayan Annabawan Allah ne. Aƙidar ɗaya ce; babu wani bambanci a tantagaryar tushenta. Iyakar inda ake samun bambance-bambance shi ne a cikin tsare-tsaren shari'o'i, da ƙananan hukunce-hukunce gwargwadon yadda za su dace da sauye-sauyen zamani. Haka aka yi ta tafiya har zuwa lokacin da aka aiki cikamakin Annabawa da Manzanni, *Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallam*, domin ya ɗora harsashen Shari'a ta ƙarshe wa gaba ɗayan halitta.

Tun daga nan ne Alƙur'ani yake tabbatarwa a fili cewa, addini guda ɗaya ne rak, wato, Musulunci. Saɓanin da muke gani tsakanin addinan da suka zo daga sama a ɓangaren aƙidah ya faru ne sakamakon canje-canje da mutane suka shigar cikinsu, waɗanda su ne suka nisantar da su daga abin da Manzanninsu suka zo da shi na gaskiya. *(Ali imran : 19).*



# Musulunci Addinin Duniya

Wani

Wani abin ban mamaki shi ne rashin fitowar kalmar ‘arab’ wato ‘Larabawa’ a cikin Alƙur’ani tattare da cewa ya sauka ne da harshensu, kuma daga cikin su ne aka zaɓi Annabi Muhammad a matsayin Manzo. Amma kuma yau, Larabawa su ne adadi mafi ƙaranci a tsakanin Musulmi. Hasali ma ba su kai kashi ashirin (20%) a cikin ɗari na ƙididdigar yawan Musulmin duniya ba. Mafi girman ƙasa daga ƙasashen Musulunci ita ce Indonisiya, wadda take ƙarshen iyakar kudu maso gabashin Asia. Kai! Adadi mafi ƙaranci a duniyar Musulunci ma, da suke ƙasar Indiya kaɗai, ya kusa ninka yawan Musulmi a mafi girman daular Larabawa.

Wannan shi yake nuna cewa, addinin Musulunci ya zo ne a matsayin rahama da shiriya ga dukkan al'ummomin duniya tattare da bambancin wayewa, da yaruka, da al'adu, da wajen zama da yake tsakaninsu, kamar yadda ya zo a cikin Alƙur'ani cewa: *{Ba mu kuma aiko ka ba, face rahama ga halitta baki ɗaya} (Anbiya :107)*.


Musulunci yayi duba na musamman game da bambancin da yake tsakanin mutane ta hanyar da wani tsarin bai san da ita ba, wata ƙasa ba ta san da ita ba.

Ashe kuma ya kamata mu dubi wannan yanayi da darasi, da Alƙur'ani ya yi amfani da shi, na rashin yin magana da jinsin Larabawa ko Musulmi kaɗai. A maimakon haka sai yake magana da jinsin mutane gaba ɗaya ba tare da kula da bambance-bambancen jini da mazhabobin rayuwarsu ba. Tabbacin haka kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *{Ya ku mutane! Lalle mu mun halicce ku daga namiji da mace, muka kuma sanya ku jama'a-jama'a da ƙabilu don ku gane juna. Lalle mafi girmanku a wajen Allah shi ne wanda ya fi ku tsoron sa. Lalle Allah Masani ne, Kwararre.} (Hujrat :13)*.

Da wannan ne Alƙur'ani ya tabbatar cewa gaba ɗayan mutane asalinsu shi ne Adam da Hauwa'u, *alaihimussalamu*. Bambance-bambancen da suke tsakaninsu kuma, ba suna nufin fifita wani jinsi a kan wani ba ne, ko alama. Amfaninsu shi ne gane juna, da taimako a tsakaninsu. Fifiko da girma da ɗaukaka suna ga wanda ya bauta ma Allah ya kuma ji tsoron sa.

Hasali ma Alƙur'ani ya ja hankalinmu game da saɓanin launukan mutane, da yanayin ƙirarsu, da yawan yarukansu, da wayewarsu, cewa duk, yana cikin ni'imomin Allah da alamomin samuwarsa, da abubuwan ban mamakinsa a wannan duniya. Ya kuma sanya waɗananan bambance-bambance su zama wani ma'auni, na gane girman wannan halitta da muhimmancinta, idan aka kwatanta da halittar sammai da ƙasa. Sa'annan kuma babu mai hankaltuwa ya lura sai masu ilmi da tunani. *(Rum:22)*.

A lokacin da farkon shela mafi girma da duniya ta yi game da haƙƙin ɗan Adam da mutuncinsa, ya faru ne a 1948, aka fara amfani da shi daga baya. Shi kuwa Manzon Musulunci Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya yi irin wannan shela tun kafin shekara 1400 da suka wuce, lokacin da ya dasa wa 'yan Adam sabuwar rayuwa, inda yake cewa a huɗubarsa ta bankwana da mutane: *"Ya ku mutane, ku saurara ku ji! Lalle Ubangijinku ɗaya ne, kuma kakanku ɗaya ne. Don haka babu fifiko ga Balarabe a kan Ba'ajame, ko ga Ba'ajame a kan Balarabe, ko ga ja a kan baƙi, ko ga baƙi a kan ja, sai da tsoron Allah." (Ahmad 23489).*



**Muhammadu Manzon Musulunci**

Ya ku mutane! Ku sani Ubangijinku ɗaya ne, ubanku kuma ɗaya ne. Ku saurara ku ji! Balarabe bai fi Ba'ajame da komai ba. Haka Ba'ajame bai fi Balarabe da komai ba. Farar fata bai fi baƙar fata da komai ba. Haka nan baƙar fata bai fi farar fata da komai ba; sai da tsoron Allah.



**Sanarwar Duniya a kan haƙƙin ɗan Adam**

Wanda take tabbatar da zaman mutane ɗaya a cikin abin da ya shafi 'yanci, da haƙƙoƙi, da mutunci.

630m — 1948m

## Kula da Yanayi Yanki ne na Imani :

Wasu daga cikin malaman Falsafa sun ɗauki ɗan Adam a matsayin shugaban duniya, da ba shi da doka. Saboda haka zai iya sarrafa ta dai-dai da biyan buƙatunsa, ba tare da sa ido ko bincike ba, ko da hakan zai kai ga rusa wani yanki na duniya, ko halakar wani nau'i na halitta. A lokacin da wasu suke ganin mutun ba shi da bambanci da sauran halittu takwarorinsa. Hasali ma, wani jinsi ne kawai daga cikin miliyoyin jinsunan halittun. To, yanzu za mu duba mu ga irin matsayin da Musulunci ya ba mutun a wannan duniya da yake ciki.

Musulunci yana kallon mutum da alaƙar da take tsakanin sa da duniya baki ɗaya, da tabaran imani da tsare-tsaren da suka dace da tushen imanin. Ƙarshe sai ya shata masa waɗansu hukunce-hukunce da za su zama jagoran zamantakewa tsakanin mutum ɗin, da sauran dabbobi, da ƙasa ita kanta, da sauran halitta takwarorinsa.

Farkon abin da zai ja hankalin mai bincike a cikin wannan alaƙa, shi ne daidaton da Alƙur'ani ya tabbatar a tsakanin halitta, wanda a cikinsa Allah Maɗaukakin Sarki ya ɗaukaka mutun ya banbanta shi daga sauran halittu. (Isra'i:70), ya hore masa duniya da halittun da suka kewaye da shi, don ya amfana da su, ya kuma kula da su. (Ibrahim:32-33). A Musulunci, mutun ba wai kawai halitta ne kamar sauran halittu ba; babu wani bambanci da fifiko a tsakaninsu. Ba haka abin yake ba. A tsarin Musulunci, mutum halitta ce mai girma da ɗaukaka, duk kuma abin da yake cikin duniya, an halicce shi ne, don amfaninsa. (Baƙara :29).

Sai dai kuma a ɗaya ɓangaren, Alƙur'ani yana tabbatar mana da cewa, shi mutum ba wai shugaban duniya ba ne, da zai riƙa yin abin da ya yi masa daɗi. Sa'anan kuma wancan matsayi da fifiko da aka ba shi, a kan sauran halittu, ba zai ba shi damar ɓarna a duniya, da wargaza albarkatun da suke cikinta ba, domin ba mallakarsa ne ba. Mamallakinsu shi ne Allah Mahalicci. Iyakar matsayin mutun a wannan duniya, bai wuce na sanya shi da Allah ya yi ya zama halifa a cikinta ba. Ma'ana, an damƙa masa alhakin kula da ita, saboda haka yana da haƙƙin cin gajiya da moriyar abin duk da yake cikinta, a matsayinsa na wanda aka umarta da rayawa da bunƙasa ta, ba tare da cutarwa ko ɓarna ga mutun ba, ko waninsa daga cikin halittu. (Hud: 61, 30).


Shari'ar Musulunci ta shimfiɗa ɗaruruwan dokoki da bayanai daki- daki, don tsarawa da ƙarfafa alaƙa tsakanin mutun da halittun da suke kewaye da shi, ga misalai kamar haka :

## 1. Kula da Haƙƙin Dabbobi :

An samu bayanai da yawa daga bakin Muhammadu *sallallahu alaihi wa sallam*, da suke kira zuwa ga kare haƙƙin dabbobi, tare da tanadin lada mai yawa a gobe Kiyama ga wanda ya kyautata musu, ya kuma nisanci cutar da su, da kuma tanadin azaba mai raɗaɗi irin ta Ubangiji, a kan wanda duk ya cutar da su.

Wannan tanadi ya faru ne a lokacin da farkon ƙungiya mai kula da haƙƙin dabbobi, an kafa ta ne a Burtaniya a shekarar 1824 da sunan Jam'iyyar Masarauta Mai Kula Da Haƙƙin Dabbobi. Sa'annan, farkon dokar da aka sani a wannan ƙarni, da ta haramta ta'addanci ga dabbobi, an tabbatar da ita ne a Burtaniya a shekarar 1949. A yayin da shi kuwa Musulunci tun fiye da ƙarni 14 ya haramta ta'addanci ga dabbobi, ta bakin Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, kamar haramcin barin dabba da yunwa, ko azabtarwa, ko ɗora mata kayan da ya fi ƙarfinta, ko yin wasar da za ta cutar da ita, har duka a fuskarta, da sauran hukunce-hukunce waɗanda suka shahara a littafan fiƙhun Musulunci.

Mai yiwuwa ne, mai karatu zai ƙara fahimtar matukar kulawar da Musulunci ya yi da tausasa ma dabba, idan ya kalli zancen Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, inda yake labarta ma mutane cewa: *"Wata karuwa, (ɗaya daga cikin laifukan da Musulunci ya tsananta akan haramcinsu), ta ga wani kare ya yi kusa mutuwa saboda ƙishirwa, ta tausaya masa, ta cire takalminta, ta ɗebo ruwa da shi daga cikin rijiya, ta zuba masa ya sha, sakamakon haka sai Allah ya gafarta mata." (Buhari (3280).*



Doka ta farko da aka kafa a Ingila a kan zaman takura wa dabbobi, ta'addanci, ta faru ne a shekara ta 1949m

Kafa ƙungiya ta farko kuma domin kare haƙƙin dabbobi kuma ya faru ne a shekara ta 1824m

A yayin da Musulunci ya haramta hana wa dabbobi abinci, ko azabtar da su, ko ɗora musu kayan da ya fi ƙarfinsu, ko wasa da su ta hanyar mai cutarwa, tun shekara ta 632m

## 2. Kula da Tsirrai:

Musulunci ya kwaɗaitar game da kula da tsirrai da shuka, don maslahar ka ko waninka, ko don sauran halittun duniya!

Daga cikin irin wannan kulawa, akwai abin da Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, yake gaya mana cewa: "Babu wani mutun da zai yi shuka, ko ya sa hannu wajen tsirar da abin da zai amfani halitta, wani tsuntsu ya ci, ko mutun, ko dabba, face ya zama sadaƙa gare shi *(Bukhari : 2320)*.



Hasali ma kira Annabin rahama, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya yi ga Musulmi cewa, ko a cikin lokaci mafi wahala da tsanani, su yi ƙoƙarin bayar da tasu gudunmawa a cikin kula da yanayi, da cigaban ƙasa, da raya ta da tsirrai, ko da kuwa mutum yana da tabbatacin shi, ba zai ci moriyar abin ba, inda yake cewa: *"Idan Alƙiyama za ta tsaya, alhalin a hannun ɗayanku akwai irin dabino, to, ina horonsa da yin gaggawar dasa shi, idan yana da ikon yin haka, domin ya zama sadaka a gare shi." (Ahmad:12981)*

Ka ga yadda ya sanya raya ƙasa da bunkasa ta yana daga muhimman lamura da ibada waɗanda tsananin yanayi da tashin hankali baya hanawa ayisu.

## 3. Kula da Yanayi :


Musulunci ya tabbatar da muhimmancin kula da lafiyar yanayi, da nisantar gurɓatawa da ɓatawa da kuma yamutsa hazonta, inda ya samar da wani tsari cikakke wa mutane, mai taken: 'Rigakafi ya fi Magani.' Daga cikin tanade-tanaden wannan tsari da shiri kuwa, shi ne, tabbatar da muhimmancin kula da tsaftar jiki, da bayyana rukunanta filla-filla. Sa'annan muhimmancin kula da tuwasun albarkatun yanayi, da na tattalin arziki a lokacin da ake ƙoƙarin cin amfaninsu, da kuma haramta ɓatawa da gurɓata su. Misali a kan wannan shi ne:

- Musulunci ya haramta ɓarna wajen amfani da kowane irin arziki na ƙasa da na yanayi, musamman ruwa, ko da niyyar ibada ne kamar alwala, wato, wanke wasu keɓantattun gaɓoɓin jiki kafin a yi sallah.
- Ya kuma hana masu ƙarfin tuwo da na doka mamaye ababen amfani na ɗabi'a, ta yadda hakan zai zama cutarwa ga sauran jama'a. Don haka ya haramta mamaye ruwa, sabo da shi ne tushen rayuwa, ko wuta, saboda ita ce tushen ƙarfi, ko tsirrai, saboda su ne tushen abinci. *(Abu dawud 3477).*

> Haka kuma a Musulunci, kula da muhalli, da sadaukar da kai a cikin tsabtace shi daga ƙazanta, yana daga cikin imanin, kamar yadda Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya bayyana.

- Ya kuma yi hani da duk abin da yake ɓata yanayi a tsakaninmu. Misalin wannan kuwa shi ne, haramta yin fitsari a cikin ruwan da ba ya gudu, don kada ya gurɓata shi. Ya kuma hana yin ba-haya a cikin wurare masu inuwa, da a kan hanyoyi, a matsayinsu na wuraren da mutane suke zama da bi, ko matafiya suke ya da zango don hutawa.

Kaɗan kenan daga cikin irin waɗannan hane-hane. Ba kuma abin mamaki ba ne, a samu haka a cikin addinin da, Manzonsa mai girma, bai tsaya ga ɗaukar kula da tsaftace yanayi daga ƙazanta, da saka hannu a cikin gyara da kawar da ƙazanta daga hanyoyi, matsayin aiki na ƙwarai kawai ba. A'a, ya ma ɗauke shi a matsayin wani yanki na imani.



## Addinin Ilimi :

Ba da banza ba ka ga kalimar farko da ta sauka daga cikin Alƙur'ani, ga Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ita ce “yi karatu”. Hujjoji da daman gaske sun zo a cikin Alƙur'ani da zantukan Manzon Allah *sallallahu alahi wa sallam*, da suke nuna irin yadda Musulunci ya ƙarfafa tare da nuna muhimmancin gaba ɗayan fannonan ilimi mai amfani ga mutum, har ya ambata cewa hanyar ma duk da Musulmi zai bi don neman ilimi ɗin nan, ita ce hanyarsa zuwa Aljannah, kamar yadda Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *“Wanda duk ya kama wata hanya yana neman ilmi a kan ta, Allah zai sauwaƙe masa hanya zuwa Aljannah.” (Mulim :2699).*

A cikin wani awo da gwaji kuma, da Manzo, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya yi domin bayyana muhimmancin ilimi, cew ya yi: *“bambancin matsayi da ɗaukakar da ke tsakanin Malami, da mai ibada, kamar bambancin Manzo ne da mafi ƙarancin daraja a cikin mutane.” (Tirmizi :2685)*.

Don haka ne a Musulunci babu gaba tsakanin addini da ilmi kamar yadda abin yake a wasu addinai. Bai kuma yanke ma Malamai hukuncin kisa saboda wasu fatawoyi na ilimin kimiyya ba, kamar yadda hakan ta faru a waɗansu zamuna na duhun kai a wasu al'umomi. Hasali ma saɓanin haka, kacokam, shi ne abin da ya faru; addinin Musulunci shi yake haska hanyar ilimin kimiyya, tare da kira zuwa gare karatu da karantar da shi. Masallatai a duniyar Musulunci, su ne harsasan gini da bunƙasa ilimin kimiyya da sauran ilmoma, matuƙar suna da amfani ga rayuwar ɗan Adam.

Don haka ba za mu yi mamaki ba cewar mafiya yawan Malaman Musulunci masana ilimin kimiyya, sun fara rayuwarsu ta ilmi ne, da koyon karatun Alƙur'ani da hardace shi, da fahimtar ilimin addini, sannan suka shiga ƙirƙire-ƙirƙire masu zurfi a fannona da fagage daban-daban, da suke goge suka kuma yi fice a cikin su.

Ta tabbata a Musulunci cewa, Allah Maɗaukakin Sarki ya ɗaukaka darajar mutumin da yake karantar da mutane alheri a matsayin malami, ya ba shi matakai daban-daban, har Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam* ya ce: *“Lalle, gaba ɗayan halittu suna yin addu'ar alheri ga mai karantar da mutane alheri.” (Tirmizi:2685)*

**Da yawa daga cikin Malaman lafiyar yanayi, da likitanci na Musulmi, sun fara rayuwarsu ta ilimi ne, da neman ilimin Alƙur'ani, wanda ta hanyarsa ne suka haɓaƙa a cikin sauran fannonan ilimi.**

## Wasu Daga cikin Malaman Musulunci:

### 1. Khuwarizimiy (790 – 850, Bagdad):



Malamin lissafi ne da ƙere-ƙere da ilimin sanin taurari, wanda ya assasa lissafin algebra. Tuni aka tarjama littafansa zuwa waɗansu harasunan duniya daban-daban. A dalilin haka ne ma, kalmomin Larabci irin su 'al-jabru' da 'sifru' suka yi kaka-gida a cikin harshen Turanci.

### 2. Ibnul Haitham (965-1040, Alƙahira):



Masanin ilimin Fiziks da zane-zane, wanda yake da alaƙa da Jami'ul Azhar. Ya bayar da babbar gudunmawa wajen ilimin idanu. Shine farkon wanda ya ƙirƙiro na'urar Camera, har ma mafi yawan masu bincike sun tabbatar cewa ita kalimar Camera wanda haka ake kiran ta a mafi yawan yaruka, asalinta daga Larabci ne, wato 'ƙumrah' yana nufin ɗakin haske, wanda Ibnul Haitham ya ƙirƙira.

### 3. Albairúní (973-1048, a garin Khuwarizm):



Babban masani ne a fannin taurari. Shi ne kuma farkon wanda ya gano cewa, ƙasa tana zagayawa a matsuguninta, ya kuma ankarar da malamai a kan danƙon kasa (magnetism).



### 4. Zahrawy (936 – 1013, a Andalus):



shi ne sanannen likitan nan Musulmi, da ya ƙware a fannin fiɗa, wanda ya bunƙasa da wannan fanni har sai da ya siffanta, tare da ƙiƙƙiro ɗaruruwan kayan wannan aiki, a cikin littafinsa, waɗanda suka zama wata babbar manazarta a fagen ilimin likitanci da fiɗa, tsawon ƙarnuka bayan lokacinsa, a cikin harsuna daban-daban.

### 5. Ibn Sína (980-1037, a Bukhara):



An fi sanin sa da suna Abiccenna a duniyar ilimin likitanci, kuma shahararren Malamin Falsafa ne, wanda ya wuce zamaninsa ta hanyar ganowa da bayanin waɗansu curutoci, tare da bayanin maganinsu. Haka kuma yana da babban matsayi a duniyar awo da gwaji irin na ilimi, ta hanyar bincike-bincike, da nazarinsa na likitanci, waɗanda suka kai shi ga gano sakamako daban-daban masu zurfi, da babu su a zamaninsa, waɗanda kuma suka cigaba da wanzuwa har zamanin nan namu. An iya ganin haka ƙarara a cikin littafinsa 'Alƙanun' wanda aka ɗauki tsawon shekaru ɗari bakwai, babu manazartar ilimin likitanci kamar sa. Saboda haka aka cigaba da karantar da shi a Jami'o'in Turai har zuwa tsakiyar ƙarni na goma sha bakwai.

Bayan shaharansa a fannin likitancin kuma, sai ya shiga ba wa marasa lafiya magani kyauta, a matsayin gudunmawarsa ga jinƙayin ɗan Adam. Kai! Godiya dai ta tabbata ga Allah a kan ni'imar ilimi da sani.

### 6. Ibnun Nafis (1213-1288, a Dimashƙa):



Ɗaya ne shi daga cikin Malamai masana Shari'ah da Fikihu. A lokaci ɗaya kuma yana cikin sahun Malaman likitanci, da ilimin ayyukan gaɓoɓin jiki, da Tarihi. Shi ne farkon wanda ya ƙwanƙwance tare da gano yadda ƙananan ƙwayoyin halitta suke kai da komo, ya kuma yi bayani dalla-dalla. Ya samar da laƙunƙuna daban-daban a fagen likitanci, waɗanda har yanzu ana amfani da mafi yawansu.

## Musulunci ya Shafi Dukkan Rayuwar Mutun :

Da yawan mutane za su yi mamaki, idan suka ji cewa, koyarwar Musulunci ba ta tsaya a kan nau'o'in bauta ba, da wasu 'yan aikace-aikace, da darussan rayuwa na ɗabi'un yau da kullum, kawai, kamar yadda abin yake a mafi yawan addinan da suka sani.

A zancen gaskiya, Musulunci ba yana magana ne a kan biyan buƙatu na ibada ba ne kawai, irin waɗanda Musulmai suke yi a Masallatai ta hanyar yin Sallah da addu'a kawai.

Haka nan kuma ba wani ra'ayi ba ne, ko aƙidoji, ko wata Falsafa da mabiyanta suka yarda da shi ba, kawai.

Haka nan kuma, ba wani tsari ne na tattalin arziki kawai ba, ko na gina tsarin zamantakewa, mai cikakken tanadi.

Haka nan kuma, ba wasu ƙa'idoji ba ne, da nazarce-nazarce kawai, na gina al'umma..

Ba kuma ba wasu tarayyar ɗabi'u da halaye ba ne, na kyautata mu'amala, kawai.



Shi Musulunci, wani cikakken tsari ne da ya tattaro dukkan ɓangarorin rayuwa, tattare da yawa da faɗinta. Saboda haka babu wani ɓangare na rayuwar duniya, da Musulunci bai karaɗe ba, har ma da ƙari. Tare da haka kuma, bai dabaibaye mutane ya hana masu 'yancin walwala ba, idan aka yi la'akari da irin yadda ya sauwaƙe musu hanyoyin rayuwa. Hakan kuwa wata dama ce, ta mayar da hankali ga ƙirƙiro ababen jin daɗin rayuwa, da gina tarihi mai armashi, a matsayin wata ni'ima daga cikin ni'imomin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi ga bayinsa, kamar yadda Alƙur'ani ya tabbatar a cikin Surar *(Ma'idah:3)*

Hakan ta sa a lokacin da wani mutum ya yi nufin izgili ga sahabban Manzon Allah *sallallahu alaihi wa sallam*, sai ya kalli Salmanul- Farisi, ya ce masa: "Abokinku - yana nufin Manzon Allah - yana karantar da ku komai, har da yadda ake kama ruwa" Sai Salmanu ya karɓa masa da cewa: *"Wannan gaskiya ne; ya karantar da mu." Sai kuma ya shiga lissafa masa hukunce-hukuncen Musulunci da ladubbansa ga abin da ya shafi wannan buƙatu na kama ruwa da biyan buƙata ɗan Adam." (Muslimu:262)*

## Duniya da Lahira :

Misirawan farko sukan shafe jikin mamatansu da jar ƙasa, sa'annan su rufe su tare da gaba ɗayan dukiyarsu, bisa zaton cewa mamacin zai buƙace ta a halin rayuwarsa ta Lahira.

Su kuma Tibtawa, daddatsa gawar suke yi, su ɗora ta a kan manyan duwatsu don ta zama abincin tsuntsaye.



A yayin da Indiyawa ƙona ta suke yi, domin, a zatonsu ita ce hanya ƙwaya tak wadda za su iya kuɓutar da rayukansu daga wahala a bayan mutuwa.

Waɗannan 'yan misalai ne kaɗan, waɗanda ke nuna bambancin mutane game da mu'amalantar gawa, ko dai saboda bambancin zamani, ko gari, gwargwadon fahimtar da suka yi wa abin da zai faru bayan mutuwa, ta hanyar addininsu ko al'ada, wanda ke nuna akwai zurfafan tambayoyi da suke buƙatar amsawa game da haka a kewaye da su: Shin ko akwai wata rayuwa bayan an mutu? Idan akwai ta, to yaya take? Kuma me za mu buƙata ne a can?

Yin waɗannan tambayoyi ya zama wajibi tunda mutuwa wani al'amari ce, wanda kowane mahaluki ya yi imani da shi, babu togiya. Ko mun yi imani da rayuwar Lahira, ko tunaninmu ya taƙaita a kana abin da muke gani kawai, muke kuma iya ji da taɓawa da ɗanɗanawa. Haka kuma ko mun shirya ma wannan tafiya da take jiran mu, ko mun manta, mun kuma yi watsi da ita, ta hanyar wasanni da ababe masu ɗauke hankali.

Tambayar kuma da ta rage a yanzu ita ce, wadda take kawar da kowace irin gafala, da shagala, da mantuwa, take kuma yawaita bijirowa mutum a zuci a duk lokacin da ya ɗan nisa ya yi batun zuci, cewa: Shin idan mun mutu shikenan, babu wani abu da zai biyo baya? Samar da mu da Allah ya yi a duniya, wani nau'i ne na wasa kawai?

Wannan tambaya tana yawan faɗowa a tunaninmu, Alƙur'ani kuma yana yawan bijirowa da ita a cikin sigogi daban-daban. A lokaci ɗaya kuma yana ba mu labarin irin yadda mutane da dama za su samu kansu a cikin nadama, da hasara da taɓewa a ranar Kiyama, domin ba su tsaya sun ba wa kansu amsar wannan tambaya ba. Saboda haka suka kasa neman guzurin wannan tafiya. Sai ka ji wasu daga cikinsu suna cewa: *"Na shiga uku! Ina ma dai na yi ma wannan rayuwa wani tanadi?"* Can kuma sai wani ya ce: *"Ya kaicona! Ina ma dai in zama ƙasa." (Fajar:24/ An-Naba':40)*

Tabbatacciyar magana ce kuma sananniya cewa, gaba ɗayan waɗanda suka yi imani da wasu addinai na sama, sun yi imani da akwai wata rayuwa a Lahira. Sun kuma yi imani da akwai sakamakon lada da na azaba a cikin ta. Ba kuwa don komai abin ya zama haka ba, illa kasancewar zancen Lahira shi ne ƙashin bayan gaba ɗayan saƙonnin da Annabawa da Manzanni suka zo da shi. Sa'annan kuma lafiyayyen hankali yana yarda da cewa, rayuwa da addini ba su da wata ma'ana; haka kuma kyawawan halaye da ɗabi'u ba su biyan buƙata, matuƙar babu wata rayuwa



a Lahira, wadda za a yi hisabi a cikin ta, inda kowane mutum zai haɗu da sakamakonsa na alheri ko sharri.

Tare da haka kuma, da yawa daga cikin mutane suna tsammanin cewa, ba shi yiwuwa mutum ya yi addini da bauta, a lokaci ɗaya kuma ya nemi dukiya, ya ji daɗi, ya kuma cigaba. A nasu lissafi idan duniya ce mutum zai nema ya nema, in kuma Lahira zai nema to, amma ba zai yiwu ya haɗa su a tare ba a lokaci ɗaya, kamar yadda dare da wuni ba za su haɗu ba. Saboda haka wajibi ne hankalin mutum ya tsaya wuri ɗaya; nan ko can.

Mamakinsu ba zai ƙare ba. Zai kuma yi wahala ga wasu daga cikinsu, su yarda idan an gaya musu cewa, babu irin wannan wariya a tsakanin ibada da jin daɗi, misali. Ko tsakanin ibada da dukiya a cikin Musulunci. Haka kuwa al'amarin yake tunda Manzo, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya gaya mana cewa, *“Duk wanda ya yi aiki mai kyau, a kowane irin fage ne kuwa, matuƙar yana nufin alheri da shi, to, za a ba shi ladar aiki a lahira, ko da kuwa ƙaya ce ya kawar daga hanyar mutane; kar ta cutar da su. Ko lomar abinci da ya saka a bakin matarsa!”* (Bukhari:56).

Kuma a lokacin da Manzon Allah Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya bayar da labarin cewa, hanyoyin aikata alheri suna da yawa; ba za su ƙare ba. Bai rufe bakinsa ba, sai da ya faɗi wata hanyar, wadda ta ba wa Sahabbansa mamaki, in da ya ce: “Idan ɗayanku ya biya buƙatarsa tare da matarsa, za a rubuta masa lada”. Sai suka ce: “Menene alaƙar lada da biyan buƙatar sha'awa?” Sai ya ce: “Ku bani labari idan a ce ya biya buƙatarsa ta hanyar haram, ba laifi za a rubuta masa ba?' Sai suka ce: Haka ne. Sai ya ce: *“Saboda haka ne za a rubuta masa lada saboda ya zaɓi hanyar daidai don biyan buƙatarsa.” (Muslim :1006).*

Saboda haka ne, duk wanda ya fara nazari a kan Musulunci, tun tashin farko, zai fahimci yadda addinin ya ba rayuwar duniya da ta Lahira haƙƙinsu madaidaici, kamar yadda Alƙur'ani ya bayyana. A daidai lokacin da yake zaburar da mutane zuwa ga bautar Allah don samun lada a Lahira, yana kuma ƙarfafa musu ƙwazo a cikin neman falalar Allah a rayuwar duniya. *(Juma'ah: 9-10)* Ko duniya mutum ya nema, yana da lada, matuƙar ya yi hakan don Allah. Musulunci ya hori Musulmi su ƙulla niyyar bauta ma Allah iyakar ƙoƙarinsu a cikin ayyukan neman arzikin duniya, da tarbiyyar yara, da kula da lafiyar jiki da ta mazauni, da bunƙasa al'umma, kamar yadda Musulmi zai yi salla, da sadaka, da kuma azumi a matsayin ibada.

Wannan na ɗaya daga cikin sirrukan da suke samar da aminci da natsuwa da kwanciyar hankali a rayuwar Musulmi; jin cewa akwai nagartacciyar alaƙa a tsakanin rayuwarsa ta duniya da ta Lahira, da kuma jin daɗi da ibadarsa a hannu ɗaya. Saboda ta tabbata cewa, babu cin karo da juna a tsakaninsu, domin gini ne cikakke, da sashensa yake ƙara wa sashe ƙarfi.

Saboda tabbatar da wannan manufa ne, Alƙur'ani yake tabbatar mana da cewa, duk rayuwar Musulmi addini ce. Wannan kuma ita ce Falsafar Musulunci. Musulmi yana cewa: *“Rayuwata gaba ɗaya ibada ce ga Allah; ciki da waje. Ba salla da sauran ibadojina ne kawai na Allah. A'a, gaba ɗayan yanayin rayuwata, ina yin ta ne don neman lada da yardar Allah, domin shi ne Sarkin da zai auna ayyukana bayan mutuwata, ya yi mani sakamako a kai. Saboda haka babu wani motsi da zan yi, sai yadda Allah ya ce a cikin addininsa na Musulunci.” (An'am:162)*





## Addinin Haɗin Kai da Zumunci:

Ana ɗauka cewa bayanin da ɗan yawon buɗe ido Musulmi, Ahmad ɗan Fadhlan ya yi a mafi yawan yankin Rasha da Denmark, da daulolin Iskandanafiya, bayani na farko mai zurfi a kan haƙiƙanin halin rayuwar mutane, da ɗabi'unsu na yau da kullum, wanda duniya ta sani game da waɗannan ƙasashe.

Wannan kuwa ya faru ne a lokacin da Ahmad ɗan Fadhlan ɗin ya ɗauri aniyar wannan yawo mai ban mamaki, wanda a ƙarshe duniya ta ɗauka, yawo mafi muhimmanci na sadar da zumuncin ilimi da wayewa a matakin duniya, a cikin ƙarnuka na tsakiya. Ibnu Fadhlan ya tashi ne daga birnin Bagdada, hedikwatar ilimi da wayewa ta wancan lokaci. Daga nan ya cigaba da ratsa manyan birane, da ƙabilu, yana yi yana rubuta abin duk da ya gani, da waɗanda aka yi tare da shi a cikin wani babban kundi, wanda aka wallafa a karon farko, a shekarar 1923, wanda aka kwafa daga rubutun hannunsa, da aka samu a ƙasar Rasha.

Dalilin muhimmancin wannan rubutu na Ibnu Fadlan kuwa, kamar yadda Malamin nan Ba'amirke Michael Crichton ya faɗa, shi ne kasancewar Musulmi a Bagdada, duk da tsananin riƙonsu da addini, sun buɗe ƙofofinsu hayan-hayan ga sauran ƙabilu, waɗanda suka banbanta da su a tsarin sa tufafi, da ɗabi'a har ma da aƙida. A wannan lokaci, sun fi kowace al'umma a duniya ƙarancin ƙabilanci. Wannan shi ya ba su damar buɗe idonsu a kan al'adun jama'a daban-daban. (Michael Crichton Eaters of the Dead)

Musulunci yana kira ga haɗa hannu tsakanin gaba ɗayan al'uman duniya, a wajen gina ilimi da wayewa, kawo gyara, da cuɗanya da juna, da sada zumunci, ta hanyar mafi girma da ɗaukakar kyawawan halaye da ɗabi'u, tattare da bambancin wayewa, da addininsu. Yana kuma faɗakarwa da cewa, zaman 'yan marina da warewa nesa ga mutane, ba ingantattar koyarwar Musulunci ce ba. Don haka ne Manzon Allah Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya bayyana cewa: *“Wanda yake cuɗanya da mutane, yake hakuri da abin da zai same shi na cutarwa da kura-kuransu, ya fi wanda ya nisance su, ya ke kuma rashin haƙuri da su.” (Ibnu Majah :4032).*



# Mahalicci Ɗaya... Abin Bauta Ɗaya

## Alƙur’ani

Alƙur’ani yana tarbiyyar ɗan Adam a kan yi ma rayuwa adalci. A daidai lokacin da yake zaburar da mutane a kan bauta ma Allah don neman lada a Lahira, yana kuma ƙarfafa musu ƙoƙari a cikin neman falalar Allah ta duniya.

## Kalimar 'Allahu' a harshen Larabci tana da ma'anoni guda uku:

- Tana nufin abin bauta, wanda mutane suke tsarkake sallarsu da azuminsu, da fuskantar da zukatansu da dukkan ibadunsu zuwa gare shi.
- Tana kuma nufin Allah mai girman Zati, da siffofi, da ƙarfi, ta yadda hankula suke ɗimauta saboda girmansa, har su kasa tantancewa da ƙure sani a cikinsa.
- Tana kuma nufin Sarki, wanda zukata suke ɗamfare da shi, rayuka suke bege, suke kuma ɗebe kewa da ambatonsa, tare da jin daɗi da kusanta, da bauta masa.

Alƙur'ani yana tabbatar mana cewa dole ne, a fahimci Allah kyakkyawar fahimta, a kuma tsarkake shi daga dukkan canje-canje da ƙage-ƙagen da suke tawaye girma da ɗaukakarsa.

Allah, kamar yadda Alƙur'ani ya bayyana shi, shi ne Mahalicci kuma Maƙagin wannan duniya, mai kuma tsara al'amurranta. Duk abin da yake faruwa a cikinta, komai ƙanƙantarsa, shi ya halicce shi, da so, da ƙaddarawa da kuma saninsa yake faruwa. Babu wata mace, daga cikin gaba ɗayan halitta, da za ta ɗauki ciki, ko ta haihu, sa da so, da saninsa. Ɗigon ruwan sama ba zai sauka ba, ko wani canji ya faru a cikin yini ko dare, baɗini ko zahiri, a kowane ɓangare ne kuwa na halitta, face Allah yana sane da shi; shi ya ƙaddara faruwar hakan a matsayin wata rahama ga halittu. *(Fissilat:47/ An'am:59).*

Allah subhanahu wa ta'alah yana da siffofi mafi kyau da cika da kamala. Shi ne Sarkin da ba a rinjaya, mai rahamar da ta yalwaci dukan komai, mai girman da nakasa ba ta riskar sa ta ko wace irin fuska.

A lokacin da wasu suka yi imani da cewa, bayan da Allah ya halicci sammai da ƙasa a cikin kwana shida, sai ya shiga hutu a rana ta bakwai. Sai ga Alƙur'ani ya zo yana



Haka kuma Alƙur'ani ya tabbatar da cewa, kowane irin al'amari, yana faruwa da wakana ne da sani, da kuma ikon Allah Maɗaukakin Sarki, har kuwa da ɗigon kowane ruwa na sama, da faɗowar ganyaye daga jikin itace.



> Matsala mafi girma da zama narau-narau a idon Musulunci, ita ce wajabcin bauta ma Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai, da kuma zuciya ɗaya. Ita ce kuma fahimtar da gaba ɗayan Manzanni, alaihimussalam, suka yi ta kira zuwa gare ta, kamar yadda Alƙur'ani ya tabbatar.

rusa wannan mummunan zato nasu, yana faɗa da babbar murya, cewa: *{Lalle haƙiƙa, mun halicci sammai da ƙasa da abin da ke tsakaninsu a cikin kwana shida. Kuma babu wata wahala da ta same mu.} (Kaf:38)* Yana da kyau a fahimci cewa, babu abin da ya jefa wancan zato a cikin ƙwaƙwalen waɗancan mutane, face yadda suke kamanta Allah da sauran halittu a cikin ransu. Alhali kuwa Allah, subhanahu wa ta'alah, Mahalicci ne. Duk kuma abin da ba shi ba, sunansa 'abin halitta.' Babu kuwa yadda za a yi 'Mahalicci' ya yi kama da 'abin halitta.' Ko akwai? *{Babu wani abu da ya yi kama da shi. Kuma shi mai ji ne, mai gani.} (Shura : 11).*

Shi ne kuma mai hukunci na adalci, Sarkin da ba ya zalunci ko kaɗan. Abubuwan da muke gani na rayuwar yau da kullum, waɗanda yake ƙaddarawa, alamu ne da suke nuna mana miƙidarin hikima da jinƙayi irin nasa Maɗaukakin Sarki. Sai dai kamar yadda yaro ƙarami yakan kasa ganewa da fahimtar wasu kaiwa da komowa na mahaifinsa, balle ya fassara su daki-daki sakamakon bambancin matsayi da tunani da ke tsakaninsu. Kamar haka ne, hankalin ɗan Adam ba zai yi fahimtar wasu hikimomi na Allah ba, a cikin halitta da ikonsa.

Musulunci bai tsaya a nan ba, har sai da ya tabbatar mana da cewa furta imani da harshe kawai, ba ya sa imani ya zama ingantacce. Idan dai an yi imani da cewa, Ubangiji Mahalicci ɗaya ne tallin-tal. To, bai kuwa kamata a ce akwai wani abin bauta bayan shi ba. Saboda haka ba ya inganta a fuskanci wani, wanda ba Allah ba, subhanahu wa ta'alah, da wani abu na bauta, ko neman agaji. Wajibi ne a bauta masa shi kaɗai, ba tare da an bi ta kan wani mahaluki ba, ko an nemi cetonsa. Allah Mahalicci ya fi ƙarfin haka.

Idan Sarki ko wani shugaba a nan duniya, ba ya iya sanin mabuƙata ko masu rauni daga cikin mutanensa, balle ya iya kai musu ɗauki, sai ta hanyar mataimakon na kusa da shi, waɗanda aikinsu ne su sanar da shi halin da talakawa suke ciki, ya taimake su. To, ba haka Allah Maɗaukakin Sarki yake ba. Sarki ne shi, da ya san duk abin da yake gudana a ɓoye ko bayyane. Sarki ne Marinjayi, Mabuwayi, kuma Mamallaki, wanda gaba ɗayan halitta take a hannunsa; shi yake sarrafa ta. Duk abinda yai nufi, sai ya ce masa: 'zamo' nan take kuwa sai ya zamo… To don me za a ɗauki wani, wanda ba shi ba, abin bauta?

Ga shi kuma Alƙur'ani ya tabbatar da cewa, ba yadda za a yi Musulmi ya samu natsuwa da kwanciyar hankali, cikakke, matuƙar ba ga Ubangijinsa ya dogara ba, ta hanyar kai kowane irin kuka a wurin sa. Sarki ne shi, mai ƙarfin iko, mai kuma matuƙar son bayinsa, mai tausaya musu, Makusanci kuma gare su, wanda yake farin ciki idan

bayinsa sun ɗaga hannu sun roƙe shi. Yana kuma kuma karramawa tare da yi musu sakamakon alheri gwargwadon yadda suka dogara suka kuma nemi biyan buƙata a wurin sa. *(Baƙara:28/ Namli:62-63)*

Saboda haka ne, babu wani darasi a Musulunci, da aka yi bayaninsa dalla-dalla kamar wajabcin bauta ma Allah shi kaɗai da zuciya ɗaya. (Nahli:36). Alƙur'ani ya tabbatar mana da cewa, wannan matsala ita ce abin da gaba ɗayan Manzanni suka yi ta kira zuwa gare ta, cewa, babu wani Manzo, ko mala'ika, ko waliyyi, komai girmansa da tsoron Allansa, da ya kamata a kai wani kuma gare shi, komai ƙanƙantarsa kuwa, bisa hujjar cewa, ba a iya kai wa ga Allah sai ta hannunsu. Babu wannan a Musulunci, tunda ƙarshe kowa da komai Allah ne ya halicce shi; duk bayinsa ne. Shi kuwa Allah kusa yake ga bayinsa, yana jin maganarsu, yana karɓa roƙonsu matukar sun bauta masa da zuciya ɗaya.

Ya kuwa za a yi, wanda ya bauta ma Allah shi kaɗai, ba tare da ya raba hankalinsa biyu ko fiye da haka ba, ya kasa samun kwanciyar hankali da cikakken arziki! Tunda ba wani Mamallaki sai Allah, ba wani Mahalicci sai Allah, bai kamata a samu  wani abin bauta bayansa ba; wanda ake fuskanta, da fakewa a wurinsa shi kaɗai, subhanahu wa ta'ala, koma bayan waninsa.

Wannan shi ne abin da gajeruwar Surar nan, ɗaya daga cikin Surori mafiya girma da shahara a cikin Alƙur'ani, wato, suratul-ikhlas, take karantarwa.

### Suratul- ikhlasi:

Sura, wadda Allah ya umarci Annabinsa Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, da ya shelanta ta, kai ka ce amsa ce aka bayar ga mai tambayar wa ye Allah?

- Lallai Allah ɗaya ne ba shi da abokin tarayya a ibada.
- Allah shi ne wanda duk halittu suke dogaro da shi, suke kuma komawa zuwa  gare shi don biyan buƙatunsu.
- Lalle kuma shi, ya fi ƙarfin wani ya zama ɗa a gare shi, ko ya zama haifuwarsa aka yi shi. Shi ne na farkon da babu komai kafinsa.
- Allah ba shi da kishiya, ko tamka a Zatin da siffofinsa, domin shi ne Mahalicci. Duk abin da ba shi ba halittar sa aka yi.






## Bambanci Tsakanin Dokokin Ɗabi'a Da Dokokin Shari'a

Allah ya halicci wannan duniya da muke rayuwa a cikinta, tun farko, da wata ƙanƙanuwar ƙwayar halitta kamar ta cikin jikinmu, ya kuma kamala da wani tauraro mai nisan gaske, wanda na'urorin hangen nesa suka ci nasarar tsinkayowa da kyau, tare da gano cikakken tsari mai ban mamaki, da wannan tsarin halitta ya ƙunsa, wanda rayuwa a cikin wannan tauraro da muke ciki, ba ta yiwuwa, sai da shi. Sa'annan gaba ɗayan Malaman kimiyyar yanayi, sun bayar da tabbatacin cewa, da zarar aka gurɓata wancan tsari; ƙiris, to, hakan zai zama sanadin tashin duniya kwata-kwata.

Duk Musulmi ya yi imani da cewa, Mahaliccin da ya samar da wannan tsari mai bankaye, a cikin wannan irin siga mai tsananin kaifi da taka-tsantsan, shi ne kawai ya san dokokin Shari'a, da hukunce-hukunce, da tsare-tsaren rayuwar da suka fi dacewa da halittarsa. Addinin kuwa da ya zaɓar ma wannan halitta, shi ne tsari ƙwaya ɗaya tal, da rayuwar mutane take inganta da shi; ta samu tsira daga zaluncin sahensu zuwa ga sashe. Tabbacin hakan kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki a cikin Alƙur'ani cewa, ko shakka babu, wanda ya halicci duniya da mutane, shi ne kawai ya san abin da zai inganta rayuwarsu: *"Ashe wanda ya yi halitta bai sani ba, alhali shi mai tausasawa ne, kuma Masani." (Mulk:14).*



## Bamu Mai Rabon Gafara a Musulunci




Za mu iya lura da cewa mafi yawan addinai, sun ba wa wasu daga cikin mabiyansu muhimmanci fiye da wasu, ta yadda ibadoji da imanin mutane ba za su karɓa sunansu ba, sai sun samu yarda da amincewar waɗannan mutane. A tanade-tanaden waɗannan addinai, irin waɗannan mutane shafaffi da mai, su ne tsani, tsakanin Allah da mutane. Su suke bayar da lasisin gafara. A imanin masu waɗannan addinai ma, irin waɗannan mutane har gaibi sun sani, saɓa musu kuma wani abu ne da yake haifar da hasara mai tsanani.

Amma a Musulunci babu wani matsayi, wai shi 'bafaden Allah.' Allah ya riga ya ɗaukaka matsayi da darajar ɗan Adam, ya kuma 'yanta shi daga duk wani abu da zai mayar da shi bawa ya hana shi walwala a zuci, balle ya bukaci sai wani ya shiga tsakaninsa da Allah. Da wannan tanadi sai aka wayi gari arzikin mutum na duniya da Lahira, da tuba, da ibadarsa, ba ta da wata alaƙa da yarda da amincewar wani mahaluki irinsa, komai kuwa girma da ɗaukaka da zamansa mutumin kirki.

Haka kuma ya 'yanta shi daga bauta irin ta ilimi, wadda a cikinta ake gogen cewa, ilimin addini na wasu mutane ne na musamman, saura kuwa sai kallo da saurare. A maimakon haka, za mu ga cewa Alƙur'ani, bai ma tsaya ga shelanta cewa ilimi haƙƙin gaba ɗayan mutane ne ba, sai ma ya sanya shi a cikin abubuwan da suka wajaba a kan su, inda ya umarci gaba ɗayan Musulmi da karanta Alƙur'ani, da fahimtarsa, da bibiyar ma'anoninsa, sa'annan su yi aiki da shi. *(Swad:29)*

Saboda haka imani da ibada, abubuwa ne da suke tsakanin bawa da Ubangijinsa. Babu wani mutum da ya fi wani a wannan fage, balle ya zama tsani tsakanin bawa da Allah. Allah, *subhanahu wa ta'alah,* kusa yake sosai da bayinsa, yana jin addu'o'i da koke-kokensu, yana kuma karɓawa. Yana ganin bauta da sallar da suke yi dominsa, zai kuma saka musu a kan haka. Babu wani mahaluki da yake da ikon gafarta ma wani, ko karɓar tubarsa. Duk lokacin da bawa ya tuba ga Allah, tuba irin ta haƙiƙa, to, Allah ya yafe ya kuma gafarta masa. Allah kusa yake da kowa a duk lokacin da aka fuskance shi da wata buƙata, zai karɓa. Tabbacin wannan kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki a cikin Alƙur'ani: *"Kuma idan bayina suka tambaye ka a game da ni, gaya musu ni a kusa nike, ina karɓa kiran mai kira idan ya kira ni. Saboda haka, su karɓa kirana, su kuma yi imani da ni, tsammanin su, su shiriya." (Baƙara:186)*

> Musulunci ya karrama ɗan Adam ya kuma ɗaukaka darajarsa, ta hanyar 'yanta shi daga kowace irin bauta, da ta haɗa da 'bautar ruhi' ta yadda ba zai iya mu'amala da Ubangijinsa ba, sai wani ya shige masa gaba. Sai Allah ya haramta arzikin mutum, ko tubarsa, ko bautarsa, su zama damƙe a hannun wasu mutane tsiraru, komai kuwa daraja da addininsu.




> Saboda haka Alƙur'ani ya tabbatar ma duniya da cewa, Allah Maɗaukakin Sarki kusa yake da gaba ɗayan bayinsa. Duk lokacin da suka fuskance shi da wata bukata, yana ji.

### Ko Akwai Wasu Dokoki na Musamman Don Shiga Musulunci?

Babu wasu dokoki, ko wata tsatsuba, masu rikitarwa da Musulunci ya gindaya, kafin a iya karɓa da shiga cikinsa. Ba kuma sai a wani wuri na musamman, ko sai su wane suna nan ake iya karɓar sa ba. Iyakar abin da ake nema ga mutumin da yake son shiga Musulunci, shi ne furta 'Kalimar Shahada' tare da sani da imani da abin da ta ƙunsa, sa'annan kuma ya miƙa wuya da shika-shikai da rukunai da kuma ginshiƙanta manya da ƙanana. Wannan 'kalima' kuwa ita ce:

*"Ashhadu an lá'iláha illalláh:* Ma'ana, na yarda na kuma ƙudurce cewa, babu abin bauta da gaskiya sai Allah. Saboda haka, zan bauta masa shi kaɗai, ba tare da na yi masa kishiya ba.

*"Wa ashhadu anna Muhammadan rasulullah,"* Ma'ana, na kuma yarda cewa, Annabi Muhammad Manzon Allah ne zuwa ga mutane baki ɗaya. Zan bi umarninsa, zan nisanci abin da ya hana, zan kuma bauta ma Allah kamar yadda ya karantar.



# Su Wane ne Manzanni a Haƙiƙa?

Allah

Allah dai ya halicci bayinsa ne domin su bauta masa. Saboda haka ya aiko musu da Manzanni domin su sanar da su shari'o'insa, su kuma faɗakar da su a kan addininsa. Ba gyaran addini kawai ba, har al'murran duniyar mutane, su ne da alhakin ɗora su a kan tafarki madaidaici, su kuma jagorori nagari ga jama'arsu, ta hanyar ƙalubalantar duk wata karkacewa. Su ne za su riƙa kiran mutane zuwa ga hanyar gaskiya, domin kada su samu hujjar kafawa idan sun ƙi yin imani. To, mene ne haƙiƙanin waɗannan Manzanni?

## Mutuntakar Manzanni:

Alƙur'ani ya tabbatar mana, a cikin ayoyi masu yawa, da cewa, gaba ɗayan Manzanni mutane ne, da Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓa, ya damƙa ma saƙon wahayi da manzancinsa. Duk da yake akwai kamanceceya irin ta 'yan'adamtaka tsakaninmu da Manzanni, su, suna da wata daraja da ɗaukaka ta tsarki da nagarta. Bisa wannan dalili ne, Allah ya zaɓe su, ya ɗora masu nauyin isar da saƙon addininsa zuwa ga mutane, kamar yadda ya zo a cikin Alƙur'ani, cewa: "Ka ce: Ni mutum ne kawai kamar ku, da ake yin wahayi zuwa gare ni…" (Kahfi).

Saboda haka gaba ɗayansu Manzanni mutane ne, da ake haifuwa kamar yadda ake haifuwar kowane mutum. Sa'annan kuma suna mutuwa kamar yadda kowane mutum yake mutuwa. Suna rashin lafiya, kamar yadda suke yi, ba su kuma da wani tsari na halittar jiki, ko buƙatun rayuwa, da suka saɓa wa na sauran mutane.

Babu wani sanadari a cikin jiki ko ruhinsu, na Ubangizantaka, saboda Allah Maɗaukakin Sarki shi ne kaɗai Ubangiji. Matsayinsu bai wuce na zama wasu mutane, da ake yi ma wahayi ba, wato, saƙon Allah na isa zuwa gare su, ta hannun mala'iku, ko waɗansu hanyoyi daban.

Haƙiƙa al'umomin farko sun yi matuƙar mamakin wahayi, sai Allah ya rusa wannan mamakin nasu; ya nuna musu cewa babu wani abin mamaki a ciki, domin wannan ita ce hanya guda ɗaya tal, ta sadar da shiriyarsa da ilmantarwar addininsa zuwa ga halitta. *(Yunus :2).*

## Matsakaicin Matsayin Manzanni:


Zaɓen da Allah ya yi ma wasu daga cikin mutane, ya ɗora musu nauyin saƙon isar da manzancinsa, da sunan Manzanni, hakan ya ba su wata daraja maɗaukakiya a kan sauran mutane, ta fifikon nagarta da biyar umarnin Allah. Saboda haka ne Alƙur'ani ya sifanta su da zama shiryayyu, masu kyautatawa, nagartattu, zaɓaɓɓu, waɗanda kuma aka fifita a kan sauran halitta. *(An'am:84-87)*

Idan har wani Manzo ya aikata wani ɗan kuskure, to, Allah ba bar shi a kan sa ba. Sai dai ya faɗakar da shi don ya dawo a kan daidai, ya tuba daga wancan kuskure. Irin wannan kuskure na Manzanni kuma ba ganganci ba ne da ƙetare iyakokin Allah, sukan faɗa cikinsa ne a ƙoƙarinsu na ijtihadi da samar wa al'uma mafita.

Irin haka ne muke ganin Alƙur'ani yana sifanta Annabawa, sifantawa ta ƙarshe, ba tare da ya wuce wuri ya kai su inda Allah bai kai su ba, ba kuma tare da ya yi musu dimoshin ba. Tabbas! Suna da cikakkiyar kariya daga Allah tsakaninsu da ayyukan zunubi, manya. Amma, tattare da haka, wannan bai tayar da su daga zama mutane kamar kowa ba; su ba Allola ba ne, ba kuma 'ya'yan Allah ba. Babu wani abu tare da su na sanadarin allantaka ko Ubangizantaka.

Abin da zai fayyace mana hakan, shi ne yadda Allah ya hikaito irin tattaunawar da za ta kasance a gobe Kiyama, a cikin Alƙur'ani, don kuɓutar da Annabi Isa, *alaihissalamu* daga bautar da mutane sukayi masa, cewa: *{Ka ambata ya yin da Allah zai ce: Ya kai Isah ɗan Maryama! Kai ka ce wa mutane ku riƙe ni, ni da mahaifiyata ababen bauta guda biyu koma bayan Allah? Sai Isah ya ce: Tsarki ya tabbata gare ka, bai kamace ni in faɗi abin da ba ni da haƙƙi akai ba. Idan ma na faɗi hakan, to haƙiƙa ka sani. Domin, ka san abin da yake a raina; ni kuma ban san abin da yake a ranka ba. Lalle kai masanin duk abin da yake ɓoye ne. Ba abin da na ce musu, sai abin da ka umarce ni da shi, cewa: Ku bauta ma Allah Ubangijina kuma Ubangijinku. Na kuma kasance mai shaida a kan su matuƙar ina cikin su. Yayin kuma da ka kashe ni, kai ne mai kula da su. Lalle, a kan komai, kai masani ne.} (Ma'idah :116 – 117).*

> Duk wanda yake da masaniya da abin da Alƙur'ani ya ƙunsa, ya san cewa ayoyi da yawa daga cikinsa, da sunan Annabawa ake ambatonsu, kamar Surar Ibrahimu, da ta Yusuf. Karewa da ƙarau ma, har sura sukutum Allah ya ambata da sunan Maryamu tsarkakakkiya, mahaifiyar Isa, *alaihissalamu.*



## Matsayin Musulunci Game da Manzanni:

Wasu mutane na zaton cewa, babu abin da yake a cikin Alƙur'ani sai ƙissoshin Manzon Allah Annabi Muhammadu, *sallallahu alahi wa sallam*, da labaransa. Saboda haka sai kansu ya ɗaure, idan suka fahimci cewa, Alƙur'ani ya ambaci sunan Annabi Isah, *alaihissalamu*, har sau ashirin da biyar (25) domin girmamawa ga al'amarinsa, da kuma wanke shi daga miyagun zarge-zargen da aka yi masa. Ya kuma ambaci sunan Annabi Musa, *alaihissalamu* shi kuma har sau ɗari da talatin da shida (136), a yayin da bai ambaci sunan Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* ba, wanda aka saukar ma da shi Alƙur'ani, illa sau biyar (5) kacal.

Amma, mafi yawan mabiya wasu addinai, ba su yarda da abin duk da ba shi da alaƙa da addininsu ba, har ma wasu daga cikinsu, suna ƙiyayya da sauran Annabawa. A daidai wannan lokaci, duk wanda ya karanta Alƙur'ani zai ga irin yadda ayoyi da yawa, suka tabbatar da cewa, mutum ba zai zama cikakken Musulmi ba, sai idan ya yi imani da gaba ɗayan Annabawa. Inda kuma zai kafirce ma ɗaya tal, daga cikinsu, ko ya yi kokwanton ingancin manzancinsa, ko ya tuhumce shi da wani aikin ɓarna, to, ya fita daga Musulunci. Haka nan kuma Alƙur'ani ya tabbatar da cewa, Manzanni da waɗanda suka yi imani da su, sun yi imani da abin da ya zo daga wurin Allah. Saboda haka suka yi imani da Allah kansa, da Mala'iku, da Manzanni, ba tare da nuna ma ɗaya daga cikinsu wani bambanci ba. *(Baƙara:275)*



# Matsayin Musulunci Game Da Isa, *alaihissalam*

Isa

Tarihin duniya yana lissafa Annabi Isah *alaihissalamu*, daga cikin muhimman mutanen da suka bayar da gagarumar gudummawa ga cigaban ɗan Adam. Saboda haka ne mutane suka yi saɓani a kan matsayinsa. Wasu suka ce Allah ne shi, wasu suka ce ɗan Allah dai. Wasu suka kafa masa ƙahon zuƙa, suka zarge shi da miyagun tuhumce-tuhumce. To, shin mene ne matsayin Isah, *alaihissalamu*, a idon Musulunci?




**1.Annabi Isa Yana Daga Cikin Manyan Manzanni:**

Alƙur'ani ya tabbatar da cewa, Annabi Isah, *alaihissalamu*, na daga cikin manyan Manzanni masu girman daraja. Sa'annan kuma mahaifiyarsa Maryamu tsarkakakkiya, mai ƙanƙan da kai ce da bauta ga Ubangijinta, mai kuma kamun kai, da ba ta zubar da mutuncinta ba. Cikin da ta samu kuma na Annabi Isah *alaihissalamu*, ba tare da tana da miji ba, ya faru ne da izinin Allah Maɗaukakin Sarki, domin ya samar da wata wanzajjiyar mu'ujiza, kamar yadda ya samar da Annabi Adamu ba uwa, ba uba. Wannan, kamar yadda Allah ya faɗa ne a cikin Alƙur'ani cewa: Tabbas! Isah wata mu'ujiza ce wanzajjiya; kamar yadda Allah ya samar da Adamu ba uwa ba uba, haka ya samar da Isah ba uba, da ƙarfin ikonsa, wanda yake ce ma abu kun-fa-ya-kunu: *"Hakiƙa kwatankwacin Isa a wurin Allah kwatankwacin Adamu ne; ya halicce shi daga ƙasa, sa'annan ya ce masa ya zamo, sai ya zamo." (Ali'imrana:58)*

**2. Duk Musulmi Ya Yarda Da Mu'ujizozin Annabi Isa:**

Haka nan kuma babu wani Musulmi, da bai yarda da mu'ujizozin Annabi Isa *alaihissalamu* ba, waɗanda Allah ya gudanar a hannunsa, kamar warkar da kuturu, da makaho, da rayar da matattu, da ba da labarin abin da mutane za su ci, da wanda za su ɓoye a gidajensu. Duk waɗannan mu'ujizoji sun wakana ne da izinin Allah. Hakiƙa Allah ya sanya wannan ya zamo hujja ƙuru-ƙuru game da gaskiyar annabcinsa da manzancinsa.

**3. An Saukar Masa Da Littafin Allah Mai Tsarki, Injila:**

Alƙur'ani ya tabbatar da cewa, Allah ya saukar ma Annabi Isah *alaihissalamu* da ɗaya daga cikin manyan Littafansa, wato, Injila, domin shiriya ga mutane. Sa'annan kuma yau da gobe, sun haifar da waɗansu canje-canje da yamutse-yamutse a cikinsa.

**4. Annabi Isa Mutun Ne Ba Allah Ba:**

Musulunci ya tabbatar da cewa, Annabi Isa *alaihissalamu* mutum ne daga cikin 'yan Adam, wanda Allah ya ɗaukaka ya aiko shi a matsayin Manzo kuma Annabi ga Bani-isra-ila, ya kuma gudanar da waɗansu mu'ujizoji a hannunsa. Amma, babu wani sanadarin Ubangizantaka, ko Allantaka a tare da shi, kamar yadda Allah ya faɗa a cikin Alƙur'ani, cewa: Isah, ba kowa ba ne illa bawan Allah, salihi, da Allah ya yi ma ni'ima, ya ba shi mu'ujizoji, domin su zama wata alama ga mutanensa, da dalili zuwa ga alheri: *"Shi bai zamo ba face wani bawa, da muka yi ma ni'ima, muka kuma sanya shi abin misali ga Bani-isra'ila." (Zukhruf:59).*

**5. Ba A Gicciye Shi Ba, An Ɗaukaka Shi Ne Zuwa Sama :**

Annabi Isa a mahangar Musulunci, ba a kashe shi ba, ba a kuma gicciye shi ba, Allah ya ɗauke abinsa ne zuwa sama, lokacin da maƙiyansa suka yi nufin kashe shi. Bayan haka sai Allah ya sanya kamanninsa ga wani, su kuwa sai suka kashe shi suka gicciye, tsammaninsu Isah ne, *alaihissalamu*. Shi kam Isah, *alaihissalamu*, tuni Allah ya yi sama da abinsa, yana nan kuma da ransa, kamar yadda Alƙur'ani ya tabbatar: *(Nisa'i :157 – 158).*

## Bishiyar Annabawa :

Annabawan Allah suna da yawa, amma, ga waɗanda suka fi shahara da yin fice a cikinsu, amincin Allah ya tabbata a gare su:

### Adam:

Annabi Adamu, *alaihissalamu*, shi ne kakan mutane gaba ɗaya. Allah ya halicce shi ne daga ƙasa, ya kuma umarci mala'iku su yi masa sujjada. Karshe ya saukar da shi daga Aljanna zuwa duniya.

### Nuhu:

Annabi Nuhu, *alaihissalamu*, ya kira mutanensa zuwa ga Allah, amma suka kafirce. Sai aka yi musu azaba da ruwan ɗufana. Shi kuma ya tsira tare da waɗanda suka yi imani da shi, a cikin jirgin ruwa.

### Ibrahimu:

Annabi Ibrahimu, *alaihissalamu*, shi ne Baban Annabawa, ɗaya kuma daga cikin manyan Manzanni. Ya yi kira zuwa ga kaɗaita Allah da bauta. Shi ne farkon wanda ya gina Ka'aba, alƙiblar Musulmi.

### Isma'ila:

Annabi Isma'ila, *alaihissalamu*, ɗan Annabi Ibrahimu ne, *alaihissalamu*, ya kuma taimaki babansa wajen ginin ɗakin Ka'aba.

### Ishaƙa:

An haifi Annabi Ishaƙa, *alaihissalamu*, ne bayan Mala'iku sun yi wa mahaifinsa Annabi Ibrahimu, *alaihissalamu* bushara da samun sa.

### Ya'aƙuba:

Annabi Ya'aƙuba, *alaihissalamu*, ɗa ne ga Annabi Ishaƙa, *alaihissalamu*, ana kuma yi masa laƙabi da 'Isrá'ila,' inkiya, wadda Bani-isra'ila suke amfani da ita.

### Yusufa:

Annabi Yusufa, *alaihissalamu*, ɗa ne ga Annabi Ya'aƙuba, *alaihissalamu.* Ya fuskanci jarrabawa mai tsanani, ƙarshe kuma ya zama Sarkin Masar.



### Musa:

Annabi Musa, *alaihissalamu* ɗaya ne daga cikin manyan Manzanni. Allah ya aike shi ga Bani-Isra'ila, ya kuma saukar masa da Attaura, sa'annan ya ƙarfafe shi da mu'ujizozi. Sai Fir'auna, Sarkin Misra ya ƙaryata shi. Sakamakon haka, Allah ya halakar da shi a cikin ruwa. Annabi Musa, *alaihissalamu*, ya tsira, shi da duk waɗanda suke tare da shi.

### Dawuda:

Annabi Dawuda, *alaihissalamu*, Annabi ne da Allah ya ba shi mulkin mutanensa.

### Sulaimanu:

Annabi Sulaimanu, *alaihissalamu*, ɗa ne ga Annabi Dawuda, *alaihissalamu*. Annabi ne shi ma da Allah ya ba wa gagarumin mulki, ya kuma hore masa halittu masu yawa.

### Zakariyya:


Annabi Zakariyya, *alaihissalamu*, ɗaya ne daga cikin Annabawan Bani-israila. Shi aka ba wa riƙon Maryamu mahaifiyar Annabi Isah, *alaihissalamu*, don kulawa da tarbiya da iliminta. Allah ya yi masa kyautar ɗa Yahya, tattare da yawan shekarunsa da bakararancin matarsa.

### Isah:

Annabi Isah, *alaihissalamu*, ɗaya ne daga cikin manyan Manzanni. Allah ya halicce shi ta hanyar uwa, babu uba. Ya kuma aika shi wajen Bani-Isra'il, tare da saukar masa da Injila, sa'annan ya ƙarfafe shi da mu'ujizozi daban-daban.

### Muhammadu:

Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, shi ne cikamakin Annabawa da Manzanni. An aiko shi ne zuwa ga mutane gaba ɗaya, domin ya cika aikin da Manzannin farko suka fara. An kuma saukar masa da Alƙur'ani. Littafi, wanda ɓarna ba ta iya kai masa farmaki ta baya ko ta gabansa.




# Wa Ye Manzon Musulunci?

## Muhammadu

Muhammadu shi ne sunan Annabin Musulunci. Wannan suna kuwa ɗaya ne daga cikin sunayensa masu yawa, waɗanda suka shahara a bakin duniya a yau. Ma'anarsa kuma ita ce, wanda mutane suke gode ma, suke kuma yaba ma kyawawan halaye da ayyukansa.

## Sunansa:

Sunansa Muhammadu ɗan Abdullahi ɗan Abdulmuɗɗalibi ɗan Hashimu Baƙuraishe. Ya rayu a tsakanin shekarar 570 zuwa 632 Miladiyyah.

Gaba ɗayan Musulmi kuma sun yi imani da cewa:

## Manzon ne da Allah ya Aiko Zuwa ga Mutane Baki Ɗaya:

Ma'anar wannan kuma ita ce, Allah ya aiko Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* zuwa ga mutane baki ɗaya, ba tare da kula da bambancin jinsi, da dangantakarsu ba. Kuma Allah ya wajabta wa gaba ɗayan mutane yi masa biyayya. Tabbacin haka shi ne faɗar Allah a cikin Alƙur'ani da yake cewa: *{Ka ce ya ku mutane! Lalle ni Manzon Allah ne zuwa gare ku baki ɗaya.} (A'araf :158).*

## An Saukar Masa Da Alƙur'ani:

Sun kuma yi imani da cewa, Allah ya saukar ma Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, Littafinsa na ƙarshe kuma mafi girmansu gaba ɗaya, wato, Alƙur'ani, wanda ba yadda za a yi ɓarna ta kai masa farmaki ta baya ko ta gabansa.

## Cikamakin Annabawa da Manzanni:

Sun kuma yi imani da cewa, Allah ya aiko Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam,* ne a amatsayin cikamakin tsarin Annabawa; babu wani Annabi bayansa, kamar yadda Alƙur'ani yake faɗa cewa: *"Sai dai manzon Allah ne kuma cikamakin tsarin Annabawa." (Ahzab:40)*



## Taƙaitaccen Bayani a Kan ko Waye Manzon Musulunci, Annabi Muhammad *sallallahu alaihi wa sallam*- :

### 1. Haihuwarsa:

An haife shi a Makkah, yamma ga tsibirin Larabawa a shekarar 570 Miladiyya, a matsayin maraya wanda mahaifinsa ya cika. Ya kuma rasa mahaifiyarsa yana ɗan shekara shida. Saboda haka kakansa Abdulmuɗɗalib ya ɗauki ɗawainiyar kulawa da tarbiyyarsa. Sa'annnan ya koma hannun baffansa Abu Ɗalib, inda ya girma.

### 2. Rayuwa da Tasowarsa:

Ya rayu a cikin ƙabilarsa ta Ƙuraishawa tsawon shekaru arba'in, kafin daga bisani a aiko shi a matsayin Manzo (570-609). Ya zama abin buga misali saboda kyawawan halayensa da tsayuwar sa ƙyam a kan manufofin ƙwarai, har ya shahara a cikinsu da laƙabin *'assádikul-amin'* wato, 'mai gaskiya kuma amintacce. Ya yi sana'ar kiwon ƙananan dabbobi, sannan ya yi sana'ar fatauci.

Tun kafin bayyanar Musulunci Manzon Allah bai taɓa bauta ma gunki ba. A maimakon haka sai yake bauta ma Allah bisa koyarwar Annabi Ibrahim, *alaihissalamu,* ya yi watsi da duk wani abu na bautar gumaka, da duk abin da yake da alaƙa da ita. Tare da haka kuma shi ummiyyi ne, da bai iya rubutu ko karatu ba.

### 3. Aiko Shi a Matsayin Manzo :

Bayan da Manzon Allah ya cika shekara arba'in da haihuwa, alhali yana nazari tare da bautar Allah a kogon Hira' da yake kan dutsen Nur, ɗaya daga cikin duwatsun birnin Makka. Sai wahayi ya zo masa daga wurin Allah, ta hanyar fara saukar masa da Alƙur'ani. Farkon abin da aka fara saukar masa kuwa daga cikinsa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Ka yi karatu da sunan Ubangiji wanda ya yi halitta." (Alaƙ:1)*



**4. Fara Kiransa ga Mutane:**

Manzon Allah ya fara kira zuwa ga addinin Allah a ɓoye tsawon shekaru uku. Sa'annan ya bayyana kira a iyakar garin Makkah tsawon shekaru goma, ƙari a kan waɗancan. Mafi yawan waɗanda suka bi shi talakawa ne, da raunana, kamar yadda take faruwa ga sauran Manzanni. A tsawon wannan lokaci kuma, Manzon Allah da sauran muminai da suka bi shi, sun ɗanɗani nau'ukan cutarwa da gallazawa daga 'ya'yan ƙabilarsa ta Ƙuraishawa. Saboda haka sai ya tallata Addinin Musulunci ga ƙabilun da suke zuwa Makkah don aikin Hajji. Sai mutanen Madinah suka karɓa kira, ƙarshe sai Musulmi suka shiga yin hijira can sannu-sannu.

**5. Hijirarsa:**

Manzon Allah ya yi hijira zuwa Madinah, gari mai haske, wanda a wannan lokaci ake kiran sa "Yasriba" a shekarar 622 Miladiyya yana ɗan shekaru hamsin da uku, bayan waɗanda suka ƙi karɓar kiransa daga cikin shugabannin Ƙuraishawa sun ƙulla maƙarƙashiyar kashe shi. Ya rayu a Madinah tsawon shekara goma yana kira zuwa ga Musulunci, yana umarni da sallah da Zakka da attunetattun halaye da sauran shari'o'in Musulunci.




**6. Yadda ya Yaɗa Musulunci:**

Manzon Allah ya kafa hasasshen wayewa irin ta Musulunci a garin Madinah bayan hijirarsa (622 – 632), inda ya kafa duk wasu alamu masu samar da zamantakewa ta Musulunci, ta hanyar watsi da ƙabilanci, tare da yaɗa ilmi, da kafa tushen adalci da daidaito, da 'yan'uwantaka, da taimakon juna, da zama mai tsari. Ƙabilu da yawa sun yi ta ƙoƙarin rusa Musulunci a wannan lokaci, ta hanyar yaƙe-yaƙe, inda Allah ya taimaki Addininsa, da Manzonsa. Ƙarshe jama'a suka rinƙa shiga Musulunci; Makkah gaba ɗayanta tare da mafi yawan birane da ƙabilun Larabawa suka musulunta bisa zaɓin kansu, da kuma gamsuwarsu da wannan ƙasaitaccen addini.

**7. Rasuwarsa:**


A cikin watan Safar na shekara ta 11 bayan hijira, wannan kuma bayan da Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya isar da saƙo, Allah kuma ya cika ni'imarsa ga mutane ta hanyar cika musu addini. Sai zazzaɓi mai tsanani ya kama shi, *sallallahu alaihi wa sallam*, rashin lafiya ta tsananta a gare shi. A hantsin ranar litinin, 12 ga watan *Rabi'ul-auwal* shekarar hijira ta 11, wanda ya yi daidai da 8/6/632 Miladiyyah, Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam* ya kwanta dama yana ɗan shekaru sittin da uku. An binne shi a ɗakin matarsa A'ishah a kusa da masallacinsa.





# Muhammad Manzon Allah Ne A Mahangar Masu Adalci

Babu wani mutum mai adalci, ko wane irin ilimi kuwa yake da shi, da zai nazarci rayuwar Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, da kyau, face ya samu kansa cikin ɗimbin mamaki, a kan kowace gaɓa ta wannan gagarabadan labarin rayuwarsa. Don haka ne ka ga Malamai da masana Falsafa da Adabi, na gabashin duniya da yammacinta, sun tabbatar da hakan har ma sun rubuta a cikin littafai da maƙalusu. Cikin su har da:



### Mahatma Gandhi:

Mahatma Gandi ya faɗa a cikin jaridar Young India, 1924 cewa: “Na yi ƙoƙarin sanin siffofin Mutumin da ya mallaki zukatan miliyoyin mutane ba da jayayya ba, sai na yi matuƙar gamsuwa cewa, lalle ba da takobi Musulunci ya nemi matsayin da yake da shi ba. Ya samu wannan matsayin ne ta yadda Manzonsa ya rinka mu’amala da gaskiyar alƙawari, da nuna matuƙar ƙaunarsa ga abokai da mabiyansa, da sadaukantakarsa tare da amincewarsa da Ubangijinsa, da gamsuwa da manzancinsa. Waɗannan siffofi su suka share wa Musulunci hanya, suka kawar masa da wahalhalu, ba takobi ba. Bayan na ƙare karatun littafi na biyu a kan rayuwar wannan Manzo, sai na samu matuƙar damuwa saboda rashin samun ƙarin sani game da rayuwarsa mai girma, a kan wanda na yi.”

> *“Da na so in san sifofin mutumin nan da ya mallake zukatan miliyoyin mutanen duniya, ba tare da wata jayayya ba. Sai na gamsu da cewa, ba da kaifin takobi ne Musulunci ya yi amfani ya samu ɗaukaka a duniya ba.” {Ghandi}*

An ciro wannan jawabi daga cikin kundin Cikakkun Ayyukan Mahatma Gandi mai suna: Collected Works of Mahatma Gandi, juzu’i: 25, shafi:27.




### Michael H. Hart:

Michael H. Hart ya faɗa a cikin shahararren littafinsa mai suna: Mutane Ɗari Masu Girma A Tarihi. Malamin ya fara ne da sunan Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, a matsayin wanda ya fi ragowar, tare da bayyana dalilinsa na zaɓarsa a farko inda ya ce: Lallai zaɓin da na yi wa Muhammad ya zama shi ne na farko a muhimmanci da girma a mazajen da tarihi bai ga irinsu ba, zai ba wa masu karatu mamaki. To amma fa, shi ne mutum ɗaya tilo a tarihin duniya, da ya cimma mafi girman nasara a addini da duniya.”.

A cikin littafinsa mai suna: The 100: A Ranking Of The Most Influeintial Persons In History, shafi na:3,






### Alphonse De Lamartrine:

Shararren mawaƙin nan ɗan ƙasar Faransa, Alphonse ya faɗa a cikin littafinsa mai suna: Histoire De La Turkuie, juzu’i: 1, shafi:111, cewa: “Ko shakka babu, ƙarfin niyya, da raunin kayan aiki, da girman sakamako, su ne alamomin gagarabadan namiji. To, babu kuwa wanda zai yi rashin adalcin kwatanta Annabi Muhammadu da wani mahaluki komai girmansa kuwa a tarihi, a wannan fage. Ko akwai shi?



### Ramakrishna Roa:

Malamin nan masanin Falsafa, ɗan ƙasar Indiya, Ramakrishna, yana cewa a littafinsa mai suna: “Muhammad The Prophet Of Islam, shafi: 24, cewa: “Tattare da irin yadda al’amurra suka canza kacokam, Muhammadu bai canza ba; nasara ko faɗuwa, ɗaukaka ko tsanani, wadata ko rashi; shi dai ne Muhammadun da aka sani, babu ɗaya daga cikin sifofinsa da suka canja. Ba kuwa shi kaɗai ba, haka Allah ya nufa ga gaba ɗayan Annabawa, tsarin halittarsu ba ya canzawa har abada.”



### Goether:


Mafi girma daga cikin Mawaƙan ƙasar Jamus, Goether yana bayar da labarin yadda ta wakana gare shi, a cikin wata wasiƙa da ya rubuta ma masoyiyarsa, yana bayyana mata irin yadda Musulunci da Annabi Muhammadu suke burgewa da ba shi mamaki, ya ce:

“Duk da yake ya kai shekara saba’in a duniya, amma har yanzu bai gushe ba, Musulunci yana ba shi sha’awa. Hasali ma kullum abin sai ƙara haɓaka da bubuta yake yi kamar wutar daji a cikin zuciyarsa.” Catrina Momzone ce ta bayyana haka a kan Goethe und die arabische Welt, a cikin nata littafin, shafi:177.

### James W. H. Stobart:

Farfesa James ya bayyana cewa, “Babu wani mahaluki ɗaya a cikin tarihin ɗan Adam, da za a iya kwatantawa ko kusa, da Annabi Muhammadu. Tattare da ƙarancin abin duniya a hannunsa, amma, ya kafa wata irin jaruntaka, wadda babu irin ta. Idan muka yi nazarin tarihi ta wannan mahanga, to, lallai kuwa ba za mu samu suna mai irin wannan haske da sauƙin fahimta kamar na wannan Annabi Balarabe ba.” (Islam And Its Founder: 227-228).

## Simon Ockley:



Simon Ockiey ya faɗa a cikin littafinsa mai suna: "History of the Saracen Empire" shafi:45 cewa: "Ba yaɗuwar Musulunci da bazuwarsa ne abin mamaki ba, irin yadda aka kasa ganin baya gare shi tsawon zamuna shi ne abin mamaki. Dubi irin yadda har yau dashen da Muhammadu ya faro a garin Makka yake cigaba da kama ƙasa a cikin zukatan mutanen Indiya, da Afrika, da Turkiyya, waɗanda Alƙur'ani ya je musu a matsayin baƙon haure.

**"Har yau kyakkyawan tasirin da Muhammadu ya ɗora harsashensa a Makka da Madina, yana nan da wannan matsayi da ƙarfi a cikin zukatan Indiyawa, da Afirkawa, da Turkawa, waɗanda ba su daɗe ma da sanin ko me ye Alƙur'ani ba." {Simon Okly}**

## Will Durant:



Will Durant yana cewa a cikin shahararren littafinsa mai suna: The Complete Story of Cibilisations:

"In za mu yi hukunci game da duk wani mai girman da ya yi tasiri cikin mutane, cewa za mu yi: Tabbas! Muhammad shi ne mutun mafi girman masu girma, wanda ya yi tasiri a tarihin duniya, domin ya ɗora ma kansa nauyin ɗaukaka matsayin al'ummarsa ta bangaren ruhi, da ɗabi'u da halaye, wanda ɗumamar yanayi, da mamayar sahara, suka rikita. Haƙiƙa ya cim ma burinsa irin cim ma burin da duk wani mai gyara a tarihin duniya bai samu ba. Zai yi wahala mu samu mutumin da ya cim ma dukkan burin mafarkinsa, irinsa… Lokacin da ya fara da'awa, tsantsar sahara ce a tsibirin Larabawa, mazauna cikinta ƙabilu ne masu bautar gumaka, ba yawa gare su ba, kawunansu ba a haɗe suke ba. Amma, ya rasu ya bar ta a matsayin al'umma ɗaya mai cikakken haɗin kai, ya muƙurƙushe bambance-bambance da shaci-faɗi, ya kafa sassauƙan addini mai ƙarfi, wanda ya haɗiye Yahudanci da Kiristanci da daɗaɗɗen addinin garinsa, ta hanyar ɗabi'u masu haifar da mutunci da ƙima ga mutanensa. Ya samu nasarar yaƙoka da yawa, ya kafa daula mai girma a cikin ƙarni ɗaya, wadda ƙarfinta ya wanzu ya mamaye rabin duniya har wannan lokaci namu."

An ciro wannan jawabi daga cikin littafinsa mai suna: The Story Of Cinilization: The Age Of Faith, sashe:4, shafi:173.



Haka nan kuma, Hercules, Sarkin Rum a shekara ta 628, da ya bayar da wani labari mai ban mamaki, bayan ya musulunta, a matsayinsa na ɗaya daga cikin manyan maƙiyan Annabi Muhammadu, *sallallahu a alaihi wa sallam,* a can da, cewa: "Lokacin da saƙon Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam* ya je masa, yana kiran sa zuwa ga Musulunci, sai mamaki ya kama shi. Sai ya nemi a zo masa da ɗan ƙasar larabawa, da yake da masaniya da kusanci da wannan Manzo. Sai aka ci karo da Abu Sufyan ya je ƙasar Sham don kasuwanci. A lokacin kuma yana ɗaya daga cikin shugabannin Kuraishawa mafiya tsananin ƙiyayya ga Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*. Sai aka gayyato shi tare da gaba ɗayan waɗanda suke tare da shi zuwa fada. Hercules ya yi musu tambayar ƙwaƙwaf a cikin hikima da tsabar wayo, ta hanyar wani mai fassara, don ya gane gaskiyar manzancin Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ko rashin ta. To, a lokacin da ya ji irin amsoshin da Abu Sufyan ya ba shi, sai ya amsa masa da cewa:

"Na tambaye ka nasabarsa (matsayin gidansu), ka ce: Mai nasaba ne a cikinku. Da ma kuma Annabawa ana aiko su ne daga cikin mafi ɗaukakar gidaje. Na tambaye ka cewa wani ya taɓa irin wannan da'awa a cikinku? Ka ce: A'a. Da wani ya taɓa yi da sai na ce: Yana kwaikwayon waɗanda suka gabace shi ne."

"Na tambaye ka cewa: Kun taɓa tuhumarsa da ƙarya? Ka ce: A'a, sai na fahimci cewa ba zai yiwu yaki yi wa mutane ƙarya ba, sa'annan kuma ya yi wa Allah!"

"Na tambaye ka game da mabiyansa; manyan mutane ne ko ƙanana? Ka ce: ƙanana ne. Dama kuma haka mabiya Manzanni suke. Na tambaye ka ƙaruwa suke yi ko raguwa? Ka ce: ƙaruwa suke yi. Dama haka lamarin imani yake har sai ya cika."

"Na tambaye ka: Ko ɗayansu yana yin ridda bayan ya shiga? Ka ce: A'a. Dama kuwa haka imani yake, lokacin da ya cakuɗu da zukata."

"Na tambaye ka: Ko yana yaudara? Ka ce: A'a. To, haka Manzanni suke; ba su yaudara.

"Na tambaye ka game da abin da yake umartar ku da shi, mene ne? Ka ce: Yana umartar ku da bauta ma Allah, kar ku haɗa shi da komai. Yana hana ku bauta ma gumaka, yana umartar ku da sallah da gaskiya da kamun kai."

"Idan abin da ka faɗa gaskiya ne, to sai ya mulki nan inda na taka. Dama na san zai bayyana, amma ban tsammaci a cikinku yake ba. Da na san zan iya haɗuwa da shi da na yi matuƙar ƙoƙari" (Bukhari :7).



# Kaɗan **Daga Cikin kissoshin Manzon Allah Muhammadu Da Halayensa**

Gaba ɗayan masana masu adalci, a gabasci da yammacin duniyar Turai, kuma magabtasa, sun bayyana cewa, Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, shi ne kankat a fagen kyawawan halaye da ɗabi'u irin na 'yan'adamtaka. Wanda saboda haka ne, Alƙur'ani ya sifanta halayensa da zama 'maɗaukaka.'

Yayin da aka tambayi matarsa A'ishah, *radhiyallahu anha*, game da halayensa, *sallallahu alaihi wa sallam*, ba ta samu sifa mafi ƙwanƙwancewa da za ta dace da sifofinsa ba, ban da cewa: "Alƙur'ani shi ne halayensa." Tana nufin, idan ana son a ga Alƙur'ani a aikace, to, a kalli halaye da ɗabi'unsa, *sallallahu alaihi wa sallam*.

**Wannan kaɗai ya isa bayar da hoton rayuwa da yanayin halayensa, *sallallahu alaihi wa sallam,* a taƙaice.**

## Ƙanƙantar Da Kai :


Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam,* bai yarda a miƙe tsaye don a girmama shi. Hasali ma kashedi ya yi ma Sahabbansa daga yin haka. Saboda haka, duk da tsananin ƙaunar da suke yi masa, ba su miƙewa tsaye idan suka hango shi yana zuwa. Ba kuma wani abu ya sa haka ba, illa fahimtarsu da cewa ba ya so. *(Ahmad :12345).*

Wata rana Adiyyu ɗan Hatim ya zo wurinsa, *sallallahu alaihi wa sallam*, kafin ya musulunta. A matsayinsa na ɗayaa daga cikin mutane masu mutunci a cikin Larabawa kuma shugabanni, yana so ya san haƙiƙanin wannan addini da Annabi Muhammadu yake kira zuwa gare shi. Sai Adiyyu ya ce: *"Bayan na zo wajen sa, sai na tarar da shi da wata mace, da wasu yara guda biyu, da na ga irin yadda ya ba su damar kaiwa kusa da shi, sai na tabbata cewa, shi ba irin Sarakunan Farisa ko Ruma ba ne." (Ahmad :19381).* Ƙanƙantar da kai ɗabi'ar dukkan Annabawa ce.

Manzon Allah yakan zauna a cikin sahabbansa ba tare da nuna wani bambanci ba; kai ka ce matsayinsu ɗaya. Saboda irin yadda yake ƙyamar zaunawa wani wuri na musanman bamban da waɗanda ke tare da shi. Hakan ta sa baƙo, idan ya zo, ba zai gane wane ne Annabi ba, balle ya iya rarrabewa tsakaninsa da Sahabbansa. Karshe dole ya tambaya: Wa ye Annabi Muhammadu a cikin ku? *(Bukhari :63)*.

Ɗaya daga cikin Sahabbansa yake bayar da labarin cewa, duk da irin yadda yake da ayyuka masu ɗimbin yawa, Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*. Hakan ba ta taɓa hana shi tafiya wurin biyan buƙatun wasu mutane komai ƙanƙantarta ba. Har Mace kuyanga daga cikin matan Madina kan zo ta kira shi don wata buƙata tata, kuma ya tashi ya tafi don ya biya mata ita. (Bukhari:5724).

> Manzon Musulunci ya kasance yana gyara kayayyakinsa da kansa, yana kuma kama ma iyalansa aikin gida.



Sahabi mai girma Umar ɗan Khaɗɗabi ya bayar da labarin shigarsa wata rana wajen Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, inda ya ga kwancin tabarma a kuiɓin Manzon Allah, sai kawai ya fashe da kuka. Sai Annabi ya ce masa: *"Kukan me kake yi?" Sai Umar ya ce: "Ya Manzon Allah! Sarkin Farisa da na Ruma suna cikin ni'ima da daula, kai fa Manzon Allah ne! Amma, mu bar ka a haka? Sai ya ce wa Umar: "Ba ka son a ba su duniya, mu kuma a ba mu Lahira?" (Bukhari:3503).*

Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, shi da kansa yake zaunawa ya gyara duk wani abu nasa da ya lalace. Yakan kuma kama ma iyalinsa 'yan aikace-aikace. Da aka tambayi matarsa A'ishah game da rayuwarsa a gida, sai ta ce: *"Yakan kama ma iyalinsa 'yan aikace-aikace." (Bukhari:644)*. Har sai da ma ta ƙara bayani da cewa: *"Kamar yadda ɗayanku yake yi; yakan gyara takalminsa, ya ɗinke tufafinsa da kansa." (Ahmad :24749).*

Shi da kansa, Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, yake cewa: *"Duk mai girman kai a zuciyarsa kwatankwacin ƙwayar gero, ba zai shiga Aljanna ba." (Muslim:91).*

## Jinƙayi :


Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Allah Sarkin rahama yana jinƙayin duk masu jinƙayin bayinsa. Saboda haka ku ji tausayin bayinsa da ke ƙasa tare da ku, shi kuma da yake sama sai ya ji tausayin ku" (Abu Dawuda:4941)*.

Jinƙayin Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam* yana bayyana a fili ƙarara, idan aka kalli ɓangarora masu yawa da suka haɗa da:

### Jinƙayinsa Ga Yara :

- Tattare da cewa sallah ita ce ginshiƙin addini, wadda zance a cikinta, ko yawan motsi ba ya halatta. An samu cewa wani lokaci Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, yakan yi sallah yana ɗauke da jikarsa Umamah 'yar Zainab. Idan zai yi sujada sai ya ajiye ta a ƙasa. Idan kuma ya miƙe sai ya ɗauke ta. *(Bukhari : 494).*
- Idan kuma yana sallah ya ji kukan yaro, sai ya gaggauta ya sauƙaƙa ta, kamar yadda ya bayar da labari, *sallallahu alaihi wa sallam*, cewa: *"Da yawa nakan fara sallah da niyyar zan tsawaita, idan na ji kukan yaro, sai na taƙaita sallar tawa, gudun kar in takura wa mahaifiyarsa" (Bukhari :675).*





**Jinƙayinsa Ga Mata :**

- Ta tabbata cewa, Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam* ya kwaɗaitar da al'umarsa kulawa da yara mata, da kyautata musu. A kan haka ne yake cewa: *"Duk wanda Allah ya arzuta da 'ya mace ɗaya ko fiye, ya kula da tarbiyyarsu, ya kuma kyautata masu, to, za su zama shamaki tsakaninsa da wuta." (Bukhari : 5649).*
- Kai! Sai da ma ya tsananta a cikin wasicci a kan kiyaye haƙƙoƙan mata, da kula da al'amurransu, da lura da yanayin halitta da ɗabi'arsu, ya kuma umarci Musulmi da yi ma junansu wasicci da hakan, da cewa: *"Ku umarci junanku da yi ma mata alheri." (Bukhari :4890).*
- Ya kuma buga kyakkyawan misali, sallallahu alaihi wa sallam, ta hanyar kyautata ma iyalinsa, inda ta kai har yakan durƙusa wajen raƙuminsa ya saka gwiwarsa ƙasa, matarsa Safiyyah, radhiyallahu anha, ta taka ta hau kan raƙumin. *(Bukhari : 2120).*
- Duk kuma lokacin da 'yarsa Fadimah, *radhiyallahu anha*, ta zo wajensa, sai yakan kama hannunta ya sumbance ta, ya zaunar da ita a inda yake zaune. *(Abu Dawuda:5217).*

**Jinƙayinsa Ga Masu Raunana:**

- Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya kwaɗaitar da mutane a kan kula da maraya, yana cewa: *"Ni da mai kula da maraya a aljanna, kafaɗa da kafaɗa."* Yana faɗi yana nunawa da ɗan manunin yatsansa da na tsakiya, tare da buɗawa tsakanin su kaɗan. *(Bukhari :4998).*
- Ya kuma bayyana cewa, matsayin mai taimaka ma gwauraye da talakawa, daidai yake da matsayin mai jihadi saboda ɗaukaka kalmar Allah. Haka kuma shi da wanda yake yini azumi ya kwana tsaye yana sallah, duk ɗaya a wurin Allah. *(Bukhari :5661).*
- Manzon Allah ya bayyana cewa tausaya ma masu rauni, da ba su haƙƙoƙinsu, dalili ne na yin arziki, da cin nasara a kan maƙiya, kamar yadda ya ce: *"Ku nemo mani raunana, domin ana taimakon ku da azurta ku a sakamakon tausaya ma raunana daga cikinku." (Abu Dawuda: 2594).*



Manzo Muhammadu, ya sanya kusantowa da masu rauni, da kyautata musu, wani sanadi na samun nasara da arziki.



## Adalcinsa:

- Duk inda mai adalci ya kai, Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya wuce nan, saboda irin yadda yake zartar da hukuncin Allah ko a kan mafi kusancin danginsa gare shi, domin cika umarnin Alƙur'ani da ya ce: *"Ya ku waɗanda suka yi imani! ku zama masu tsayar da adalci, masu shaida ga Allah, ko a kan kawukansu, ko mahaifa da makusanta." (Nisa'i:135)*
- Wani daga cikin Sahabbai ya zo wurin Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, yana neman alfarmar, kada a zartar ma wata mata mai alfarma a wata ƙabila, da ta yi sata, hukuncin Shari'a. Sai Manzon Allah ya ce masa: *"Na rantse da wanda raina yake a hannunsa, da Faɗimah 'yar Annabi Muhammadu za ta yi sata, wallahi da na yanke hannunta." (Bukhari:4053).*
- A lokacin kuma da aka haramta ma mutane cin Riba, sai Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya fara da mafi kusanci a gare shi wato baffansa Abbas, yana mai cewa: "Farkon ribar da zan rusa ita ce ribar Abbas ɗan Abdulmuɗɗalibi; duk na rusa ta." (Muslim:1218).
- Sa'annan kuma ya bayyana cewa, mizanin da ake gane al'umma ta ci gaba, shi ne a wayi gari mai rauni daga cikinsu yana karɓar haƙƙinsa daga mai ƙarfi, ba tare da wani tsoro ko inda-inda ba, da cewa: *"Duk al'ummar da mai rauni a cikinta ba ya karɓar haƙƙinsa ba tare da wahala ba, ba za ta ɗaukaka ba." (Ibn Majah: 2426).*

## Kyautatawa Da Karamcinsa:

- Wata rana wani mutun ya zo ya roƙi Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam* wasu kuɗi, sai ya ce masa: "Tafi ka ci bashi, ni zan biya maka". Sai Sayyidina Umar, *radhiyallahu anhu*, ya ce: *"Ya Manzon Allah! Allah bai ɗora maka nauyin abin da ba ka da iko a kan sa ba."* Jin haka sai ran Annabi, sallallahu alaihi wa sallam, ya dugunzuma; bai ji daɗin abin da umar ya faɗa ba. Da mutumin ya ji abin da Umar, *radhiyallahu anhu*, ya faɗa sai ya ce ma Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam: "Ka ciyar da al'umma dukiyarka, kar ka yi tsammanin Allah Mamallakin al'arshi, zai tauye maka hannu."* Jin haka sai Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam,* ya yi murmushi, har fuskarsa ta nuna farin cikin sa. *(Al ahadisul mukhtarah :88).*

Littafan tarihi sun tabbatar da cewa, Manzon Musulunci bai tara ma kansa dukiya ba a tsawon rayuwarsa.



- Wata rana kuma an ɗauko dirhami dubu tamanin niƙi-niƙi, aka kawo ma Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*. Sai ya zuba su a kan shimfiɗarsa, ya shiga rabon su, har suka ƙare ƙaf; duk wanda ya roƙa sai ya ba shi, har ya kakkaɓe hannuwansa. *(Hakim :5423).*

## Haƙuri Da Juriyarsa:

- Ko da Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya fita daga birnin Ɗa'if, ɗan garin nan mai yawan duwatsu, mai nisan kilo mita 90 daga birnin Makkah, bayan da ya je yi musu wa'azi da kira zuwa ga Musulunci, amma suka yi tsananin cutar da shi, tare da mayar masa da mugun martani ta hanyoyi daban-daban. Ko da ya bar wannan gari, *sallallahu alaihi wa sallam*, yana cikin matsananciyar damuwa. A kan hanyar dawowarsa zuwa Makkah, garin da mutanensa suka kore shi daga ciki, bayan sun cutar da shi, su ma. Sai Allah ya aiko wani mala'ika zuwa gare shi, ya tambaye shi ko yana so a halakar da mutanen wannan garin. Amma, sai ya amsa da cewa: *"A'a, ina dai fatar Allah ya fitar da wanda zai bauta masa shi kaɗai, ba tare da yi masa kishiya ba, daga cikin tsatsonsu." (Bukhari: 3059).*

- Yanayi mafi tsananin muni ma a kan wannan shi ne, abin da ya faru tsakaninsa da mutanen Makka, waɗanda suka kore shi, bayan irin yadda suke gaya masa miyagun maganganu, da karkashe mabiyansa da takobi; babu wata dama da suka bari tsawon shekaru a ƙoƙarinsu na ganin baya gare shi da mabiyansa. Amma, lokacin da taimakon Allah ya zo masa, ya samu ɗaukakar nasara da cin garin Makkah, ya kama gaba ɗayansu a matsayin bayi. Sai ya miƙe tsaye a cikinsu yana cewa: "Me kuke zaton zan yi muku?" Sai suka amsa da cewa: "Alheri! Ya kai ɗan'uwa mai karamci, ɗan ɗan'uwa mai karamci.*" Sai ya ce musu: "Zan faɗa muku irin abin da ɗan'uwana Annabi Yusuf ɗan Ya'ƙubu ya faɗa ma 'yan'uwansa - yayin da yai musu afuwa, bayan sun cutar da shi sun jefa shi cikin rijiya. Amma, ya ce musu: "Ba ku da wani laifi a yau, Allah ya yafe muku. Shi ne mafi jinƙayin masu jinƙayi," (Yusuf: 92) Don haka, ku je an sake ku." (Baihaƙi :18275).*

> Manzon Musulunci ma, har kamanta abin da yake tsakaninsa da duniyar nan yakan yi, da matafiyi da ya ya da zango a cikin inuwar wata itaciya, sa'annan ya tashi ya wuce abinsa, ya bar ta…



## Gudun Duniyarsa:

- A kowane lokaci Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam* yana ƙoƙarin aiwatar da umarnin Ubangijin sa, inda yake cewa : *"Kuma kada ka miƙar da idanunka zuwa ga abin da muka jiyar da su daɗi, nau'i-nau'i, daga gare su, kamar huren rayuwar duniya yake, domin mu fitine su a cikinsa, alhali kuwa arzikin Ubangijinka shi ne mafi alheri, mafi kuma wanzuwa." (Dáha : 131).*

- Wata rana kuma amininsa Umar, *radhiyallahu anhu*, ya kai masa ziyara, sai ya tarar da shi a kishingiɗe a kan tabarma, har ta kwanta masa kuiɓi. Sai Umar ya ce: "Na waiga ko ina a cikin ɗakin nan ban ga wani abu wanda yake na jin daɗi ba. Sai na ce masa: Ka roƙi Allah mana ya yalwata ma al'ummarka, domin an yalwata ma Farisa da Rum; an ba su duniya tare da cewa ba su bauta ma Allah. Sai ya amsa masa da cewa: *"Kana kokwanto ne ya ɗan Khaddab?! Su mutane ne da aka gaggauta musu jin daɗinsu a rayuwar Duniya." (Bukhari : 2336).*

- Da yawa kuma, *sallallahu alaihi wa sallam*, yakan ce: *"Me ya haɗa ni da duniya?! Ni fa a duniyar nan kamar matafiyi ne, da ya ɗan ya da zango ya huta a ƙarƙashin bishiya, sa'annan ya tashi ya cigaba da tafiya abinsa." (Turmizi : 2377).*

- An saba a kwashe wata ɗaya ko biyu ko ma uku, ba a hura wuta a gidan Manzon, *sallallahu alaihi wa sallam* ba, balle a dafa abinci. Sai dai su riƙa cin dabino da ruwa kaɗai. *(Bukhari: 2428)*. Har wuni sukutum yakan kwashe, ba tare da ya saka wani abu a cikin bakinsa ba, *sallallahu alaihi wa sallam*, ko da kuwa busasshen dabino ne, balle maganar cikinsa ya cika. *(Muslim: 2977)*. Sa'annan bai taba jera kwana uku yana cika cikinsa ba, da wainar alkama har aka karɓi rayuwarsa. *(Muslim :2976).*




## Cika Alƙawarinsa :

- Cika alƙawari yana daga cikin manyan kyawawan halaye masu daraja, da suke ƙara ma mai yinsa ƙima a zukatan mutane, musamman idan ya zo ta sigar yaba kyauta tukuici. Wannan shi ne abin da Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam* ya saba yi; mayar da hannun baiwa da abin da ya fi wanda aka yi masa, ko da kuwa babu dalilin yin haka. To, ya kake ganin idan akwai dalilin?
- Lokacin da Hercules, Sarkin Kiristoci ya tambayi kafiran Ƙuraishawa game da siffofin Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, cewa ya yi: *Ko kuna ganin abin da yake yi yaudara ne? Sai suka ce: A'a. Sai ya ce musu: Haka nan Manzanni suke; ba su yaudara." (Bukhari :7).*
- Misalin wannan shi ne irin yadda ya kai matuƙa a cikin riƙe amanar matarsa ta farko, Khadijatu, saboda kariyar mutunci da matsayinta, a cikin siga ta bayyanawa da yarda da irin gudunmawar da ta ba shi a rayuwar addini, inda ya cigaba da yi ma abokai da makusantanta abin arziki.
- A'ishah, radhiyallahu anha, matar Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, tana ba mu labarin irin yadda ya damu da matarsa ta farko, Khadijah, *radhiyallahu anha*, wadda ta kwanta dama a cikin kwanukan da aka aiko shi Manzo. A'ishah ma ba ta san ta ba. A'ishah ta ce: "Annabi ya zamo yana yawan ambaton ta, yana yanka akuya ya daddatsa ta gaɓa-gaɓa, sa'annan ya aika wa ƙawayen Khadijah. Wata rana na ce: Kamar dai babu wata mace a duniya sai Khadijah? Sai ya ce: "Ita ce mai kaza da kaza da kaza…" *Ya ambaci wasu daga cikin managartan halayenta." (Bukhari: 3607).*
- Wata rana wata tawaga ta zo daga wajen Najashi, Sarkin Habasha, farkon wanda ya ba wa Musulmi kariya a farkon Musulunci, ta zo wurin Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*. Sai Annabi *sallallahu alaihi wa sallam*, ya tashi da kansa yana yi musu hidima da kansa. Sai Sahabbai suka ce masa: Mu za mu isar maka game da su. Sai ya ce: *"Haƙiƙa sun mutunta Sahabbaina, don haka ni nake so in saka musu da kaina." (Shi'abul iman :8704).*

Haƙiƙa Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam,* ya buga mana ƙayataccen misali game da kyawawan ɗabi'u a dukkanin fagagen rayuwa, don tabbatar da umarnin Allah, da koyi da Annabawa masu girma da suka gabace shi.

Masallacin kuma da Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya gina a Madina, ko birnin Madina mai haske, kamar yadda Musulmi suke kiranta, a matsayinta na birni mafi tsarki na biyu bayan Makka. Manzo Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya yi hijira zuwa can ne, ya kuma gina masallaci a wurin, aka kuma rufe shi a ciki. A yau kuma miliyoyan Musulmi suna ziyartar wannan wuri duk shekara.






# Wasu Daga Cikin Zantukan Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*

Musulmi sun ba da muhimmiyar kulawa wajen cirato zantukan Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ta hanyar saurarowa ko rubutowa. Manyan malamai masana makamar tantance Hadisai sun zabura don haddacewa da tantance lafuzansa. Saboda haka suka gabatar wa duniya ingantaccen tsari, don tabbatar da ingancin magana, da sanin abin da ya tabbata, da wanda bai tabbata ba, komai ƙanƙantar kalima kuwa, tare da lura da abin da aka jingina mata, alhali ba ya ciki. Ga misalan Hadisan da Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* ya faɗa:

## Ga misalan Hadisan da Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* ya faɗa:

- *“Dukkan ayyuka ba su karɓuwa sai da niyya. Kowane mutun za a saka masa gwargwadon niyyarsa.” (Bukhari :1).*
- *“Nagarta ita ce: kyawawan halaye, amma laifi shi ne duk abin da yake yi maka ƙaiƙayi a cikin zuciya, kana kuma ƙyamar mutane su san shi.” (Muslim :2553).*
- *“Ka ji tsoron Allah a duk inda kake. Ka bi bayan mummunan aiki da kyakkyawa, sai ya goge shi. Ka yi ma mutane kyakkyawar mu’amala.” (Turmuzi :1987).*
- *“Ka guji duniya, sai Allah ya so ka. Ka guji abin hannun mutane sai mutane su so ka.” (Ibn Majah :4102).*
- *“Misalina da misalin Annabawan da suka riga ni, kamar mutun ne ya gina gida ya ƙawata shi. Sai wajen bulo ɗaya ya hana kyawon nasa ya isa matuƙa. Sai mutane suka rinƙa kewayar gidan suna mamakin kyawon nasa, suna cewa: Ina ma a saka bulo ɗaya a nan, da kyawon nasa ya cika sosai! Ya ce: “Ni ne wannan bulo ɗin; Ni ne cikamakin Annabawa.” (Bukhari :3342).*
- *“Wanda ya yaye ma mumini wani baƙin ciki daga cikin baƙƙan cikin duniya, Allah zai yaye masa wani baƙin ciki daga cikin baƙƙan cikin ranar Ƙiyama. Wanda ya yalwata ma mai ƙunci, Allah zai yalwata masa a duniya da Lahira. Wanda ya rufa asirin Musulmi, Allah zai rufa asirinsa duniya da Lahira. Allah yana taimakon bawansa matuƙar bawan yana taimakon ɗan’uwansa. Wanda ya shiga hanyar neman ilmi, Allah zai sauwaƙe masa hanyar shiga Aljanna. Wanda aikinsa ya jinkirtar da shi ga barin shiga Aljannah, nasabarsa ba za ta gaggautar da shi ba.” (Muslim :2699).*



*“Duk wanda ba ya tausaya ma na ƙasa da mu, bai kuma san haƙƙin na sama da mu ba, ba ya tare damu.” (Turmizi: 1920).*





*“Ba za ku shiga Aljanna ba, sai kun yi imani. ba kuma za ku yi imani ba sai kun so junanku. Ko kuna so in gaya muku abin da idan kun yi shi, za ku so junanku? Ku watsa sallama a tsakaninku.” (Muslim:54)*

- *“Imanin ɗayanku ba ya cika sai ya so ma ɗan’uwansa abin da yake so ma kansa.” (Bukhari :13).*
- *“Musulmi shi ne wanda Musulmi suka kuɓuta daga harshensa da hannunsa. Mai hijira shi ne wanda ya ƙaurace ma abin da Allah ya hana.” (Bukhari :10).*
- *“Ku saurara! Duk wanda ya zalunci wanda ba Musulmi ba, ko ya ɗora masa abin da ya fi ƙarfinsa, ko ya karɓi wani abu daga hannunsa ba da daɗin rai ba. to, ni zan zama maga’isarsa ranar Ƙiyama.” (Abudawuda:3052)*
- *“Masu tausayi, Allah mai tausayi, zai tausaya musu. Ku tausaya ma waɗanda suke ƙasa, (Allah) wanda yake sama sai ya tausaya muku.” (Abu dawud :4941).*
- *“Wanda ya yi mana algussu ba ya tare da mu.” (Turmizi :1315).*
- *“Misalin muminai wajen ƙaunar junansu, da jinƙayin junansu, da tausaya ma junansu, kamar gangar jiki ce; idan gaba ɗaya ta yi ciwo, sai sauran jikin ya ɗume da zazzaɓi da rashin bacci” (Muslim: 2586).*
- *“Dukanku makiyaya ne, za a kuma tambayi kowane makiyayi. Shugaba makiyayi ne, za a kuma tambaye shi. Namiji makiyayi ne a cikin gidansa, za a kuma tambaye shi. Haka nan Mace makiyayiya ce a cikin gidan mijinta, za a kuma tambaye ta. Ku saurara! Dukanku makiyaya ne, kuma dukanku za a tambaye ku.” (Bukhari:4892)*
- *“Mafi cikarku imani, shi ne wanda ya fi ku kyawon hali. Mafiya alherinku kuma, su ne waɗanda suka fi ku alheri ga matansu.” (Turmizi :1162).*

- *"Mafi alherinku shi ne wanda ya fi alheri ga iyalinsa. Ni kuwa ni ne mafiyinku alheri ga iyalina." (Tirmizi :3895).*
- *"Lalle Allah yana son sassauci a cikin dukan lamari." (Bukhari:5678). Ya kuma ce: "Wanda aka haramta ma sassauci, an haramta masa dukan alheri." (Muslim: 2592).*
- *"Alamomin munafuki uku ne : Idan ya yi zance zai yi ƙarya. Idan ya yi alƙawari zai saɓa. Idan aka amince masa zai yi ha'inci." (Bukhari:33).*
- *"Yana daga kyawon Musuluncin mutun ya bar abin da bai shafe shi ba." (Turmizi:2317).*
- *"Wani lokaci wani mutum yana cikin tafiya, ƙishirwa ta tsananta gare shi. Sai ya samu wata rijiya, ya shiga ya sha ruwa, sa'annan ya fito. Sai ga wani kare ya zo yana lallagi, yana cin ƙasa saboda ƙishirwa. Sai mutumin nan ya ce: Lalle wannan karen yana jin matukar ƙishirwa kamar yadda na ji. Sai ya koma cikin rijiyar nan ya ciko takalminsa da ruwa, ya shayar da karen. Sai Allah ya gode masa, kuma ya yi masa gafara. Sai Sahabbai suka ce: ya Manzon Allah, har ta hanyar dabbobi muna da lada? Sai ya ce: Kuna da lada game da duk wani ma'abucin ɗanyar hanta." (2466).*





## Yaya Alƙur'ani Ya Siffanta Manzon Allah Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*?

Alƙur'ani ya bayyana mana wani ɓangare mai ƙayatarwa game da rayuwar Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, da mu'amalarsa da waɗanda suka kewaye shi. A lokaci ɗaya kuma ɗabi'u da halayensa, suna matuƙar bayyana ga duk mai karatun sa:

- Shi rahama ne ga dukkan halittu *(Anbiya: 107)*, ba wai ga Musulmi kawai ba.
- Yana da ɗabi'u masu girma. *(Kalam: 5).*
- Yana matuƙar kwaɗayi a kan shiriyar mutane, yana kuma jin tsananin damuwa game da ɓacewarsu. Sau da yawa magana ƙaƙƙarfa tana nusarwa cewa babban aikinsa shi ne kira da isar da saƙo. Allah kuma shi yake da ikon datarwa zuwa ga shiriya. *(Hud :12, An'am :107, Kahaf :127).*
- Yana nemar ma mutane uzuri, yana kuma kau da kai daga kura- kuran su. *(Taubah :43).*
- Yana roƙon Allah ya yi gafara ga makiyansa har sai da aka hane shi. *(Taubah :80).*
- Abin da duk yake takura muminai, yana takura shi. Shi kuma mai tausasawa ne, mai jinƙayi a gare su. *(Taubah : 128).*
- Wani lokaci yana cutuwa saboda jimawar da mutane suke yi a cikin gidansa, sai kunya ta hana shi ya yi musu magana. *(Ahzab: 53).*
- Mai sauƙin hali ne, mai rangwame, mai taushin zuciya. Yana cuɗanya da abokansa da tausasawa, yana kuma neman shawara da karɓar ra'ayinsu ko da a mafi tsananin yanayi ne, ko mafi hatsarinsa. *(Ali-imran: 159).*



# Alƙur'ani **Mai Girma Shi Ne Dauwamammiyar Mu'ujizar Musulunci**

Wane

Wane littafi ne wannan, Alƙur'ani, wanda aka fi yin cinikinsa ko rabar da shi a duniya? Littafin da masu imani da shi yawansu ya haura biliyan ɗaya da rabi?

## Alƙur'ani shi ne littafin Musulmi mai tsarki wanda suka yarda cewa, shi:


- Zancen Allah ne, wanda ya saukar ga Manzonsa Annabi Muhammadu *sallallahu alaihi wa sallam*, don shiriya da haske ga mutane.
- Cikamakin Littattafai ne waɗanda suke saukakku daga sama.
- Abin kiyayewa ne daga jirkice-jirkice ko canje- canje.
- Abin yin ibada ne da shi, ta hanyar karanta shi, da hardace shi, kamar yadda Musulmi suke yin ibada ta aiki da yin Shari'a da shi.

Alƙur'ani ya fara sauka ne ta hanyar Mala'ika Jibril, *alaihis salam,* bayan Annabi *sallallahu alaihi wa sallam* ya cika shekaru 40 da haihuwa. Farkon ayar da ta fara sauka kuwa ita ce: *{Ka yi karatu da fara ambaton sunan Ubangijinka wanda ya yi halitta}*. Ya sauka ne daki-daki a cikin shekaru 23 gwargwadon buƙata, ko faruwar wani abu.

> Aya ta farko ta Alƙur'ani da ta sauka, ita ce: *{Ikra'a bismi Rabbikal-lazi khalaƙ.}* "Ka karanta da sunan Ubangijinka wanda ya yi halitta." Bayan haka kuma ya cigaba da sauka gwagwadon rayuwar Musulmi har tsawon shekaru ashirin da uku (23)

Alƙur'ani yana da surori 114, masu bambancin manufa da tsarin zubi, mai ƙololuwar daraja a gwaninta da fasahar magana, waɗanda aka saukar don shiryar da mutane da kiran su zuwa ga bauta ma Allah shi kaɗai.

### Wasu Daga Cikin Muhimman Fagagen Da Alƙur'ani ya yi Magana A Kansu:



1. Tabbatar da kaɗaituwar Allah, da warware shubuhohin masu yi masa Shirka.
2. Ƙissoshin Annabawa, da al'ummomin da suka gabata.
3. Kira zuwa ga lura da girman halittun sammai, da duba ga halittun da suke kewaye da mu, da ƙididdige gwargwadon ni'imomin Allah gare mu.
4. Bayanin shari'o'in addini da umarni da haninsa.
5. Bayanin siffofin muminai da ɗabi'unsu, da tsoratarwa game da siffofi munana.
6. Zancen ranar Lahira, da sakamakon masu aikin ƙwarai da masu yin maras kyau.
7. Tarbiyyantar da muminai ta hanyar alaƙanta su da abubuwan da suka faru game da Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam* da Sahabbansa.

**Ga 'Yan Misalai Game Da Wasu Darajoji Da Alƙur'ani Ya Keɓanta Da Su.**





## Ƙalubalanta A Harda:

Allah ya ambaci littafinsa na ƙarshen aikowa, da sunan Alƙur'ani (Abin karatu) don ya yi nuni da cewa karanta shi ake yi, tare da aiki, da kuma hardace shi a ƙiraza. Ya ambace shi da alkitáb (Littafi) a cikin ayoyi da dama, don ya yi nuni game da rubuta shi da kiyaye shi a takardu. Haƙiƙa Allah Maɗaukakin Sarki ya kiyaye Alƙur'ani ta hanyoyin nan guda biyu; karantawa da hardacewa. Idan wata aya ta sauka ga Manzo, sai nan take a rubuta ta a gabansa. Za a hardace ta yadda akaji ta daga bakinsa. Ba kuma za a karɓi shaidar mahardata ba komai yawansu, matuƙar ba ta dace da wanda yake a rubuce ba. Shi kuma wanda yake a rubucen, ba za a karɓe shi ba, matuƙar bai dace da wanda aka hardato daga bakin Manzon Allah ba.

Amma, sai ga shi Malaman Kirista sun yarda sun kuma tabbatar da cewa, tubƙa da warwara da ake samu a cikin Injila ba wani abu ne sabo, ko kuma na assha ba. Hakan ya faru ne sakamakon karkasuwar tushen da marubuta Injilar suke da shi, da saɓanin tarihin wallafar kowaccensu. Ga rashin samun wahayi kai tsaye da ya mamaye ta. Amma, duk da haka sun gamsu da ita, da cewa duk abin da yake cikinta shiriya ne ga mutane.

Sai dai abin da yake tabbas, wanda ba zai yiwu ga dukkan manazarci mai adalci ya yi musunsa ba, shi ne cewa : Lalle Alƙur'ani shi ne littafi ƙwaya ɗaya kacal a duniya, wanda ya tsira daga tubka da warwara, ko cin karo da juna; domin lafazinsa da ma'anarsa duk zancen Allah ne. Hardace shi kuma da rubuta shi ya samu ne ta bakin Annabi mai girma, Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ta hanyar yi masa wahayi. Shi kuma ba ya ƙari ko ragi a cikinsa. Musulmi kuma, tattare da saɓanin mazhabobi da fahimtarsu, sai ga shi ko kalima ɗaya ta Alƙur'ani ba su yi saɓani a kan ta ba.

Tarihi kuma ya tabbatar da cewa, hanyar da aka riwaito Alƙur'ani da ita, tsawon zamuna, ta samu kyakkyawar kulawa. An shimfiɗa mata nagartattun hanyoyi kuma tsaurara, na harda, da tacewa, da rairayewa idan za a rubuta shi. Hakanan hanyoyin saka masa ɗigagga, da karantawa da hardace shi a cikin ƙiraza, da na zana haruffansa a kan takardu; ba yadda za a yi harafi ko wasali ɗaya ya faɗi, daga cikinsa ko a ƙara wani. Domin tabbatar da haka a yau, kowa na iya sayen kwafin Alƙur'ani, a ƙuryar ƙasar Chana, ko tsakiyar Afrika, ya kuma kwatanta shi, da wanda aka rubuta shekara dubu da suka wuce, da suke taskace a manyan gidajen tarihin duniya, domin ya ga abin mamaki da ban tsoro. Zai taras da cewa, salon zana ɗigagga, da kalmomi, da ƙa'idojin rubutu, su ɗin dai ne na dindindin, ba ragi ba ƙari bale canji, tattare kuwa da saɓanin zamuna, da bambancin harasa. Duk kuwa daga bakin wanda za ka ji Alƙur'ani; ƙaramin yaro ne ko babban malami, a hardace, a ƙasar Indonisiya, za a ji shi daidai da Malami Musulmi, da yake karantar da shi a Masallacin Ka'aba shekaru dubu da suka wuce. Daman dai Allah ya faɗi haka a cikin Alƙur'ani in da ya ce: *Kuma da ya kasance daga wurin wanin Allah, da sun samu saɓani mai yawa a cikinsa." (Nisa'ai: 82)*. Wannan kuwa ba abin mamaki ne ba, tunda Allah Maɗaukakin Sarki da kansa, ya ɗora ma kansa nauyin kulawa da kiyaye alfarmarsa, ya ce: *"Ko shakka babu, mu muka saukar da Alƙur'ani. Kuma mu, a gare shi, masu kiyayewa ne."*

## Gagarabadau ta Fuskar Bayani da Janhankali:

Duk mai karanta Alƙur'ani tare da cikakken mayar da hankali, zai fahimci cewa, Alƙur'ani yana mu'amala da mai karatunsa ne kai tsaye, a matsayinsa na ɗan Adam, tilo, ba tare da ya yanke zaren tattaunawa da shi, da kuma ƙalubalantar sa ba. To, abu mafi ban mamaki ma fiye da haka, duk bai fi irin yadda yake zarce tunanin mutum ɗin ba, har yake yi masa jagora a zuci. Sai kawai ya ji kamar an sauko masa wahayin aya ta gaba, tun bai kai ga karanta ta ba!.

Sanannen abu ne cewa, gwanin zane, na iya zana ido, da bayyana irin kallon da yake fitowa daga gare shi, kai tsaye. To, amma, ya za a yi Littafi, abin da ba mutum ba, ya iya tsinkayo tunanin da tambayoyin da suke cikin ƙwaƙwalwar mai karatunsa, ya kuma ba shi amsa, tun bai iso ba. Wani lokaci ma, shi ne da kansa, Littafin, yake hurawa da rura wutar tunani da tambayoyin, tattare da bambance-bambancen masu karanta shi, na ilmi da wayewa, da kuma tsarin rayuwarsu!

Lalle Alƙur'ani ya mallaki wannan irin salo, mai ƙayatarwa game da yin filla- filla da tunanin mutum, da fayyace wani abu nasa na ɓoye, da bayyana rauninsa, ta hanyar da a farkon al'amari, mai karatun zai ji kamar ana cin dugadugansa. Ba kuwa komai ba ne, illa wani salo na farkar da rai da yake yi ta hanyar jefa tambaya ga hankali da zuciya a haɗe; tambayoyi irin waɗanda da yawa, rai ke jinkirtawa, koma yana gudun jin amsarsu.

Yayin duk da ɗaya daga cikinmu, yake karatun Alƙur'ani, yana bibiyar ƙissoshi da sifofin wasu jama'a, da rayuwa da tunani irin nasu, da yanayin rayuka, da tsinkayensu, da yadda wasu suka halaka, wasu kuma suka tsira. To, nan da nan za ka ga ya tsaya yana batun zuci, tare da ɗora kansa a kan sikeli. Duk wannan kuma yana faruwa ne, a daidai lokacin da yake karanta ayoyin, da misalan cikinsa. A hankali sai zuciyarsa ta tasirantu, kaɗan-kaɗan ba tare da ya farga ba. Har sai a wayi gari Alƙur'ani ya zama madubi gare shi; ya rinƙa bayyana masa haƙiƙanin ko waye shi, ta hanyar bayyana masa aibinsa, da kasawarsa, da abin da zai iya, da damar da yake da ita. A haka sai ran mai karatun ya nutsa cikin tunanin, wanda a ƙarshe zai tabbatar da cewa, lalle: Babu Sarki Sai Allah.

Sai ka taras da shi, a duk lokacin da ya samu kansa cikin halin yanke ƙauna ga cimma wani abu, sai ya tuna ayar da take cewa: *{Ka ce: Ya ku bayina! waɗanda suka mike ƙafa a cikin saɓon Allah, kar ku yanke ƙauna daga rahamar Allah. Lalle Allah yana gafarta zunubai gaba ɗaya. Lalle kuma shi, mai gafara ne, mai jinkayi}* (Zumar :53).

A lokacin kuma da yake jin ƙaiƙayi da gumzar rikici mai tsauri tsakanin 'ya'yan halittarsa na azaliyya, can a cikin ransa, yana neman wanda zai fake bayansa, sai kawai ya tuna ayar da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: *"Kuma idan bayina suka tambaye ka game da ni. To, lalle ni Makusanci ne; ina jin kiran mai kira idan ya kira ni. Saboda haka sai su karɓa kirana, su yi imani da ni, tsammanin su, su shiriya."*



A lokacin kuma da ya ji cewa, rayuwarsa ta fara ɗaukar sabon salo; an wayi gari ba ya iya ɗaukar ɗawainiyar da take tattare da ita. To, sai ya tuna inda zai samu cikakken magani da waraka, can a cikin faɗar Allah, subhanahu wa ta'alah, a cikin Alƙur'ani: *"Allah ba ya kallafa ma rai face iya ikonsa. Yana da ladar abin da ya tsirfata, kuma a kansa akwai zunubin abin da ya yi ta aikatawa. Ya Ubangijinmu! Kada ka kama mu, idan mun yi mantuwa, ko kuma mun yi kuskure. Ya Ubangijinmu! Kada kuma ka aza nauyi a kanmu, kamar yadda ka aza shi a kan waɗanda suke a gabaninmu. Ya Ubangijinmu! Kada ka sanya mu ɗaukar abin da babu iko gare mu da shi. Ka kuma yafe daga gare mu, ka kuma gafarta mana, ka kuma yi jinkayi gare mu. Kai ne Majiɓincinmu, saboda haka ka taimake mu a kan mutanen nan kafirai."* (Baƙara:286)

Haƙiƙa Will Durant, babban masanin tarihin wayewa da ilimi a duniya, ya tabbatar da gagarumin tasiri da gudunmawar Alƙur'ani, da matsayinsa a wannan fage, wanda ya zama wajibi a kan duk mai adalci, ya tabbatar (The Story of Cibilisation 13\68-69). Ga abin da yake cewa:

"Haƙiƙa, da yawa daga cikin masu ilmi da binciken ci gaban duniya, a kowane zamani da ya shuɗe, da ma wannan zamanin da muke ciki; sun yi imani da Alƙur'ani, kamar yadda mutane masu yawan da ba za su ƙirguwa, suka yi imani da shi, tattare da bambancin hankali da tunaninsu. Ba kuma wani abu ne ya sa haka ba, sai shi Alƙur'ani da ya zo da aƙidar gaskiya, bayyananniya, wadda kowa zai iya karɓa. Mafi sauƙin aƙidu, mafi ƙarancin wahalar ganewa, mafi nisanta daga dabaibayi, mafi yawan 'yanci daga maguzanci ko bautar wani. Haƙiƙa Musulunci ya sanar da mutane da su fuskanci wahalar rayuwa, su yi juriya ga tunkarar dabaibayinta, ba tare da raki ko ƙosawa ba. Musulunci ya yi cikakken bayani a kan addini, tiryan-tiryan a cikin siga irin wadda babu abin da zai hana Kirista ko Bayahude mai ingantacciyar aƙida ya karɓa, ya yi imani da shi. Dubi abin da Allah yake cewa: *{Juyar da fuskokinku ɓangaren gabas da yamma, ba shi ne nagarta ba kawai. Amma, nagarta ita ce aikin wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira da Mala'iku da Littafai da Annabawa; ya bayar da dukiya alhali yana so, ga makusanta da marayu da mabuƙata da matafiyi, da masu tambaya da bayi; ya tsayar da sallah ya bayar da Zakka. Da masu cika alƙawarinsu idan suka yi, da masu haƙuri a lokacin ƙunci da yalwa da lokacin yaki. Waɗannan su ne waɗanda suka gaskata. Waɗannan su ne masu taƙawa.}* ( Baƙara :177).

*Will Diorant yana cewa: "Tabbas, da yawa daga cikin mazajen ilimi da tunani, sun yi imani da Alƙur'ani, tattare da bambancin matsayin ilimi da kaifin hankalinsu, ba don komai ba, sai don irin yadda Littafin ya zo da wata aƙida ta gaskiya, kuma bayyananniya, wadda kowa ma ke iya karɓa a matsayinta na aƙida mafi sauki da ƙarancin rikitarwa…"*



# Daga Ina Alƙur'ani Ya Zo?

Wannan tambaya ce irin ta hankali, wadda kai tsaye takan bijiro ma ƙwaƙwalwa a duk lokacin da aka yi magana game da Littafin Musulmi mai tsarki, wato, Alƙur'ani, da Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, cewa: Wai me ya sa ya zama wajibi a kan mu karɓar riwayar Musulmi da ta zo a cikin Alƙur'ani, game da wani al'amari na rayuwa? Ashe bai kamata gare mu, yin wannan tambaya a kan wannan lamari ba?

Masana tarihi ba su yi saɓani ba game da cewa Alƙur'ani, ya zo ne ta harshen wani mutum Balarabe, wanda ba ya karatu ba ya rubutu, da aka haifa a Makkah a ƙarni na shida miladiyya. Sunansa kuma Muhammad ɗan Abdullahi. Wannan shaida ta tarihi ce, wadda ta zo ta hanyoyi masu tarin yawan da wata shaida ba za ta iya rusa su ba. Wannan, kamar yadda muke karantawa a cikin Littafin ɓaro-ɓaro cewa, ba aikin wanda ya zo da shi ba ne; zance dai ne shi, na Mahalicci mai girma, wanda aka yi masa wahayinsa daga wajen Allah. Aikin Annabi Muhammadu *sallallahu alaihi wa sallam*, game da shi, shi ne isarwa kawai, da bayaninsa ga mutane ba tare da ƙari a cikinsa ko ragi ba.

Ko zai yiwu a ce Manzon Musulunci Annabi Muhammadu, shi ne ya ƙirƙira Alƙur'ani a karan kansa, ko ya koyi abin da yake a cikinsa, sa'annan ya sauya masa salo daga baya, ya gabatar da shi ga mutane?

> Ai, inda Manzon Musulunci ya so yaudarar mutane tare da yi musu mulkin mallaka, ta hanyar jingina zantukansa ga Allah, da sai ya gaya musu cewa, duk abin da ya fito daga bakinsa, daga wurin Allah yake. Me ya sa bai yi haka ba, *sallallahu alaihi wa sallam*?

Daga cikin abubuwan da za su sa a yi tambaya, shi ne, a ce, ai inda Manzon Allah ya so yaudarar mutane ne, da sai ya mamaye su da ƙarfin tsiya, ya kuma ce Allah ne ya yi umarni da haka. Amma sai ga shi, zantukan ma da suke fitowa daga bakinsa, bai ce dukansu daga wurin Allah suke ba, me ya sa?!

To, a hankalce, idan aka yi la'akari da haka, ai ba zai yiwu a ce shi ne ya wallafa, ko ya ƙirƙiri wannan littafi, da nufin jingina shi ga Allah don zartar da manufarsa, da ɗaukaka matsayinsa, da darajarsa ba. Alhali kuma muna gani ƙarara a wurare masu yawa a cikin wannan Littafi, inda aka zarge shi a matsayinsa na mai isar da saƙon, zargi irin na kai tsaye, da gabatar da nusarwa, da gyara game da kura-kuransa?

Haƙiƙa Alƙur'ani, kamar yadda duk wani mai karanta shi ya sani, bai ware wani keɓantaccen wuri da zai saukar da gudumar zarginsa ba. Annabi Muhammadu da kansa Alƙur'ani ya yi masa zargi, ya kuma gabatar masa da nasiha, a kan lamarin rayuwar iyalinsa, kamar yadda ya tabbatar da zaman wasu hukunce-hukuncensa kuskure ne, da suka haɗa har da wasu hanyoyinsa na kiran mutane zuwa ga addini!

Waɗannan tambayoyi ne da suka dace, da suke yin tsalle zuwa ga ƙwaƙwalwar mutum, kai tsaye, matuƙar wanda hakan ta faru gare shi, bai zamo mai karanta Alƙur'ani da nazarinsa ba, ko masanin tarihin rayuwar Annabi Muhammadu da ƙissoshinsa.

Abin da dai muka sani, nazarce-nazarcen tarihi kuma suka tabbatar shi ne: Mafi yawan Malaman adabi, da masu nazari, suna lelleka fasahohin wasu al'umomi waɗanda ba su ba, sa'annan su aro wani abu, ƙarshe su jingina shi ga kawunansu. Amma, don me wani zai jingina ma waninsa tunanin ƙashin kansa?

Daga cikin irin wannan zargi da aka yi masa, shi ne lokacin da wani mutum makaho daga cikin Sahabbansa, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya zo wurinsa, alhali shi kuwa Manzon Allah, hankalinsa ya ɗauku ga waɗansu jigajigan Kuraishawa da yake ta ƙoƙarin ganin sun karɓi Musulunci, amma shi makahon nan bai san da haka ba. Sai kawai ya buɗa baki ya yi ta kira da cewa: Ya Muhammadu! Ina roƙon ka karantar da ni wani abu daga cikin abin da Allah ya sanar da kai. Ya kuma nace; yana yi yana maimaitawa. Sai Annabi ya yi fushi har fuskarsa ta nuna cewa, yana jin ina ma dai makahon nan zai saurara har ya ƙarƙare wannan aiki. Sai kawai ya fita batunsa, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya cigaba da abinda yake yi, bai saurari makahon nan ba. Nan take sai Alƙur'ani ya sauka, ya kuma saka wannan lamari a cikin kundin tarihi. Ya kuma bayar da cikakken hoton yadda wannan al'amari ya faru, da irin yadda Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya sauya wa makaho nan fuska ya bar shi ba tare da ya amsa masa ba. Alƙur'ani bai tsaya nan ba, sai da ya ci gaba da zargi tare da faɗakarwa a cikin siga irin ta kai tsaye, tare da jan kunnensa kana ya sake. Hakan kuwa ta zo ne a cikin Sura ɗaya sukutum a cikin Alƙur'ani, da aka raɗa wa suna *(Abasa:1-11)* sai Annabi ya zamo bayan faruwar haka duk lokacin da wannan makahon yazo sai yace: *"maraba da wanda Allah na ya zarge ni saboda shi"* sai ya shimfida masa mayafinsa. Daga nan kuma sai ya shimfiɗa masa mayafinsa, *sallallahu alaihi wa sallam*. ya zauna.

Alƙur'ani ya tabbatar mana da ƙissoshi da dama, waɗanda a cikinsu aka zargi Manzon Allah sallallahu alaihi wa salla, aka kuma nusar da shi, a kan waɗansu abubuwa da, da yawa daga cikinmu ba za mu so a gaya mana a bainar jama'a ba. Ma'ana, ba mai son a yayata kurakuransa a kasa shi a faifai, har ma tarihi ya kama ya riƙe, kamar irin haka, matuƙar yana son girma da ɗaukaka da matsayi ga kansa!

To, ga shi tarihi yana gaya mana, a wurare da yawa, yadda Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya rayu a wani yanayi mai ƙunci, da yake sauraron a saukar masa da wahayi don ya tabbatar da gaskiya da matsayinsa, ko kuɓutarsa da ta iyalinsa, amma wahayin ba zai sauka ba.

Wani misalin shi ne irin yadda mutanensa waɗanda suka nuna masa adawa, suka nemi taimakon wasu masu ilimi da saukakken Littafi daga cikin al'ummomin da suka shuɗe, don su taimake su a kan yaƙar Annabi Muhammad.

Sai suka ba su shawarar su tambaye shi a kan abubuwa uku. Idan ya amsa musu, to, shi Annabi ne. Idan bai amsa ba kuwa, to, ba Annabi ba ne. Sai suka bi wannan shawara suka tunkari Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam,* da tambayoyi. Sai shi kuma ya fuskanci wannan ƙalubale, ya gaya musu cewa, zai ba su amsa gobe, (zaton zai samu amsa daga wurin Mala'ikan Allah).

Ana cikin sauraren haka kuwa, sai wahayi ya yanke daga Annabi

Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam,* tsawon wasu kwanaki bai zo masa ba. Sai maƙiyansa suka riƙa zuwa suna yi masa izgili a kan rashin bayar da wannan amsa kamar yadda ya yi alƙawari. Annabi ya samu kansa a cikin tsananin damuwa saboda wannan lamari. Alƙur'ani kuma bai sauka gare shi ba sai bayan kwanaki goma sha biyar, a tare da wahayin kuma, sai da Alƙur'ani ya yi masa wani irin hannunka mai sanda, ya ce masa: Kar ka ce, kai tsaye, zan yi kaza gobe, sai ka ce, in Allah ya so. Wannan jinkiri na zuwan wahayi don ka ba su amsa, ya zama alheri, domin Allah ya ba ka makama. *(Kahf :24)*.

## Tuhumce-tuhumcen Yau Da Gobe:

Yana daga cikin abubuwa masu ban mamaki, a ce ƙissar rayuwar Annabi Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, da tarihinsa zai yiwu a kalle su ta waɗansu nahiyoyi, a matsayin wasu manyan dalilai, da suke tabbatar da zamansu gaskiya, da suka haɗa da cewa:

Ya za a ce mutumin da ba ya rubutu ba ya karatu, yake kuma rayuwa a cikin waɗansu mutane da su ma, ba su rubutu ba su kuma karatu, yana kuma tarayya da su a cikin duk wani fannin rayuwa, wanda ba na fasiƙanci ba. Wanda kuma lalurar neman abin da zai ci shi da iyalinsa, ta ishe shi, inda ya fara daga aikin kiwon dabbobi, sa'annan ƙwadago da kasuwanci. Wanda kuma bai taɓa zaunawa karatu gaban wani malami ba. Sai kuma da ya kwashe shekaru arba'in cif, a cikin wannan hali. Sai kuma kwatsam ranar nan, ya ɓullo musu da wata sabuwar magana kuma baƙuwa, wadda ba su taɓa sani a wajen iyaye da kakanninsu ba. Sai ga shi yana ba su labarin mutanen farko, da tarihin farkon halitta, da bayanin rayuwar Annabawan da suka gabata daki- daki, da bayanin shari'o'i da hukunce-hukuncen gaba ɗayan ɓangaroran rayuwa, dalla-dalla.

Haƙiƙa wannan lamari ya tayar da hankalin maƙiya daga cikin mutanen Annabi Muhammadu, ba zato ba tsammani. Saboda haka ma, sai suka rasa irin kalimar da za su sifanta wannan lamari da ya zo masu da shi, da ita. Nan sai suka shiga tunanin wane irin ƙazafi ne za su yi masa, don hana mutane su saurare shi?

Suka kalli Alƙur'ani, suka tabbata cewa, abu ne mai matuƙar wahala, a iya gamsar da mutane cewa, Annabi Muhammadu ne ya ƙirƙire shi. Duk wanda ya karanta Alƙur'ani ba zai yarda da haka ba. Ba kuma zai yiwu a koyi wannan Littafi daga wajen wani wanda ba shi ba, *sallallahu alaihi wa sallam*, domin a cikinmu yake rayuwa; mun san sa ciki da waje. Saboda haka, sai suka shiga tuhumarsa da abubuwa masu takin saƙa da juna. Yau su ce, ya naƙalto Littafin ne daga waɗanda suka gabace shi. Gobe kuma su ce, shi ne dai ya rubuta shi da kansa. Wata ranar kuma su ce, yana ba su labarin mafarkan da yake yi ne a cikin barci. Idan kuma suka kasa tabbatar da gaskiyar haka, sai su ce, mai sihiri ne shi, ko mawaki, ko ma mahaukaci! Kai ka ji.

Irin wannan lamari kuwa, na 'yan ƙazafe-ƙazafe ƙissa ce, da ba ga Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* farau ba. Annabi Musa, *alaihissalamu,* ba an tuhumce shi da sihiri ba? Annabi Isa, *alaihissalamu* kuma aka jefe shi da hauka?!

Irin haka fa ya yi ta faruwa ga kusan gaba ɗayan Annabawan da suka gabaci waɗannan, *alaihimussalamu*. Duk lokacin da manyan suka rasa abin da za su tuhume su da shi, sai su yi da'awar cewa matsafa ne, ko mahaukata. Dama kuwa haka maƙaryaci yake. Idan ya san zai ji kunya, ko hujjarsa ta ƙare, sai ya riƙa 'yan kame-kame, yana laluben kowace hanya, komai ƙanƙantar ta, don ya samu madogara, alhali kuwa babu nasara a tare da shi!

## Me Zai Hana Mu Ɗauke Shi A Matsayin Gwarzo?:

Duk mutane sun yarda cewa Allah ya yi wasu tanade-tanade irin na ƙarfi da ikon ƙirƙira a cikin hankalin ɗan Adam, wanda ba za a iya kimantawa da iyakancewa ba. Amma, kana ganin ko a tsari irin na ɗabi'ar rayuwa, bai kamata a ce, wannan irin baiwa ta hankali, tana da iyakoki a fagen waɗannan ƙirƙira ba. Shi yasa kake ganin, tattare a hankalce, an yarda da samuwar Mahalicci ɗaya, mai cikakken iko. Sa'annan kuma a ƙarƙashin inuwar adalcin wannan Ubangiji, ya hukunta cewa akwai wata rayuwa da za a yi gobe Ƙiyama, wadda a cikinta kowa zai karɓi gwargwadon sakamakonsa na alheri ko sharri. Amma, duk da haka, kana ganin hankali na iya tabbatar da haƙiƙanin yadda rayuwar Lahiran nan za ta kasance, tun da ba shi da wasu hujjoji a kan haka? Babu.



Duk wanda yake karatu da nazarin Alƙur'ani, zai ga irin yadda yake cikakken bayani a kan iyakokin imani, daki-daki. Yana kuma bayar da cikakken hoton yadda aka fara halitta, da yadda za ta ƙare. Sa'annan yana sifanta yadda Aljanna da ni'imominta suke, da Wuta da sigogi da yanaye-yanayen azabobinta, da adadin ƙofofinta, da adadin Mala'ikun da aka damƙa ma alhakin kula da ita. Yana kuma tabbatarwa tare da bayanan manya da ƙananan lamurran duniya, da mutum. To, a ganinka a kan wane ma'auni na ilimi ne aka ɗora harsashen gaba ɗayan wannan masaniya?

Ko shakka babu, kai ka san ba tsabar wayo, da jaruntaka ne ya samar da wannan ba. Ko dai ka ce ƙarya ce, kuma ta banza, da yaye-yayen tunani. Ko kuma ka ce wata ƙasaitacciyar gaskiya ce, da ba a iya samu sai ta hanyar ilimi da karantarwa.


An kuma samu cewa, Ilimin zamani ya tabbatar da wasu daga cikin abubuwan da Alƙur'ani ya zo da su, ba tare da an samu wani abu na ilimi, da ya ci karo da su ba. Kamar yadda kuma a lokaci ɗaya aka tabbatar da cewa, sun dace da abubuwan gaibi da aka bayar da labarinsu a cikin saukakkin Littafai, da suka gabaci Alƙur'ani.

## Ko Dai Waɗancan Littaafan Ne Ya Canza Ma Tsari?

Mu ɗan tsaya kaɗan mu lura, don mu gani shin ko akwai wata kafa komai ƙanƙantarta da za a bi, a zartar da hukuncin cewa, ilmoman da suke ƙunshe a cikin waɗancan Littafai ne na Annabawan da suka gabata, Alƙur'ani ya tace ya canza musu fuska da fasali?

Idan muka wuce matsayin haƙiƙar da muke da ita cewa, Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ummiyi ne, da bai iya rubutu da karatu ba. Sa'annan kuma mafi yawan mutanensa, su ma ummiyai ne, ba su da masaniya da ilmummukan da ya zo da su. Ba shi kuma da wata alaƙa da ma'abuta waɗancan Littafai da suka gabata, wadda ta wuce haɗuwar da ya yi da Bahira a lokacin tafiyarsa yana ƙaramin yaro tare da Baffansa zuwa Sham, kuma Tarihi ya tabbatar cewa masu ilimin Lattafan a wancan zamanin suna ɓoye ilminsu ne don amfanin kansu kawai; kada matsayinsu ya kubce. Saboda haka ba abu ne da kowa ke iya samu ba.

Idan kuma ma muka rufe wannan babi, za mu tarar da cewa, tantagaryar gaskiyar da duk wani mai nazarin Alƙur'ani ya sani, ita ce, babu wani abu a cikin Alƙur'ani da yake kankankan da abin da yake cikin waɗancan Littafai da aka saukar daga sama a wannan lokacin. Ya zo ne da wani sabon salo da sabon tsari, don gyara wasu daga ilmomin da suke cikinsu, waɗanda wasu daga cikin Malamansu suka hautsina suka yamutsa, ya kuma kammala wasu ƙissoshi da ba su cika ba, sa'annan ya bayyane abin duk da suke ɓoyewa na ilimi. Ƙari a kan haka kuma, ya bayyana miyagun aƙidu da halaye, waɗanda wasu Malamai suka ɗanfara wa addinan Annabawa, *alaihimussalamu*, alhali ba su da alaƙa da su kowace iri. Alƙur'ani cike yake da misalai irin waɗannan. Kana ganin zai yiwu, tattare da waɗannan martabobi, a ce Alƙur'ani ya shawo ne daga ilmukan da suke cikin waɗancan Littafai na farko?!



## Tantagaryar Gaskiya a Tarihance:

LDuk wani mai bincike mai adalci ba zai rasa tsayawa ba, don yin nazarin shin wai Manzon Musulunci Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, ashe ba Balarabe ba ne?

Ashe kuma tarihi bai gaya mana cewa, Larabawa a wannan lokaci, ba su da wani adabi na rayuwa abin a zo a gani, face fasaha da balaga ba? Sa'annan kuma ba su da wata sana'a baya ga waƙa da adabi, waɗanda suke shirya taruka da majalisai da bukukuwa domin gudanarwa. Har ma ƙabila takan samu ɗaukaka ko ƙasƙanta darajar wata waƙa ɗaya da aka yi a kan ta?

A gefe ɗaya kuma littafan tarihi da na adabi sun ba mu labarin cewa, babu wani daga cikinsu, da zai yi waƙa ko rubutun zube, sai an ci duduniyarsa, an cika inda ya samu tawaya, an ƙara abin da ya kuɓuce masa, sai an yi masa raddi da irin zubin waƙar da ya yi amfani da shi. Lalle wannan shi ne dandamalin gasarsu, shi ne wajen bayyana ƙarfi da darajarsu.

Ta yaya kuma ɗaya daga cikin manyan maƙiyansu, wanda ba ya barin kafa komai ƙanƙatarta, ta cutarwa da yaƙa, da ɗanɗana masa azaba, shi da mabiyansa, tare da ƙoƙarin kashe masa kasuwa, har kuma shi a nasa ɓangare, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ƙalubalance su a kan su zo da wani abu mai kama da Alƙur'ani, ko misalin wani abu daga cikinsa, sannan su kasa tunkarar sa da abin da ya nema ɗin a nan, a maimakon haka sai suka kama bakinsu, suka yi kamar ba su ji shi ba saboda kasawa da gazawa.

Ashe ba kamata ya yi Annabi Muhammad, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya yi fargaban motsa fushinsu da wannan ƙalubale da ya jefa musu ba, musamman na ƙwarewar da suke da ita ta Balaga da fasaha, don kada ƙarshe su ƙalubalance shi, ɗaiɗaiku da cikin jama'a, su kuma rinjaye shi. Ƙarshe su tabbatar wa mutane da zaman abin da ya zo da shi bakin banza. Amma bai yi ba, *sallallahu alaihi wa sallam*!

To mu ƙaddara ma, ya yanki wannan ƙaddara ne, saboda masaniyar da yake da ita a kan matsayin mutanen nasa. To, ya aka yi ya samu garantin ƙaddara ma al'ummomin bayansa irin wannan hukunci har ƙarshen duniya? Cewa su ma ba za su iya cin wannan jarrabawa ba, ta zuwa da wani abu mai kama da Alƙur'ani, ko yankinsa, ko da kuwa sun yi wa hakan taron dangi?!

Kai ka san wannan wata irin kasada ce, wadda babu mai faɗa ma ta, illa namijin da zuciyarsa take cike da yaƙini da tabbaci tare da yarda da abin da yake tallatawa. To, haka kuwa al'amarin ya kasance. Ƙuraishawa ko wani daga cikin zaƙaƙuran fasaha, babu wanda ya yi ƙarfin halin gwada cin wannan jarabawa ta ƙirƙira irin Alƙur'ani, ko wani yankinsa. Wannan wani tabbataccen abu ne da tarihi ya tabbatar a waɗancan kwanuka, da kuma waɗannan. Duk waɗanda ma suka yi yunƙurin gwadawa, sun kwashi kashinsu a hannu, ƙarshe suka zama abin dariya, da izgili, da wofintarwa a fagen adabi.

## Suratul Fatihah:

Ita ce sura mafi girman daraja a cikin Alƙur'ani. Shi ya sa aka ɗora ma Musulmi nauyin karantawa da maimaita ta ko da yaushe a cikin sallarsa. Ma'anarta kuma a taƙaice ita ce:

### *Ma'anar Suratul Fatiha*

| | |
|---|---|
| *{Bismillahir Rahmanir Rahim}* | *"Ina farawa da sunan Allah domin ladabi da girmamawa, a matsayinsa na wanda ya sifaita da rahama, wadda ta yalwaci dukan komai."* |
| *{Alhamdu Lilláhi Rabbil Álamín}* | *"Ina yabo ga Allah ta hanyar gaba ɗayan sifofi, da ayyuka, da ni'imominsa na zahiri da na baɗini, tare da so da ƙauna da girmamawa gare shi. Shi ne wanda ya halicci gaba ɗayan talikai, Mamallaki, mai sarrafawa, mai kuma ni'ima.* |
| *{Arrahmánir Rahím}* | *"Shi ne Sarkin da ya sifaita da duk wata sifa ta rahama, yadda take, da kuma inda take. Shi ne Ma'abucin rahama, wadda ta yalwaci dukan komai a faɗin wannan duniya. Shi ne kuma Ma'abuci keɓantacciyar rahamar da take saduwa da bayinsa muminai.* |
| *{Máliki Yaumid dín}* | *"Gudanar da komai a hannunsa yake a ranar hisabi da sakamako."* |
| *{Iyyaka na'abudu wa iyyáka nasta'ín}* | *"Kai kaɗai muke bauta ma; ba mu haɗa ka da wani a cikin kowane nau'i na bauta; ba mu bauta ma kowa sai kai ya Ubangijinmu! Gare ka, kai kaɗai muke neman taimako domin gaba ɗayan al'amari a hannunka yake; babu wani mahaluki da yake mallakar wani abu ko kwatankwacin ƙwayar zarra.* |
| *{Ihdinas siráɗal mustaƙím}* | *"Ya Ubangiji! Ka nuna mana, ka kuma shiryar da mu zuwa ga hanya madaidaiciya. Ka kuma tabbatar da mu a kan ta har ranar da za mu haɗu da kai."* |
| *{Siráɗallazína an'amta alaihim}* | *"Hnayar waɗanda ka yi ni'imar shiriya da daidaito a gare su, daga cikin Annabawa, da Salihai, waɗanda suka gane tafarkin gaskiya, suka kuma bi shi."* |
| *{Gairil magdhúbi alaihim waladh dhállín}* | *"Ka nisantar, ka kuma kuɓutar da mu daga tafarkin waɗanda ka yi fushi da su, saboda sun san gaskiya sun kuma ƙi biyar ta. Ka kuma nisantar da mu daga tafarkin waɗanda suka ɓace ma tafarkin gaskiyar, saboda tsananin jahilci da kasawa a cikin neman ta."* |
| *{Ámin}* | *"Ya Allah ka karɓa."* |



## Kowa Yana Da 'Yancin Yanke Hukunci:

Bayan duk wannan kaiwa da komowa, ya rage ga kowannenmu ya yanke ma Alƙur'ani hukunci, ya san matsayinsa gare shi, gwargwadon abin da ya fahimta na ƙashin kansa, bayan ya yi masa karatu da nazari irin na ƙwaƙwaf, tare da kaiwa da komowa, bayan ya nemi nagartacciyar fassarar da ta dace da shi, idan shi ba Balarabe ne ba.

Da ma kuma Alƙur'ani ya riga ya tabbatar mana da cewa, hujja mafi girma da ke tabbatar mana da gaskiyar Annabcin Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ita ce ƙarshen abin da za mu fahimta da zukata da hankulanmu, bayan dogon karatu da nazarin ma'anonin Alƙur'ani, inda ya ce: *{Bai ishe su ba ne cewa mu mun saukar da Littafi gare ka, ana karanta musu. Lalle a cikin wannan akwai rahama da faɗakarwa ga mutane masu imani.} (Ankabut :51).*

Saboda haka ne ma ya kira gaba ɗayan mutane da babbar murya zuwa ga yawaita karatun Alƙur'ani da nazarin sa, da kuma kaiwa da komowa a cikin ma'anoninsa. Ya kuma bayyana cewa, babu wanda zai ƙi haka, sai wanda an riga an sanya makullai a zuciya da hankalinsa. *(Muhammad: 24).*





# Ibadoji Da Sirrin Ma’anoninsu A Musulunci

## Allah Yana Buƙatar Ibadunmu ne?

A tantagaryar gaskiya, Allah Maɗaukakin Sarki ba shi da buƙata da ibadoji da sauran ayyukanmu. Sa’annan kuma tsira da samun babban rabo a Musulunci, ba ayyukan ibada na zahiri, da sauran ibadojin dukiya ne suke samar da su ba. hakan tana samuwa ne sakamamkon irin yadda aka yi su da gaskiya, da cikakken imani da Allah, irin abin da ake iya fassarawa a fili da, tsabar tsarkin zuciya, da aiki don hidima ga jama’a, da ƙoƙarin ciyar da su gaba.

Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: *Kuma ban halicci aljanu da mutane ba, face don su bauta mani. Ba ni neman wani arziki daga wurinsu, ba ni kuma neman su ciyar da ni. Haƙiƙa, Allah shi ne mai azurtawa, ma'abuci tsananin ƙarfi." (Zariyat:56-58)*

Shi ya sa a lokacin da mutane suka shiga ruɗani a kan ko ina ne ingantacciyar alƙiblar Sallah, saboda a Musulunci dole ne a fuskanci Makka idan za a yi Sallah. Sai aka ba su amsa da cewa, tsantsar addini a Musulunci shi ne gaskyar imani, da yin aiki na ƙwarai, da manufar amfanar da ɗan Adam, ba wai kawai fuskantar gabas ko yamma ba. Alƙur'ani ya gaya musu cewa: *"Ba ɗa'a ba ne kaɗai, ku fuskantar da fuskokinku gabas ko yamma. Haƙiƙanin ɗa'a, tana tare da wanda ya yi imani da Allah, da ranar ƙarshe, da mala'iku, da littafai, da Annabawa, ya kuma bayar da dukiya a cikin daɗin ransa, ga makusanta, da marayu, da miskinai, da ɗan tafarki, da masu roko, da cikin 'yanta wuyaye, ya kuma tsayar da salla, ya bayar da Zakka, da masu cika alƙawarinsu idan sun yi, da masu haƙuri a lokacin tsanani da ƙunci, da lokacin yaƙi. Waɗancan su ne waɗanda suka gaskata, kuma waɗancan su ne masu taƙawa." (Baƙara:177).*

Haka kuma Alƙur'ani yana ƙara tabbatar mana da cewa, duk wanda ya yi iyakar ƙoƙarinsa a cikin ibada, da addini, to, amfanin nasa ne; shi zai tsira. Wanda kuma duk ya kafirce, to, shi kaɗai hasara za ta shafa. Allah Maɗaukakin Sarki ba ya neman komai a wurin mu, kamar yadda yake cewa: *"Duk wanda ya yi ƙoƙari, to, yana ƙoƙari ne kawai domin kansa. Haƙiƙa, Allah, tabbas, Wadatacce ne daga barin talikai". (Ankabut:6).*



"A lokacin wasu mutane suka samu ruɗani a kan ina ne ainihin ingantacciyar alkibla take idan za a yi salla; suka shiga neman fatawa. Karshe sai suka samu tabbaci cewa, kar su damu da wannan. Addinin gaskiya ya tsaya ne a kan ingantaccen imani, da mayar da hankali ga ayyukan ƙwarai, da amfanar da 'yan Adam; ba kawai mayar da gaba gabas ko yamma ba.



## Rukunan Musulunci :

Rukunan Musulunci su ne mafi girman ibadu, da aka yi umarni da su a Musulunci, ga su kamar haka:




Imani:

Imani shi ne bayar da gaskiya, da tabbatar da bauta ma Allah da zuciya ɗaya, da koyi da Manzo Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*. Hakan kuma tana tabbata ne ta hanyar shaida: Babu abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma Annabi Muhammadu Manzon Allah ne. (duba shafi na: 30)




Tsayar da Sallolin Farilla:

(duba shafi na: 98)




Bayar da Zakka:

Ga waɗanda suka cancanta.

(duba shafi na: 102 )




Azumin watan Ramadan:

(duba shafi na: 104)




Ziyartar Ɗakin Allah Mai Alfarma:

Ga masu iko ta mallakar kuɗi da lafiyar jiki. (duba shafi na: 106)

## Me Ya Kawo Takalifi Da Jarrabawa?

Har wayau akwai wata tambaya, da ba ta gushe tana bijirowa da kanta a kai a kai ba, tattare da sassaɓawar sigoginta. Sai ka ji ɗayansu yana cewa: Me zai sa Allah ya halitta mana baki da hakori da uwar hanji, don mu ci abinci, sa'annan ya ce, mu yi azumi?! Ta yaya zai halitta mana kyau da sha'awa, sa'annan ya ce: Mu rintse idanunmu kada mu yi kallo! Ta yiwu wani ya yi tsaurin kai ya ce: Don me zai ba mu ƙarfi, sa'annan ya hana mu ta'addanci a kan wasu da zaluntar su?

A tantagaryar gaskiya wannan al'amari ya fi komai zama warware a Musulunci. Tabbas! Allah ya ba mu waɗannan damammaki ne domin mu yi ikonmu da su. Ai doki da Allah ya ba ka, ya ba ka shi ne don ka hau shi kai, ba ya hau ka ba shi. To, kamar haka ne jiki da ƙarfin da ya ba mu, dawaki da aka halitta domin mu, domin mu hau mu yi sukuwa a kan su, ta hanyar tuƙawa da ja musu lizzami a daidai inda ya dace, da sa'adda suka dace, ba akasin haka ba.

Wannan shi yake tabbatar da cewa, matsayi da ikon mutum suna bayyana ne a lokacin da yake saka ma sha'awowinsa linzami, da saka ma zuciyarsa ragama, tare da karkata akalarsu zuwa ga abin da yake mai amfani. Da wannan ne kuma Allah ya bambanta tare da ɗaukaka matsayin mutum, ya buɗe masa ƙofar zaɓen abin da yake so ga kansa. Saboda haka ne kuma Allah ya halicce mu.

Tabbacin hakan kuwa shi ne abin da Alƙura'ani yake cewa: *"Lalle ne mu, mun halicci mutum daga ɗigon ruwa garwayayye, muna jarraba shi. Saboda haka muka sanya shi mai ji mai gani. Lalle mu, mun shiryar da shi ga hanyar ƙwarai, ko ya zama mai godiya, ko kuma ya zama mai kafirci." (Insan:2-3)*

Dukan kuma musibu da wahalhalun da suke samun mutum, ba wani abu ne ba sai zaɓin kanmu, kari a kan yanayinmu na tun asali na ruhi, da ɗabi'a, da imani, domin mu waiwaya mu tuna manufa da matsayinmu a wannan rayuwa, kamar yadda ya zo a cikin Alƙur'ani: *"Kuma da sannu za mu jarrabe ku da wani abu na tsoro, da yunwa, da tawayar dukiya, da rayuka, da 'ya'yan itace. Amma kuma ka yi bushara ga masu hakuri, waɗanda idan musiba ta same su, sukan ce: Lalle mu, daga Allah muka fito, kuma a wurin sa za mu koma." (Bakara:155-156).*

To, haka aka shirya mana rayuwar duniya, ta zama wani wuri da yake ba mu damar bunƙasa imani da ɗabi'unmu ko nakkasa su. Duk da yake Allah subhanahu wa ta'alah, ya ba mu cikakkiyar dama, mai yaɗo, ta shiriya da nagarta, amma, bai ce dole sai mun yi amfani da ita ba. A maimakon haka sai ya bar mana ƙofar a buɗe domin zaɓin ranmu. Ya kuma nusar da mu zuwa ga raya ƙasa, da amfanar da ɗan Adam, da ɗaukar darasi daga kurakurai da tuɓatuɓanmu; mu komo mu tuba gare shi duk lokacin da muka faɗa cikin kuskure da talalaɓiya (santsi). Ta tabbata cewa Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* ya ce: *"Ba don kuna zunubi ba, da Allah ya shafe ku, ya kawo waɗansu mutane da suke yin zunubi, su kuma nemi gafararsa, ya gafarta musu." (Muslim:2749).*





> Girma da ɗaukakar mutum a idon Musulunci shi ne, zama mai ƙarfin iko a kan son zuciyarsa, da saka ma rayuwa da ruhinsa dabaibayi tare da amfani da wannan iko a cikin abubuwa masu amfani…

# Sallah

Tana yiwuwa ka taɓa yin tambaya a ranka game da haƙiƙanin al'amarin Sallah, a lokacin da ka ga lamarin nan mai ban mamaki, kai tsaye ko ta kafafen sadarwa. Ka ga Musulmi ɗaya ko fiye, sun fuskanci wani keɓantaccen wuri, sun yi tsaye. Can kuma suka yi ruku'u, da sujada, kamar dai sun kakkaɓe hannayensu gaba ɗaya daga duniyar da suke cikinta.

## Mene ne Matsayin Sallah Ga Musulmi?

Sallah tana da matsayi mai girma da muhimmanci a Musulunci, saboda ita ce hanya ƙwara ɗaya kacal, ta samun kusanci ga Allah Maɗaukakin Sarki, da roƙonsa, da kuma ƙanƙan da kai a gare shi, kamar yadda Allah, ya gaya ma Annabinsa, *sallallahu alaihi wa sallam*, cewa: *"Ka yi sujada ka kuma nemi kusanci." (Alak:19)*. Saboda haka ne aka ɗora ta a matsayi na biyu; bayan kalimomi biyu na shiga Musulunci.

Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"An gina Musulunci a kan abubuwa biyar: Shaida babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Annabi Muhammadu kuma Manzon Allah ne, da tsayar da sallah…" (Bukhari :8)*.

Musulunci ya karantar da mu cewa, ana ba wa Musulmi ladar sallarsa, gwargwadon yadda ya tsarkake zuciyarsa a cikinta, ya tattara hankalinsa da tunaninsa wuri ɗaya, ya kuma ƙanƙan da kai ga Allah da gaskiya, a cikin siga ta neman lada da kusanci a gare shi, ta yadda zuciya za ta samu natsuwa da kwanciyar hankali. Saboda haka ne, babu abin da yake faranta ma Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, rayuwa kamar Sallah.

Daga wannan matashiya ce kuma, Alƙur'ani yake umarnin mu da tsayar da Sallah, ba yin ta kawai ba, saboda tsayar da Sallah a haƙiƙanin al'amari, yana nufin tattara hankalin gaba ɗayan gaɓoɓi, da hankula, da zuciya, da ruhi a cikin ta. Da zarar mun aikata haka kuwa, to, Sallah za ta zamar mana wani jagora zuwa ga aikata ayyukan alheri, da nisantar miyagun ayyuka da manyan laifuka. Saboda haka zikirin Allah, da mayar da al'amurra gare shi, suna daga cikin mafi girman aikin da mutum zai yi.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: *"Ka karanta abin da aka yi maka wahayi na Littafi, ka kuma tsayar da Sallah. Haƙiƙa Sallah tana hani daga alfasha da abin ƙi. Kuma lalle, ambaton Allah shi ne mafi girma. Allah ya san abin da kuke aikatawa." (Ankabut:45).*


Duk wanda kuma ya zaci cewa, Sallah, motsa jiki ce kawai, da ake gabatar da tsarki da wanka kafin sa, to, tabbas bai gane cewa, motsin da yake gani ana yi a cikin Sallah, ba wani abu ne ba, illa ayyuka da zantuka, da ke girmama Allah a cikin zukata, ta hanyarsu. Farkon kalimar da mai Sallah yake furtawa tare da ɗaga hannuwansa sama, ita ce: *'Allahu Akbar.'* Sa'annan ya yi cikakken ruku'u, mai cike da tsoron Allah, a cikin siga ta jin giman Allah ya ratsa rayuwarsa, da kuma yarda da amincewa da kasawarsa shi, yana mai cewa: 'Subhana Rabbiyal-Azim." Sa'annan ya faɗi ya yi sujada ga Allah domin neman kusanci da karɓar du'ainsa, ta hanyar ɗora goshi da tsinin hancinsa a kan ƙasa, yana mai cewa: *'Subhana Rabbiyal- A'alá,"* sa'annan ya kira Ubangijinsa ya kuma kai kuka gare shi. To, haka gaba ɗayan ayyukan Sallah, da zantukanta suke. Ba kawai motsa gaɓoɓi da motsa baki ne ba. Wasu 'yan daƙiƙoƙi ne masu daraja da tsada, da suke sada mumini da Ubagiji kuma Mahaliccinsa, wanda yake lamunce masa wanzuwa da cikakken arziki.

Haƙiƙa Allah ya farlanta ma Musulmi salloli biyar a dare da wuni, da yin su a kowane wuri hali ya samu, yake inganta. Sai tattare da haka ya kwaɗaitar da su yin ta a masallaci, don saduwa da ƙara danƙon zumunci a tsakanin Musulmi; junansu su taimaka ma juna a cikin al'amarin addini, kamar yadda suke taimakekeniya a sauran al'amurran duniya.

Haka nan kuma Musulunci ya kwaɗaitar matuƙa a kan ƙoƙarin yin nafiloli, wato, sallolin da ba farilla ba, duk lokacin da Musulmi ya samu dama da nishaɗi a kan haka.



> Sallar nan kuma, ta kasance abu, wanda ya fi komai daɗaɗa ma Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam,* rai.



Masallacin Makka shi ne Masallaci mafi girma da ɗaukaka a idon Musulmi, wanda a cikinsa ne ɗakin Ka’aba, wanda Annabi Ibrahimu, alaihissalam, ya gina yake. Gini ne kuma shi, ɗakin, mai kusurwa huɗu, wanda aka umarci Musulmi a cikin Alƙur’ani, da riƙa fuskantarsa daga kowace nahiya suke a cikin duniyar Musulunci, don yin salla, tare da imani da cewa, ba ta cutarwa ba ta kuma amfanarwa.

Musulmi kuma sukan yi waɗannan salloli ne suna fuskantar ɗakin Ka’aba, ginin nan mai kusurwa huɗu. Farkon wanda ya gina wannan ɗaki kuwa shi ne Annabin Allah Ibrahimu, alaihissalamu, wanda aka fi sani da kakan Annabawa, a garin Makka, yamma ga tsibirin Larabawa. Wuri, wanda gaba ɗayan Annabawa, babu wanda bai kai masa ziyara ba. Musulmi, sun san cewa ɗakin nan da duwatsu aka gina shi, ba ya cutarwa ko amfanar da kowa. Amma, tunda Allah ya yi umarni da fuskantar sa idan za a yi Sallah don samun haɗin kan Musulmi ga fuska ɗaya, suke yi.

## Kiran Sallah

Kira Sallah shi ne wata shela da ake yi don faɗakar da mutane game da shigowar lokacin Sallah. Sai mai kira ya kira su zuwa Masallaci.

Shi kuma wani nau’i ne na zikiri da ambaton Allah da girmama shi, da jan hankalin Musulmi don halartar Sallah. Ga kuma lafuzzansa kamar haka:

1. *Allahu Akbar, Allahu Akbar, (Allah mai girma, Allah mai girma). Allahu Akbar, Allahu Akbar, (Allah mai girma, Allah mai girma).*
2. *Ash’hadu an la’ilaha illallah, (ina shaida babu abin bauta da gaskiya sai Allah.) Ash’hadu an la’ilaha illallah, (ina shaida babu abin bauta da gaskiya sai Allah).*
3. *Ash’hadu anna Muhammadar rasulullah, (ina shaida Annabi Muhammadu Manzon Allah ne). Ash’hadu anna Muhammadar rasulullah, (ina shaida Annabi Muhammadu Manzon Allah ne).*
4. *Hayya alas salah, (ku taho zuwa ga Sallah). Hayya alas salah, (ku taho zuwa ga Sallah).*
5. *Hayya alal falah, (ku taho zuwa ga babban rabo). Hayya alal falah, (ku taho zuwa ga babban rabo).*
6. *Allahu akbar, Allahu akbar, (Allah mai girma, Allah mai girma).*
7. *La’ilaha illallah, (Babu abin bauta da gaskiya sai Allah).*

## Zakka


Kowa ya yi imani da cewa, babu makawa ga ɗaukar mataki domin magance matsananciyar wadata da matsanancin talauci, domin gwargwadon rata a tsakanin mawadata da matalauta, gwargwadon yaɗuwar ɓarna da alfasha da ta'addanci a tsakanin mutane. Saboda haka ne aka samu tsare-tsaren tattalin arziki, da na Falsafofin rayuwa, da na shari'o'i da dokoki, daban-daban a kan yadda za a magance wannan matsala. To, wane mataki ne Musulunci ya ɗauka a kan haka?

Allah ya farlanta ma Musulmi mawadata su fitar da 2.5% daga cikin dukiyarsu a kowace shekara; don a raba ma mabuƙatansu daga cikin talakawa da marasa abin hannu da sauransu. Ya saka Zakka ta zama rukuni na uku daga cikin rukunan Musulunci.

Ba alfarma ba ce mawadaci zai yi wa talaka don ya ba shi Zakka. Haƙƙi ne na talaka da za a fitar daga dukiyar mawadaci, a sadar da mabukacin nan da ita ba tare da an jira ya roƙa ba, balle ya zubar da mutuncinsa.

Wannan ɗan ƙanƙanin abin da za a ciyar na Zakka, shi ne kacal haƙƙin da aka wajabta ma Musulmi mawadaci. Amma, gagarumar ciyarwa, wannan kuma ƙofa a buɗe take don masu neman lada su yi gasa a ciki, don su samu tasirin baza dukiyarsu da suka yi, a rayuwarsu ta nan duniya ta hanyar lafiya, da ƙarin dukiya, ga kuma dacewa da kwanciyar hankali, sa'annan a Lahira su samu lada da ni'ima ninkin-bi-ninkin.

Tabbacin wannan kuma shi ne abin da ya zo a cikin Alƙur'ani, cewa: Waɗanda suke sadaukantar da dukiyarsu, saboda neman yardar Allah, to, kamar alkama ce, da aka shuka, ta fitar da zangarniyoyi. A jikin kowace zangarniya akan samu ƙwaya ɗari, sai suka ninka har sau ɗari bakwai. Bayan haka kuma Allah Maɗaukakin Sarki zai cigaba da ninka ta gwargwadon niyyar mutum, domin Allah mai yalwatawa ne, mai karimci, Masanin haƙiƙanin al'amurra.



“ Ita kuwa Zakka, ba wata alfarma ce mawadata ke yi ma matalauta ba. A'a, haƙƙi ce na talakawan, da Allah ya ce a karɓo daga cikin dukiyar mawadata, a sadar da ita da su, ba kuma tare da mawadatan sun jira an tambaye su ko sun tozarta mabuƙatan ba.

Allah ta'ala ya ce: *{Misalin waɗanda suke ciyar da dukiyarsu don Allah, kamar ƙwaya ce da ta tsirar da zangarniya bakwai. A jikin kwowace zangarniya akwai ƙwaya ɗari, Allah yana riɓanyawa ga wanda ya so. Allah mai yalwatawa ne, Masani.} (Bakara: 261).*

Alƙur'ani kuma yana ba mu labari cewa, bayar da dukiya ga mabukaci tsarkaka ne ga rai, tsaftata ne ga reshi. Wannan, kamar yadda Allah ya yi wa Manzonsa magana da cewa: *{Ka karɓi sadaka daga dukiyarsu, domin ka tsarkake su, ka kuma tsaftace su da ita.} (Taubah: 103).*

Haka nan ya ba mu labarin cewa, wanda yake rowar dukiyarsa, ta hanyar ƙin bayar da ita; ya ƙi taimaka ma talakawa da miskinai, shi ne farkon masu hasara; domin ya yi ma kansa rowar arzikin duniya da lahira.

Ya zo a cikin alƙur'ani cewa: *“Ga ku nan ya ku waɗannan! Ana kiran ku domin ku ciyar ga tafarkin Allah, sa'annan daga cikinku akwai masu yin rowa. Wanda kuma ke yin rowa, to, yana yin rowa ne ga kansa. Kuma Allah ne Wadatacce alhali kuwa ku fakirai ne. Kuma idan kuka juya zai musanya waɗansu mutane, waɗansunku, sa'annan ba za su kasance misalinku ba.” (Muhammad: 38).*

Da zarar an yi sa'ar aiwatar da wannan babban rukuni daga cikin rukunan Musulunci. To, kuwa an share ma cikakken aminci, da adalci irin na ƙeƙe da ƙeƙe, wurin zama a cikin rayuwar jama'a. Saboda haka ne fitar da Zakka tare da bayar da ita ga miskinai, ba ya bayar da dama ga dukiya ta taru cunkus a hannun wasu 'yan tsiraru a cikin al'umma, daga su sai su. Saboda haka ne aka samu, a tarihin Musulmin farko, wasu lokuta da akan ɗauki Zakka da dukiyar agaji a zagaya da ita a cikin garuruwa ana neman mai buƙata, amma a rasa.

Hakan kuma tana tabbatar da danƙon zumunci da narewarsa a tsakanin al'umma, saboda irin yadda halittar ɗan Adam ta azaliyya, aka gina ta a kan tsarin son wanda ya kayautata mata. Da wannan, sai a wayi gari ɗaiɗaikun al'umma sun rayu cikin son juna; tsintsiya maɗaurinki ɗaya, kamar ingantaccen gini, wanda sashensa yake ƙarfafa sashe. Karshe kuma za a rage sace-sace, da ƙwace, da fashi da makami.



## *Azumi*

Dukanmu muna sha'awar wanda yake da cikakken iko a kan zuciya da rayuwarsa, ta yadda yake iya hana ma kansa wani nau'i na abinci don tabbatar da kiwon lafiya, da rage nauyin jiki da jini, bisa umarni da shawarar likita. Sai mu ga wannan wata irin gagarumar nasara ce da cigaba ga damar da ya samu ta mallake sha'awarsa, don cimma wata manufa mafi girma da muhimmanci.

To, azumi da Musulmi suke yi, ya fi wannan ban sha'awa, da bayar da horo ga jikinsa, da kuma bayyana ƙarfin iko a kan sha'awa da zatin ransa, a matsayin ɗa'a da biyayya ga Sarkin Sarakuna, Allah Maɗaukakin Sarki.

Azumi shi ne rukuni na hudu daga cikin rukunan Musulunci. Saboda haka, wajibi ne ga duk wanda ya yi imani, yake kuma da iko, ya riƙa yin azumi, ta hanyar nisantar duk abin da yake ɓata shi, da suka haɗa da kamar abinci, da abin sha, da saduwa da iyali, daga hudowar alfijiri zuwa faɗuwar rana, a kowace rana tsawon kwanakin watan Ramadhan, wanda shi ne wata na tara a tsarin watannin Musulunci.

Sa'annan kuma Annabin Musulunci, ya faɗakar da cewa, duk wanda yanayin rayuwarsa bai canza ba, ɗabi'u da halayensa kuma ba su kyautata ba bayan azumi, to, azuminsa ba bai ƙara shi da komai ba.

Alƙur'ani yana gaya mana cewa, Azumi, wani abu ne da aka wajabta ma al'ummomin da suka gabace mu, duk da yake tsarin nasu azumin ya sha bamban da namu, a wasu lokutan. Amma, dai manufar ɗaya ce; ba ta canzawa, wato tabbatar da bauta ga Allah da jin tsoron sa.

Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗa a cikin Alƙur'ani: *"Ya ku waɗanda suka yi imani! An wajabta azumi a kan ku, kamar yadda aka wajabta ma waɗanda suka zo gabanin ku, tsammaninku kuna yin taƙawa." (Baƙara:183).*

Yayin da Musulmi ya yi nasara a kan sha'awarsa ta halaliya a wasu lokuta a kowace rana, tsawon kwanakin nan ƙirgaggu. To, zai zama shugaba ga ransa, mai ikon kamewa da riƙe linzaminta kar ta faɗa cikin sha'awa ta haram a sauran rayuwarsa. Bisa haka ne ma Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya faɗakar game da wanda yanayinsa bai sauya ba, halayensa ba su kyautata ba, bayan an gama azumi cewa, bai fa'idantu da komai na azuminsa ba. Annabi yace: *"Duk wanda bai daina faɗin karya ba da aiki da ita ba, Allah ba ya buƙata da ya bar abincinsa ko abinshansa." (Bukhari: 1804).*

Yunwar mai azumi da ƙishirwarsa, sukan zama mafi girman masu zaburar da shi zuwa ga taimakon mabuƙata, da mayunwata, waɗanda ba su da ci da sha na yau balle na gobe. Ba kuma su suka zaɓi zama haka ba, domin sun buga sun raya amma, abinci ya gagare su samuwa.



A lokacin kuma da Musulunci ya wajabta ma Musulmi azumi, to, ko shakka babu yana tuna masa ne da halin yunwa da buƙatu, da 'yan'uwansa talakawa suke fama da su.

# *Hajji*

Manyan addinai suna da irin tsarinsu na yin balaguro na addini, ta yadda mutane za su bayyana ibada da ƙanƙan da kai ga Mahaliccinsu. Sai dai wanzajjen balaguron da ya fi shahara da bunƙasa tsawon shekaru, wanda ake yin sa duk shekara shi ne tafiya aikin Hajji na Musulunci. Fiye da mutane miliyan uku ne duk shekara, suke haɗuwa a wani ɗan ƙaramin fili, don zartar da wannan balaguro mai tsarki.

**To, Mene ne Matsayin Hajji A Musulunci?**

Hajji shi ne rukuni na Biyar daga cikin rukunan Musulunci, da ba ya wajaba sai sau ɗaya ga wanda yake da iko na dukiya da lafiya.



Wani balaguro ne mai matukar girma, wanda yake lulluɓe bambancin ƙabila ko jinsi, ko matsayin mulki ko na dukiya, saboda kowa da kowa za a ɗaura tufa iri ɗaya, mai launi ɗaya, suna bayyana kirari iri ɗaya, wanda yake nuna alaƙar mutum da Ubangijinsa, wato: (Labbaikal lahumma labbaik. Labbaika la sharika laka labbaik. Innal hamda wanni'imata laka wal mulk. La sharika lak). Ma'ana: *"Amsa maka ya Allah! Amsa maka!! Amsa maka ya Allah! Ga mu mun zo muna faɗa da harasanmu, muna tabbatarwa da zukatanmu cewa, kai kaɗai ka cancanta da ibada, ba waninka ba. Kai ka cancanta da godiya da yabo cikakku. Kai ne Mahalicci mai ni'imtawa, mai mulki, ba ka da abokin tarayya."*

Saboda haka Hajji, wata tafiya ce ta buɗe ido a duniyar imani, wadda Musulmi yake kaiwa da komowa tsakanin wasu yanaye-yanaye, da wasu ayyuka, da wasu zantuka, waɗanda manufarsa a cikin gaba ɗayansu, ita ce tuna Allah, da Ambato, da kuma tsoron sa. Sa'annan da bayyana tsananin fatara da buƙatarsa gare shi, subhanahu wa ta'alah, da kuma neman gafara, da lada daga gare shi. Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Hakiƙa an sanya ɗawafin ɗakin Allah da sa'ayi ne kawai, a lokacin aikin Hajji don samar da tuna Allah da ambaton sa." (Ibn abi Shaibah:15334).*

Shi kuwa tufan da wanda ya nufi garin Makka don gudanar da ibadar Hajji yake sa wa, bayan ya tuɓe tufafin da suke jikinsa, wato, zannuwa biyu farare, nuna matukar ƙanƙan da kai ne ga Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma daidaita kai da duk wanda ya zo da nufin aikin Hajji.




Mafi

Mafi yawan iyali a wannan zamani namu, suna nufin tarayyar wani rukuni na ɗaiɗaiku, da suke amfani da makullin gida ɗaya, da suke zaune a ciki.

Amma, sai ga shi mutane da dama suna ƙokarin tsere ma ɗaukar nauyin mata da ‘ya’yansu. Saboda haka me zai hana ya karkata akalar jin daɗi da biyan buƙatarsa zuwa inda ba sai irin wannan nauyi ya hau kansa ba?!

Duk da yake ana ganin kamar sai a wannan zamani namu ne, aka fara samun irin wannan tunani. A haƙiƙanin gaskiya abin ya daɗe yana bijirowa ga tunanin wasu mutane tun farkon tarihin duniya. A tantagaryar gaskiya kuwa, ba komai ba ne illa tsabar son kai, ba tare da la’akari da abin da hakan zai haifar ga mutum da sauran jama’a ba.

Daga wannan matashiya ne, Musulunci ya zo, ya kuma ƙarfafa sha’anin kafawa da kula da iyali, ta hanyar shata tsare-tsare, da haƙƙoki, da wajibai na ɗaiɗakun iyali. Saboda gida, da iyali a Musulunci su ne babbar cibiya ta faɗakarwa, da tarbiyya, da cigaba. Saboda haka kafawa, da ingantawa, da kula da tabbatar da manufa da saƙon iyali, amfani ne ga iyalin da sauran al’umma.

## Za Ka Iya Ganin Wannan Irin Kulawa A Fili Cikin Hukunce-Hukuncen Da Ba Su Kirguwa. Ga Kaɗan Daga Cikinsu:

**1**

### Musulunci ya ƙarfafi yin aure da samar da iyali, ta hanyoyi kamar haka:

- Musulunci ya sanya aure da samar da iyali a cikin mafi girman ayyuka da sunnonin Manzanni. Lokacin da wasu daga cikin Sahaban Annabi *sallallahu alaihi wa sallam*, suka yi nufin shagaltuwa da ibada, su yi ta kwana Sallah, suna yini azumi kullum, su ƙaurace ma aure. Sai ya tabbatar musu da cewa: *“Kar ku manta fa! Ni, ina azumi, ina kuma shan ruwa. Ina yin Sallar dare, ina kuma kwanciya. Ina auren mata. To, ku sani duk wanda ba ya kwaɗayin sunnata, ba ya tare da ni.” (Bukhari: 4776).*
- Idan Alƙur’ani ya tashi magana a kan ni’imomi da ayoyin Allah a kan bani Adama, yakan lissafa mace a farko, a matsayin abin da ya halitta masa, don samun natsuwa da rahama, da ɗebe kewa a tsakaninsa da ita, kamar yadda ya ke cewa: *“Yana kuma daga cikin ayoyinsa, da ya halitta maku mata daga gare ku, domin ku natsu zuwa gare su, ya kuma sanya soyayya da rahama a tsakanin ku.” (Rum:21).*
- Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni da sauwaka al’amurran aure, ya kuma yi alƙawarin taimaka ma duk wanda ya yi niyyar yin sa, kamar yadda Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *“Mutane uku, sun cancanci Allah ya taimake su….”* Bai ƙare lissafa su ba, sai da ya ambaci *“Wanda ya ƙulla azamar kare kansa ta hanyar aure.” (Tirmizi:1655).*
- Sa’annan ya umurci matasa, a lokacin da suke ganiyar ƙarfi da ƙuruciyarsu da su yi aure, saboda natsuwa da kwanciyar hankalin da za su samu a cikin sa, da kuma samun mafita a shar’ance daga ƙarfin sha’awa da kwaɗayinsu.

> Kuma a duk lokacin da Alƙur’ani yake magana a kan ni’imomi da ayoyin da ya yi ma ɗan Adam, to yana lissafawa a cikin na farko, ni’imar natsuwa da soyayya da rahamar da ya sanya tsakanin namiji da matarsa.



## 2

### Musulunci ya ba wa kowane ɗaya daga cikin iyali cikakkiyar girmamawa, namiji ne ko mace:

Saboda tabbatar da wannan manufa, sai Musulunci ya ɗora babba nauyi a kan iyaye maza da mata, na tarbiyyar 'ya'yansu. Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Dukan ku masu kiwo ne. Kowannen ku abin tambaya ne a kan kiwon da aka ba shi. Shugaba mai kiwo ne, abin tambaya ne kuma a kan kiwon da aka ba shi. Namiji mai kiwo ne a kan iyalinsa, shi ma abin tambaya ne a kan abin da aka ba shi. Mace mai kiwo ce a gidan mijinta, za a kuma tambaye ta a kan kiwon da aka ba ta. Bawa mai kiwo ne a cikin dukiyar shugabansa, abin tambaya ne kuma a kan kiwon da aka ba shi." (Bukhari :853).*



"Haka nan kuma Musulunci ya hana wuce wuri a cikin mu'amala da uwaye ta fuskar kalami da aiki, ko da ta hanyar ɗaukaka sauti da murya a kan tasu ne, da yake nuna raki zuwa gare su ko kosawa da su.

## 4

### Sa'annan kuma Musulunci ya yi umarni da kiyaye haƙƙin 'ya'ya maza da mata da wajabcin adalci tsakanin su a ciyarwa :

Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Ya isa laifi ga mutum ya tozarta wanda yake ciyarwa." (Abu dawud:1692).* Game da kulawa da ciyar da 'ya'ya, musamman mata, kuma, *sallallahu alaihi wa sallam,* ya ce: *"Duk wanda ya jicinci wani abu na 'ya'ya mata, ya kyautata musu, za su zamar masa garkuwa daga wuta." (Bukhari: 5649).*

## 3

### Haka kuma Musulunci ya kwaɗaitar a kan gina harsashin girmama iyaye maza da mata, da ba su kyakkyawar kulawa, da biyayya da umarninsu har iyakar rayuwa:

Duk irin yadda ɗa ko ɗiya suka girma, to, wajibi ne su girmama mahaifansu, su kuma kyautata musu. Allah, subhahanhu wa ta'ala, kuma ya gwama girmama su da bauta a gare shi, subhanahu wa ta'alah. Ya kuma hana amfani da kakkausa kuma babbar kalima a kan su, ko ɗaga murya a cikin siga mai nuna ana sa-in-sa da su. Allah Ta'alah ya faɗa a cikin Alƙur'ani: *"Kuma Ubangijinka ya hukunta, kada ku bauta ma kowa sai shi, kuma game da mahaifa biyu, ku kyautata kyautatawa. Ko dai ɗayansu ya kai ga tsufa a wurinka ko dukansu biyu, to, kada ka ce musu tir, kada kuma ka tsawace su, ka kuma faɗa musu magana mai karimci." (Isra'i:23).*

## 5

### Ya kuma farlanta wa Musulmi sada zumunta:

Ma'anar sadar da zumunta ɗin nan kuwa shi ne, kyautata wa 'yan'uwa na ɓangaren uwa ba uba. Musulunci ya lissafa sadar da zumunta a ɗaya daga cikin mafi girman ibada da neman kusanci ga Allah. Ya kuma tsawatar daga yankewa ko munana alaka tsakanin 'yan'uwan zumunta, tare da lissafa hakan ɗaya daga cikin mafi girman zunubai. Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam,* ya ce: *"Mai yanke zumunta ba zai shiga Aljannah ba." (Muslim :2556).*



# Matsayin Mace A Musulunci

Duba na gaggawa game da tallace-tallace da sanarwowi da a keyi a talabijin, ko a allunan kan hanya, ko a bangayen mujallu, zai nuna mana girman laifin da cigaban zamani yake haifarwa a kan Macce. A mafi yawan lokuta an maida ita zabari, ko kadara, ko mayen ƙarfen da zai motsa sha'awar mutane da kunna wutar shawagin tunani da hankalinsu.

Wa *la'allah*, wannnan mummunan matsayi, faɗaɗawa ne na nau'in wulakancin da Macce ta haɗu da shi hannun al'ummomin farko, da ba su da cikakkiyar wayewa, waɗanda aka ɗauka a matsayin wani kaya da ake ciniki da saye da sayar da shi.

Macce, da aka daɗe ana ɗanɗana ma wannan irin zalunci da wulaƙanci, ba ta taɓa tunani, tattare da gwagwarmayar da take yi a zamanance, na neman 'yanci na yadda za ta tsira daga wannan irin mummunan yanayi ba, sai ta hanyar da, da kaɗan ta ɗara wannan tsarki da sauƙi.

Amma Musulunci, zuwansa yake da wuya, tun shekaru 1400 da suka wuce, ya ɗaura yaƙi don kawo wani irin juyin juya hali na fatattakar munanan ɗabi'un da suka zalunci Macce, inda ya tsara dokoki da hukunce-hukunce da za su kiyaye mata haƙƙi da mutuncinta, don ta rayu tana da ƙima da mutunci, ta samu damar sauke nauyinta na rayuwa a mafi tsaftar hanya.

Don haka ne aka ambaci ɗaya daga cikin Surori masu tsawo a cikin sURORIN Alƙur'ani da 'Surar Mata.' saboda abin da ta ƙunsa na fayyace hukunce hukuncen da ya shafi Mata. Haka nan Allah, a cikin Alƙur'ani ya ba mu labarin wasu daga cikin mata na ƙwarai. Kai! har Sura sukutum ya ambata da sunan wata Macce, wato 'Maryam' mahaifiyar Annabi Isa *alaihissalam*.

A taƙaice Musulunci ya zo da wani samfurin darasi, da ke nufin canza yanayin kallon da ake yi ma Macce don ta dawo kamar yadda Allah ya halicce ta; mutum ba kadara ba, a matsayin ta na abokiyar rayuwa ba ƙawar dare ɗaya ba. A wayi gari ana mu'amala da ita da natsuwa, da ƙauna, da jinƙayi, ba kawai don sha'awa ba ko jin daɗi ba.

> Sai kuma ga shi, an wayi gari ana tuhumar waɗansu tanade-tanade na Musulunci, da zaluntar Macce, da danne haƙƙokinta, da rashin dacewar tanade-tanaden, a nasu ra'ayi, da tanade-tanaden sauyin zamani da wayewa. Amma, tattare da haka sai ga shi muna gani ƙuru-ƙuru kashi 75% na sababbin musulunta a ƙasashen da suka ci gaba, kamar Burtaniya, Mata ne. Musamman, bayan sun nazarci hukunce-hukunce da shari'o'in da Musulunci ya tsara dangane da warware matsalolin iyali (Jaridar Independent 6 /11/ 2011). To, me ya sa?!!



## Ga Kaɗan Daga Cikin Hukunce-hukuncen Da Ke Magana A Kan Mutunta 'Ya Mace:

- *Haƙkin Zaɓar Miji:* Musulunci ya ba wa Macce 'yancin zaɓar mijin aure, ya kuma damƙa mata kaso babba na tarbiyyar 'ya'ya. Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam* ya ce: *"Mace mai kiwo ce a gidan mijinta, za a tambaye ta kuma a kan kiwon da aka ba ta." (Bukhari: 853).*
- *Amfani da Sunan Mahaifinta:* Haka nan kuma ya ba ta 'yancin cigaba da amfani da sunan mahaifinta, ba tare da canjawa ba, ko bayan ta yi aure. A maimakon haka, za a cigaba ne da kiran ta da sunan mahaifinta da zuri'ar gidansu na haifuwa.
- Mallakar Dukiya: Sa'annan kuma ya daidaita ta da namiji a cikin a'amurra da yawa, da suka haɗa da kamar hulɗa da mu'amala irin ta dukiya, har Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam,* ya ce: *"Mata yan uwan Maza". (Abu Dawud: 236).*
- Ɗaukar Nauyi: Haka nan kuma Musulunci ya wajabta ma jinsin namiji ɗaukar nauyin da kulawa da jinsin Macce, ta hanyar ciyarwa da sauran buƙatun rayuwa, ba kuma tare da ya goranta Mata ba. Da zarar ciyar da Macce ya wajaba a kan mutum, a matsayinta na mahaifiya, ko mata, ko 'yarsa, to, ɗaukar sauran nauye-nauyenta yana kansa.

- Haƙkin Gado: Musulunci ya ba Macce haƙƙinta na gado, ta hanyar rabo mai cike da adalci, inda take ɗaukar daidai kason da namiji zai ɗauka a wani yanayi, take kuma ɗaukar fiye da shi ko ƙasa ga shi a wani yanayin, gwargwadon kusancinta da nauyin ciyarwa da ke kan ta. Yana daga cikin ƙarancin nazari, wani ya kafa hankalinsa game da inda aka rage gadon Macce a kan namiji kawai, ya ƙi yin duba ga abin da Allah ya wajabta ma namiji na nauye-nauyen dukiya, kamar ciyar da Macce. Musulunci tsari ne cikakke mai adalci, da ba ya sa wani sashi ya zaluci wani sa shi.
- Tausayawa: Musulunci ya ƙarfafa daraja da falalar tausayawa da yi ma Macce mai rauni, wadda ba ta da kowa, taimako da hidima, koda ba ta daga cikin makusantansa. Yin haka a Musulunci yana daga cikin mafi girman ayyuka a wurin Allah. Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Mai taimakon gwauruwa, da talaka kamar mai yin jihadi ne don ɗaukaka kalimar Allah, kamar mai raya dare ne ba ya hutawa, kamar mai azumi ne da ba ya shan ruwa." (Bukhari :5661).*

> Sa'annan Musulunci ya kuma ba ma ɗiya Mace kaso na gaskiya da adalci da girmamawa a haƙƙinta na gado, wanda a wani yanayi Macce takan yi kunnen doki da namiji, a wasu wuraren kuma yakan ɗara ta da wani abu, ko ma ta fi shi.

## Matan Da Musulunci Ya Ƙarfafa Kulawa Da Su:

**Uwa:** Haƙiƙa, wani mutum ya zo wajen Manzon Allah *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Ya Manzon Allah! Wa ye ya fi cancanta in kyautata ma mu'amala? Sai Annabi ya ce: "mahaifiyarka." Sai ya ce: Sa'annan wa? Sai ya ce masa: "mahaifiyarka." Sai ya kara cewa: Sa'annan wa? Sai ya ce masa: "mahaifiyarka." Sai kuma ya sake cewa sa'annan wa? Sai ya ce: "Sannan mahaifinka." (Bukhari :5626).*

**Falalar Kula da 'Ya'ya Mata:** Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Wanda duk yake da 'ya'ya mata uku ya yi haƙuri da su, ya ciyar da su, ya shayar da su, ya tufatar da su daga ƙokarinsa, za su zamar masa garkuwa daga wuta ranar Kiyama." (Ibn Majah: 3669).*

**Falalar Kula da Matar Aure:** Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya ce: *"Mafi alherinku shi ne wanda ya fi alheri ga iyalinsa. Ni kuwa ni ne zakaranku a fagen kyautata ma iyali." (Turmizi : 3895).*





> Alaƙar da take tsakanin jinsin Macce da na Namiji kuma, a idon Musulunci, alaƙa ce ta agaza ma juna, ba ta ƙiyayya da gwada ƙarfi ba. Bisa wannan tsari, sai kowane ɗaya daga cikinsu yake cika tare da toshe kafar da ɗaya ya kasa, a cikin gina nagartacciyar al'umma Musulma.

## Babu Filin Jajayya Tsakanin Maza Da Mata A Musulunci:

A tsarin Musulunci babu filin jayayya, balle gwabza yaƙi tsakanin jinsin Maza da na Mata. Gwargwarmaya a kan abin duniya, ba shi da wata ma'ana a Musulunci, balle wani alfanu ga kwaɗayin namiji ya yi nasara a kan Macce, ko Macce ta yi nasara a kan namiji, ko ƙoƙarin wani game da cin mutuncin ɗayansu, da kunyata shi da bibiyar gazawarsa!

Yaya mutum zai yaƙi rabin jikinsa, yaya shaƙiƙi zai yi rigima da shaƙiƙinsa, ita Macce kamar yadda Manzo mai girma yake faɗa shaƙiƙiyar namiji ce kuma rabin jikinsa, alaƙar tsakaninsu cikakkiya ce, kowa yana toshe tawayar ɗan uwansa wajen gina al'umma Musulma.

Alƙur'ani ya suranta mana wannan irin cikakken tsari mai ƙayatarwa, da cewa da ya yi: *{Su tufa ne a gare ku, kuma ku tufa ne a gare su} (Baƙara : 187).*

Abin da namiji yake gani a matsayin raunin Macce, ba wani abu ba ne illa wani nau'i na ƙarfi da shi namiji ba zai iya yinsa ba, balle ya kyautata shi. Sa'annan kuma iyali suna buƙatarsa. Abin da ita ma take gani tawaya ne ga namiji, ta yiwu ya zama wani nau'i na abubuwan buƙatar da ita bai dace da ita ba, sa'annan kuma tsarin rayuwa da gina al'umma ba za su tabbatu ba, sai da su.

Ka san ba zai yiwu ba Allah Maɗaukakin Sarki ya halicci jinsin mutane biyu; Namiji da Macce, daban-daban, sa'annan wani ya ce wai: wajibi ne nau'in nan biyu su yi daidai a komai. Wannan wani nau'i ne na wasa da hankali.

Lokacin da wasu maza suka yi kwaɗayin irin haƙƙoƙan da aka ba wa mata, wasu Mata kuma suka yi kwaɗayin irin haƙƙoƙan da aka ba wa Maza, sai ayoyin Alƙur'ani mai girma suka sauka suna cewa: *{Kar ku riƙa kwaɗayin abin da aka fifita sashenku a kan sashe. Maza suna da rabon abin da suka tsiwirwirta, Mata ma suna da rabon abin da suka tsiwirwirta. Kuma ku roki Allah daga falalarsa.} (Nisa'i : 32),* ko wanne daga cikinku yana da abin da ya keɓanta da shi; kowa da irin aikinsa da irin matsayinsa. Haka nan kowa yana ƙoƙarin sauke nauyinsa don neman falalar Allah da yardarsa. Shari'a ba ta zo ba ne don Maza kawai, ko don Mata. Ta zo ne don mutane baki ɗaya; iyali da al'umma Musulma.




## Alaƙa Tsakanin Namiji Da Macce:

Tsarawa da ƙulla alaƙa tsakanin Namiji da Macce, ta hanyar tsara iyakoki, da dokoki, da al’adu, da ɗabi’u, waɗanda aka tsara don yin hakan, yana daga cikin ƙoƙarce-ƙoƙarce da babu inda ba a yi su ba a faɗin duniya, tsawon tarihin samuwar ɗan Adam a bayan ƙasa, a cikin siga mai wuyar ƙididdigewa da bibiyar kadi. Amma tattare da haka, littafan tarihi da ilimin halayyar mutum, sun yi iya ƙoƙari na ba mu labarin wasu mutane waɗanda ba su ganin laifin yin tsirara, ko cakuɗa tsakanin Maza da Mata, da mutanen da suke ɗaure Mace da mari tsoron kar ta lalace, wasu kuma suna kulle Maza su bar Mata, ko su fi damuwa da suturta wani ɓangare na jiki su bar wani, da sauran su, da za su yi wahalar ƙididdigewa.

Mafi rinjayen waɗannan al’ummomi kuwa, da suke haka, musamman waɗanda ake ganin sun waye sosai, suna ganin lallai alaƙa tsakanin Maza da Mata, lamari ne da ke buƙatar wani tsari ko wata doka da za a tafi a kan ta, gudun kada rayuwa ta koma irin ta dabbobi a daji ko a kogo, a wayi gari duk wani bambanci da ke akwai tsakanin Mutum da dabba, ya gushe.

Mafi rinjayen waɗannan al’ummomi kuwa, da suke haka, musamman waɗanda ake ganin sun waye sosai, suna ganin lallai alaƙa tsakanin Maza da Mata, lamari ne da ke buƙatar wani tsari ko wata doka da za a tafi a kan ta, gudun kada rayuwa ta koma irin ta dabbobi a daji ko a kogo, a wayi gari duk wani bambanci da ke akwai tsakanin Mutum da dabba, ya gushe.

## Ɗabi’ar Alaƙar Namiji da Macce A Musulunci :

Alaƙar Namiji da Mace a Musulunci ba aba ce da aka bari ƙarƙashin ƙoƙarin mutum ya tsara ba, ta hanyar amfani da tarihi da ilimin Jogurafi. Tsari dai ne cikakke, mai dacewa da kowane zamani da wuri, wanda Allah ya saukar a cikin Alƙur’ani mai girma, Manzonsa kuma mai girma, Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam* ya karantarhi.

Sai dai wannan alaƙa tana sassaɓawa gwargwadon matsayin Mace ga Namiji. Ga yadda Musulunci ya fayyace al’amarin:

## Matsayin Maza Ga Mace A Musulunci Ya Kasu Kamar Haka :

**1. Mijinta:**

Idan namiji, miji ga Macce, ba wata hujja ko bayani game da ɗabi'ar alaƙa tsakanin ma'aurata, wadda za ta gamsar, face siffantawar da Alƙur'ani ya yi game da haka. Ta tabbata cewa, Allah ya ambaci Miji a matsayin tufa ga matarsa, Macce kuma tufa ga mijinta. Wannan wata siffa ce mai ƙayatarwa da take bayar da hoton alaƙar tausayi, da jinƙayi na rai da gangar jiki, da ke tsakanin Mata da mijinta, da Alƙur'ani ya ce: *{Su tufa ne a gare ku, kuma ku tufa ne a gare su.} (Baƙara :187).*

**2. Muharramanta:**

Namiji na iya zama muharrami ga Macce, wato, wanda aure ba ya halasta a tsakaninsu har abada, sakamakon matsanancin kusanci. Irin waɗannan Maza makusanta kuwa su 13 ne, da suka haɗa da Uba, da kaka, da ɗa, da ɗan'uwa, da baffa, da kawu, da ɗan ɗan'uwa ko 'yar'uwa, da jika na wurin ɗa ko ɗiya, da sauransu. Ya halasta ga Macce ta bayyana gaban ɗaya daga cikin waɗannan makusanta ko ba sanye da cikakken hijabi ba; yadda dai aka al'adanta, amma ba cikin tsiraici ba.

**3. Ajanabinta:**

Abinda ake nufi da ajanabi, shi ne dukan namijin da ba maharramin mace ba.

To, Musulunci ya shimfiɗa ƙa'idoji da doki akaƙa tsakanin mace da irin wannan namiji, domin kariya da mutunci, da toshe ƙofofin Shaiɗan ga mutum. A matsayinsa na wanda ya halicci mutum, *subhanahu wa ta'alah*, ya fi kowa sanin abin da ya fi dacewa da shi, kamar yadda Alƙur'ani yake cewa: *"Ashe wanda ya yi halitta bai fi sani ba, alhali mai jinƙayi ne kuma masani." (Mulku:14)*

### Me Ya Sa Musulunci Ya Shar'anta Rufe Jiki Ga Mace A Gaban Maza Ajanabai?

- Musulunci ya yi haka ne don Macce ta samu damar gudanar da hidimominta na rayuwa, a fagagen ilmi, da aiki, ta hanyar da ta dace, tare da kiyaye mutunci da darajarta.
- Karantawa da sauƙaƙa hanyoyin ruɗi da motsa sha'awa don a samu tsarki a cikin al'umma ta wata fuskar, da kiyaye mutuncin Macce ta wata fuskar daban.
- Taimaka ma Maza masu kallon Mace a kan kamewa da fin ƙarfin sha'awarsu. A haka sai su yi mu'amala da Macce a matsayin mutum mai cikakken 'yancin gudanar da rayuwa, da walwala ta fannin ilimi da wayewa, kamar yadda suke da ita, su Maza. Ba su mai da ita kwandon motsa sha'awa ba, ko kayan wasa da jin daɗi kawai.



## Ƙa'idodin Alaƙa Tsakanin Namiji da Macce Ajanabiyya:

**1. Ɗauke Kai:**

Allah ya umarci Maza da Mata, da ɗauke kai, ma'ana ɗauke idanu da rashin ƙura ido irin wanda yake motsa sha'awa. Saboda hakan wata hanya ce ta kiyaye mutunci, kamar yadda sakar ma gani linzami ba tare da wani dabaibayi ba, hanya ce ta faɗawa cikin zunubi da alfasha, kamar yadda Alƙur'ani ya faɗa cewa: *Ka gaya ma muminai maza su kame daga ganinsu, su kuma kiyaye farjojansu. Haka shi ne mafi tsarki a gare su. Hakiƙa Allah yana sane da abin da suke aikatawa. Ka kuma gaya ma muminai mata su kame daga ganinsu, su kuma kiyaye farjojansu…." (Nur:30-31).*

**2. Ladubba da halayen Kirki:**

Namiji da Mace, a lokacin aiki ko neman ilimi, ko wata harka ba waɗannan ba, wajibi ne alaƙarsu ta zama a kan ladabi da halayen ƙwarai, da kuma girmama juna, tare da nisantar duk abin da yake motsa sha'awa ta kowace irin hanya ce.

**3. Rufe Jiki:**

Allah ya shar'anta ma Macce rufe dukan jikinta, saɓanin namiji, saboda irin yadda ya halicce ta, a cikin siga mai kyau, da sauran abubuwa masu tayar da hankalin namiji. Wannan ya sanya ta zamo wata fitina ga Namiji fiye da yadda Namiji ya zamo fitina gare ta. Saboda haka ne za ka ga abin da ya fi rinjaye tun tsohon tarihi zuwa yau, shi ne amfani da mace don motsa sha'awar namiji, ba amfani da namiji don amotsa sha'awar mace ba. Muna ganin wannan a fili da idanunmu a kafafen sadarwa daban-daban na yau.

Iyakar wannan rufe jiki kuma a Musulunci ga Macce, shi ne rufe gaba ɗayansa, ban da fuska da tafukan hannu a duk lokacin take tare da Maza ajanabai, kamar yadda Alƙur'ani ya yi umarni cewa: *"Kada kuma su bayyana ƙawarsu sai fa abin da ya bayyana daga gare ta." (Nur:31).*



> Mafi yawan masu sukan hijabi a musulunci sun mance photon mafi girman mata a tarihin duniya kamar yadda ake zana Maryam albatul za kaga da hijabi ake zana ta, kuma yanayin kama da hijabin musulmai.



# Dokar Musulunci Game Da Ci Da Sha

Bisa al'ada, farkon tambayar da wanda yake son bincike a kan Musulunci yake yi ita ce: Me ya sa Musulunci ya haramta giya da Alade?

Don amsa wannan tambayar, lalle muna buƙatar muhimmin bayani:

Alƙur'ani ya halasta ma Musulmi duk abin da yake duniya don su yi amfani da shi. Nassin Alƙur'ani ya zo ƙuru-ƙuru a kan cewa an halitta mana duk abin da yake cikin duniyar nan don mu yi amfani da shi. *(Bakara : 29).*

Daga cikin waɗannan abubuwa kuwa akwai abin ci da abin sha. Dukkansu halas ne, sai wanda Alƙur'ani ya togace don zamansa ƙazanta, ko cutarwarsa ga lafiya, ko gusar da hankali. Ta yiwu ka yi burin sanin abin da ya sa aka haramta Alade da kayan maye.

## Alade

Haramcin cin naman Alade ya zo kai tsaye a cikin Alƙur'ani, tattare da cewa Alade ba sanannar dabba ce ga Larabawa ba. Saboda haka wasu suke mamakin wannan haramci, har suna sukar lamirinsa, alhali kuwa ba ga Musulunci farau ba; ko ga Yahudawa, cin naman Alade haram ne. Nassosan da suka zo da wannan haramci bayyane suke a cikin 'Tsohon Alƙawari.' To, abin mamaki ma duk, bai fi irin yadda da yawa daga cikin malaman addinai, sun tabbatar da cewa nassosa da dama a cikin 'Sabon alƙawari' sun haramta ma Nasara cin naman Alade ba. Sai dai, an daɗe da canza wannan haramci. (Duda Injilar Murƙisu:5/11-13. Mattah:67, Wasiƙar Bulus, Manzo, ta biyu:2/22, Luka:15/11).

Ba abin da zai hana Allah ya jarrabe mu da hana cin wani abu bayan ya halatta mana mafiya yawansa, don ya jarrabi imaninmu da biyayyarmu gare shi, kamar yadda ya jarrabi kakanmu Adam, alaihissalam, bayan ya halatta masa cin tsarkakan kayan Aljannah, sai ya ware wata bishiya ya ce ban da ita.

> Babu abin da zai hana Allah Maɗaukakin Sarki ya jarrabe mu da hana mana wasu ababen ci, bayan ya halasta mana mafi yawansu. Ba laifi ba ne don ya yi haka, subhanahu wa ta'alah, don ya jarraba imani da nauyin ɗa'armu zuwa gare shi. Wannan, kamar yadda ya jarrabi Annabi Adam alaihissalam, bayan ya halasta masa cin duk abin da yake so daga cikin abincin Aljanna, ta hanyar haramta masa cin wata keɓantacciyar itaciya.





## Giya Da Sauran Kayan Maye :

Yaƙi da annoba da cututtuka, waɗanda suke ruguza rayuwar ɗan Adam, da sanya dokoki da tsarin da zai himmatu don kare lafiyar mutane da rayuwarsu, yana daga cikin ayyuka mafi muhimmanci, da dauloli da hukumomi, suka himmatu a kai, wanda da zarar an samu cikas hakan zai haifar ma ɗaiɗaiku ko al'umma baki ɗaya, da mummunan sakamako aibi.


Ta yiwu dukkaninmu, mu yarda da wannan bayani ta hanyar gamsasshen nazari, da ya zama rahoton cibiyar kula da lafiya ta duniya, da nazarin da Jami'ar Oɗford ta yi a Mujallar Nature 483 ta yaɗa a ranar 15 ga watan Maris, 2012, 275. Da rahoton Cibiyar Kula da Lafiya ta Duniya 11/2/2011 ta fitar, cewa adadin waɗanda giya take yin layya da su a shekara ya fi adadin waɗanda ƙanjamau ko Maleriya ko kansa suke yin layya da su. Ya kuma ninka yawan waɗanda aka kashe a yaƙe-yaƙe sau uku, ko yawan waɗanda aka tarwatsa, ko aka kashe ta hanyar ta'addanci a wannan shekarar. Ga wasu alƙaluma waɗanda za su tabbatar da nazarin tare da rahoton cibiyar lafiya ta duniya.




Fiye da mutane miliyan biyu da rabi ne, suke mutuwa a shekara saboda shan kayan maye. A cikin masu tsaka-tsakin shekaru matasa 'yan shekara **15-29 su 320,000** suke mutuwa a duniya a kowace shekara, ta dalilin kayan maye, wanda yake nuna 9% daga mace-macen da ake yi a shekara a tsakanin masu waannan shekarun ne.





Ya bayyana a nazarin da Amurka ta yi cewa: a shekara ɗaliban Jami'a **700,000** suke lalacewa ta hanyar wasu ɗaliban daban, waɗanda suka zurme a shan kayan maye.



Rahoton tatacce na shekarar **2001** ya bayyana cewa, **80%** na manyan laifukan da ake aikatawa a Astoniya matasa ne suke yin su. Zurmewar su a harkar kayan maye shi ya haifar da haka.





**Ana ƙirga** kayan maye da cewar su suke haifar da ɗaya bisa huɗu na laifukan kisan kai, da ake yi a duniya.




Dukkanin bayanai da rahotannin Cibiyar Lafiya ta Duniya, suna kiran gaba ɗayan ƙasashe ne da ɗaukar matakai, da kafa dokoki masu zafi don ƙaranta wannan lamarin, ko su hana laifukan da ake aikatawa a kullum ta dalilin kayan maye.







## A shekara ɗaya rak a ƙasar Burtaniya kaɗai:

- Ana samun miyagun laifuka kusan miliyan ɗaya ta hanyar ta'amaui da kayan maye, an lura da cewa kusan rabin miyagun laifuka suna da alaƙa da kayan maye, ta mahangar waɗanda laifin ya aukawa.
- Ana karɓar hatsarori kusan miliyan 7 a Asibitocin Burtaniya sababin faruwarsu shi ne kayan maye. Ana yin hasarar kusan Fam Miliyan 650 na haraji a ƙasar ta Biritaniya ta hanyar hatsarin.
- A dunƙule, ana ƙaddara hasarar da laifukan masu ta'amali da kayan maye da wasunsu, suke jawowa a shekara ya kai Biliyan 8 zuwa Biliyan 13 na kuɗin Burtaniya a duk shekara.



### Yaya Alƙur'ani Ya Yi Mu'amala Da Kayan Maye?



Musulunci bai tsaya sauraren rahoton Cibiyar Lafiya ta Duniya ba, don ya gane illar kayan maye ga ɗaiɗaiku ko al'umma ba, domin wanda ya halicci mutum shi ne masanin abin da ya dace da rayuwarsa ko zamantakewarsa.

Tabbas, Musulunci ya taras da Larabawa a lokacin da ba su rabo da shan kayan maye. Giya da dukkan danginta su ne mafi girman jin daɗinsu, mafi tsadar abu a wajen su. Saboda ita suke alfahari, suke ɓarnatar da duk abin da yake wajensu na dukiya.

Ganin haka fa, sai Alƙur'ani ya fuskanci al'amarin a cikin wata hanya mai tsananin adalci da gamsar da hankali, inda ya tabbatar musu da cewa, lalle kayan maye suna da wani amfani, don tana yiwuwa wanda ya sha su, ya samu wata gamsuwa, da hutu, amma na ɗan lokaci, da zai gusar masa da baƙin ciki da damuwa. Sai dai sakamakon hakan kuma ba mai kyau ba ne, in ji shi. Mummunan tasiri a zuci, da rayuwa da ɗabi'u, da lafiya a kan ɗaiɗaiku da jama'a baki ɗaya, wanda ba shi da magani, kamar yadda Alƙur'ani ya faɗa cewa: *"Suna tambayar ka game da giya da caca. Ka ce a cikinsu akwai zunubi babba, da amfani ga mutane. Sai dai zunubinsu ya fi amfaninsu yawa." (Bakara:219).*


Sannan ƙarfafa hanin amfani da giya ya zo, in da Musulunci ya ƙirga ta daga cikin aikin Shaiɗan, wanda yake gadar da ƙiyayya da gaba, da hana mutane aikata manyan lamura masu muhimmanci, har aka tambayi mutane a Alƙur'ani cewa: *{Shin ku ɗin nan ba ku dainawa?}* Sai mutane suka ce: "Mun daina! Mun daina!!.". Suka kuma shiga kwararar da giya a magudanun Madina garin Manzo, don amsa umarnin Allah da ya zo a Alƙur'ani.




Yin 'kuskure' ko yin 'dai-dai' ɗaya ne daga cikin abubuwa masu muhimmanci da kuma rikitarwa a mafi yawan addinai da daman gaske, da suka shafi ɗan Adam da tunaninsa a wasu addinai da aƙidoji. Sai dai tabaran da waɗannan addinai da aƙidoji suke kallon 'kuskure' da 'daidai' da 'zunubi' da 'tuba' da 'nadama' shi ne matsala.

Shi kuwa Musulunci yana kallon ɗabi'ar ɗan Adam, wadda Allah ya halicce shi da ita, da idon basira. Sakamakon haka ya tanadi ma'aunan gane 'alheri' da 'sharri.' Musulunci ba ya kallon ɗan Adam a matsayin wani mala'ika, da bai yin komai sai aikin alheri. Saboda haka ya tabbatar ma duniya da cewa, kowane mutum mai kuskure ne. Sai dai kuma a lokaci ɗaya, yana kama shi da laifin abin duk da ya aikata da zaɓin ransa. Daga nan ne ake iya hange da fahimtar Falsafar Musulunci game da 'kuskure' da 'tuba.' wannan Falsafa kuwa ana iya taƙaita ta kamar haka:

- Farkon abin da za mu ci karo da shi a cikin Alƙur'ani shi ne cewa, duk kuskure da tubar da mutum zai yi, hukuncinsu a bayyanne yake kuma kuma mai sauƙi ne; ba rikici ba wahalarwa a ciki. Ma'ana, abubuwa ne na ƙashin kansa. Babu wani kuskure da za a ce Allah ne ya tilasta mutum ya aikata shi. Kowane mutum ana haihuwarsa tsarkakakke, babu wani zunubi da ya yo dakonsa tun kafin haifuwarsa. Haka kuma babu wani mahaluki da yake da lasisin gafarta ma wani, ko kankare ma wani, zunubi. Haka kuma kuskuren da Annabi Adamu *alaihissalamu* ya yi, ya tsaya kan sa. Ƙarshe kuma ya tuba, Allah ya gafarta masa kai tsaye a cikin sauƙi da sauri. To, haka nan duk kuskuren da wani jika nasa zai yi, ya tsaya a kansa, ƙofar tuba kuma a buɗe take a gabansa. Wannan kuwa wata cikakkiyar dama ce, a cikin siga ta madaidaicin hange, da yake raɗa wa kowane mutum cewa, ya yi ƙoƙari iyakar yinsa, kada kuma ya yanke ƙauna. Musulunci yana ɗora ma kowane mutum laifinsa; ba ya kama wani mai rai da laifin wani. Wannan ita ce ƙa'idar da gaba ɗayan Annabawa suka zo da ita daga wurin Allah, kamar yadda Alƙur'ani ya bayar da labari: "Ko kuwa ba a ba shi labari ba ga abin da yake a cikin Littafin Musa? Da Ibrahimu, wannan da ya cika alƙawari? Cewa wani rai mai kayan laifi ba ya ɗaukar kayan laifin wani. Kuma mutum ba shi da komai face abin da ya aikata. Kuma lalle aikinsa za a gan shi." *(Najm:36-41)*
- Tuba na ɗaya daga cikin manya-manyan ibadoji, da neman kusanci ga Allah Maɗaukakin Sarki, wanda kuma ake karɓa daga duk wanda ya yi shi; ba sai wane ba. Tuba ba shi da buƙatar wani wuri keɓantacce, ko wani mutum da sai a gabansa za a yi, balle neman izininsa. A haƙiƙanin gaskiya, tuba ibada ne, da yake tsakanin Allah da bayinsa. Saboda haka ne ma, daga cikin sunayen Allah da siffofinsa, waɗanda suka fito a cikin alƙur'ani, akwai'attauwabu / arrahimu' da 'gafiruz-zanbi / ƙabilut- taubi'.



A hannu ɗaya kuma sai ga Alƙur'ani ɗin yana lissafa mana siffofin bayi masu tsoron Allah, da tabbas, za su shiga Aljanna, amma kuma ya tabbatar mana da irin yadda suka faɗa tarkon wasu ayyukan zunubi. Amma, kuma nan take sai su yi gaggawar tuba da neman gafara, bayan kowane zunubi. Tabbacin hakan kuwa shi ne faɗar Allah Maɗaukakin Sarki: *"Kuma waɗanda yake idan suka aikata wata alfasha ko suka zalunci kansu, sai su tuna da Allah, saboda su nemi gafarar zunubansu ga Allah. Kuma wane ne ke gafara ga zunubai, face Allah? Kuma ba su doge a kan abin da suka aikata ba, alhali kuwa suna sane." (ali'imran:135)*

Sa'annan kuma iyakar abin da tuba ke nema a Musulunci, shi ne mutum ya nisanci zunubin kwata-kwata, sa'annan ya yi nadamar aikata shi da ya yi a can baya, da kuma niyyar ba zai sake aikatawa ba. Idan haƙƙoƙan wasu mutane ne kuma ya taba, to, ya mayar musu da abinsu. Idan aka ƙaddara masa sake aikata zunubin, to, ba za a yi watsi da wancan tuba na farko ba, balle a dawo masa da zunubinsa. Wannan wani laifi ne sabo ya aikata. Sai ya yi masa tubar kansa.

Wannan shi ne tanadin da Musulunci ya yi ma rayuwar mutum a cikinsa. Wato, kasancewa tsaka-tsaka; kwaɗayin samun cika da kamala, da ɗaukaka da nisantar kurakurai, da kuma sanin yadda tsarin halittarsa ta azaliyya take a matsayinsa na mutum, wadda rauni na iya bijiro mata a kowane lokaci, har ya iya kai shi ga sakin hanya. Babban abin da Musulunci yake buƙata gare shi a cikin gaba ɗayan waɗannan halaye nashi; na nishaɗi da tsoron Allah, ko na kasawa da karkacewa, shi ne kada ya kuskura ya yi ƙasa a guiwa, balle ya yanke ƙauna da Allah, ya daina dogara gare shi, yana istigfari da neman gafara.

A nan ne bambanci yake bayyana tsakanin salihai da wasunsu, kamar yadda Alƙur'ani ya tabbatar mana lokacin da ya labarta mana cewa haƙiƙanin bambanci tsakanin masu taƙawa da waɗanda ba su ba, shi ne idan suka auka cikin laifi sai su tuna su tuba ga Allah. Saɓanin waɗancan waɗanda suke zarcewa da laifi ba tare da sun faɗaka ko sun wa'azantu ba. *(A'araf:201-202).*



"


A Musulunci babu wani zunubi na azaliyya da yake wuyan mutum tun kafin haifuwarsa. Kowane mutum, a idon Musulunci, ana haifuwarsa ne babu wani zunubi a wuyansa, na tali-tali.



# Zumuntar Addini da Hankali

Wasu suna ganin cewar addini yana cin karo da hankali, yana kuma takinsaƙa da ilimi, saboda a nasu gani, addini ba komai ba ne illa maɓuɓɓugar tatsuniyoyi da miyagun al'adu. A yayin da shi kuwa ilimi da Falsafa hanyoyi ne guda biyu da suke sadar da mutum ga wata masaniya, da yake iya wayuwar gari a matsayin wani tabbataccen ilimi na haƙiƙa idan ya samu cikakkun sharuɗɗan bincike, da tunani, da kuma gwaji. To, idan aka kalli wannan fahimta da kyau, za a fahimci akwai kurakurai a cikinta akwai kuma daidai.

Yana iya zama daidai idan aka kalli irin yadda ake da addinai da dama, da suke takin saƙa da hankali a wasu lokuta. Saboda haka littafansu suke maƙare da tatsuniyoyi da miyagun aƙidu, da suka saɓa wa ilimi da takin ƙasar gaba ɗayan halitta.



Inda kuskuren yake kuwa shine yi wa gaba ɗayan addinai bugun kaɗanya ba tare da la'akari da bambancin da yake akwai tsakaninsu ba, ta ɓangare tushe, da manufofi, da tsare-tsare, da kuma dalilansu.

Duk mai nazarin Alƙur'ani, babban jigon Musulunci, zai tabbatar cewa Musluunci ya ba wa hankali babban matsayi, wanda wani addini bai ba shi ba. Duk wanda yake nazarin Alƙur'ani, ba ya da buƙatar dogon nazari, don ganin irin yadda Littafin yake zaburar da hankali da kira zuwa ga lura da tunani, wanda har ta kai ya maimaita tambaya fiye da sau goma sha uku (13) a cikin sigar inkari, da cewa: *"Shin ba za ku hankalta ba?"*



Duk wanda ya ɗauki Alƙur'ani ya shiga dubawa, ba ya da buƙatar yin nisa ko wani dogon bincike kafin ya iya tabbatar da cewa, Littafin yana zaburarwa tare da kiran mutum zuwa ga tunani da amfani da kaifin hankali da basirarsa a cikin rayuwa.

## Fuskantarwar Da Alƙur'ani Yake Yi Zuwa Ga Amfani Da Hankali Tana Bayyana Ta Lamurra Da Yawa Kamar Haka:

1 Alƙur'ani yana magana da mutum ne a matsayinsa na halitta mai hankali, wayayye, 'yantacce daga dukkan wani nau'i na koma-baya, da girman kai, tsoro, domin ya lurar da shi wajabcin imani da Allah ta dalilai da hujjoji na hankali, masu yawa, da suka haɗa da faɗar Allah: *{Ko an halicce su ne ba daga komai ba? ko su ne masu halitta? ko su ne suka halicci sammai da ƙasa? Kawai dai ba su sakankancewa} (Ɗur :35,36).*

2 Yana kuma tattauna hujjojin waɗanda suka ƙi miƙa wuya, yana yin biris da zantukansu, waɗanda ba su dogara a kan wani dalili ko hujja ba, kamar yadda Allah ya ce: *{Ka ce ku kawo hujjojinku in kun zamo masu gaskiya} (Baƙara :111).*

3 Yana kuma ganin lamarin waɗanda ba su amfani da hankalinsu, tare da misalta su da waɗanda ba su fahimtar komai, saboda irin yadda ba su ƙaruwa da duk abubuwan da suke gani da ji, domin su ɗauki matsayi ingantacce. Misalin wannan shi ne inda Allah yake cewa: *"Me zai hana su yi tafiya a cikin ƙasa, domin zukatansu su zama hanyar hankalta a gare su, kunnuwansu kuma hanyar ji. Hakika, ba idanu suke makanta ba, amma zukatan da suke cikin kiraza, su ke makanta." (Haj:46).*

4 Sa'annan kuma ya yi ma mutum hannunka mai sanda, daga amincewa da duk wani abu da zai bijiro ya hana shi yin tunani a cikin al'amurra. Da wannan Alƙur'ani bai tsaya a kan kwaɗaita mana amfani da gaɓoɓinmu guda biyar na sani, da hankalinmu, da kuma girmama su ba. A maimakon haka, sai da ya tunatar da mu abubuwan da suke kawo ma hankali tasgaro, saboda la'akari da ɗabi'ar mutum, ta miƙa wuya ga zazzargiyar alheri da ta sharri, wanda saboda haka ne a kowane motsi nasa yake iya faɗawa cikin kuskure, da zambiyoyi daga gaskiya bisa dalilin kwaɗayi ko tsoron wani abu, a wasu lokuta, ko ɗaukar hankali.



Kowane Musulmi ya yi imani da cewa, babu yadda za a yi halittar duk da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi, ta kasa iya ɗaukar nauyin tanade-tanaden addini da shari'arsa, da ya shimfiɗa ma mutane. Tunda haka ne kuwa, me zai sa a yi fargaba, ko a ji tsoron tambaya da ba wa hankali cikakkar damarsa? Babu.

**Abubuwa Masu Barazana Ga Lafiyayyen Tunani Kamar Yadda Alƙur'ani Ya Bayyana:**

**Makauniyar Biyayya:**

Makauniyar biyayya kan hana yin lafiyayyen tunani, saboda irin yadda gadon miyagun akidu, da halaye da ɗabi'u, da naƙasassun hanyoyin tunani irin na al'ada, suke da yiwuwar yin tasiri a kan yanayin tunani da hankalin mutum, tasiri babba kuwa, irin wanda yake da wuya ya bar mai yin sa karɓar gaskiya da yi ma ɓarna tawaye. Tana ma yiwuwa a bice hasken tunanin gaba ɗaya, bisa hujjar cewa abin da ake kansa an saba da shi, ko a kansa aka haifi mutum, kamar dai yadda Alƙur'ani yake labarta mana ta bakin wasu daga cikin waɗanda suka ga gaskiya ƙuru-ƙuru, amma makauniyar biyayya ya hana su miƙa wuya gare ta. Domin da aka ce musu: Ku miƙa abin da Allah ya saukar na gaskiya, sai suka ce: ko alama! Za mu dai bi abin da muka saba da shi ne daga cikin abubuwan da muka samu iyaye da kakanni a kai. Daga nan sai Alƙur'ani ya yi ƙarin bayani a kan wannan amsa ta su da cewa: Suna nufin su bi kakannin nasu ne, saboda gabacinsu, ko da ba a kan wata hujja ta hankali, da ilimi, da shiriya suke ba. Alƙur'ani ya ce: *"Kuma idan aka ce musu: Ku bi abin da Allah ya saukar, sai su ce: Za mu dai bi abin da muka isko iyayenmu a kai. To, ko da iyayen nasu ba su hankaltar komai ba su kuma shiriya? (Baƙara:17)*

**Kangara da Girmankai:**

Kangara da girmankai sukan hana yin lafiyayyen tunani, saboda tana yiwuwa gaskiya ta bayyana ga hankali, amma mai shi ya ƙi karɓa balle saurarenta, sai ya juya mata saboda kare wata maslaha, ko wani girma nasa, ko hassada, ko raina fuskar da gaskiyar ta zo masa daga gare ta, kamar yadda Allah yake bayar da labarin wani rukuni na mutane a cikin Alƙur'ani, da cewa: Tabbas! Sun ƙi yarda da gaskiya ne a bayyane, tare da can a cikin zukatansu, sun san da cewa gaskiya ce, haƙƙan. Ba kuma komai ya hana su miƙa wuya a gare ta ba, face girmankai da zalunci. Saboda haka: *{Suka yi inkarinta, saboda zalunci da girmankai, bayan rayukansu sun sakankance da ita – don zalunci da neman girma} (Naml :14).*

**Nutsewa A Cikin Jin daɗi:**

Abu ne mai sauƙi hankali ya gane gaskiya, amma saboda rashin cikakkiyar dama da ƙarfin ikon yin gaban kansa, sakamakon irin yadda mai shi ya nutse a cikin jin daɗin duniya, sai ya kasa karɓawa. Irin wannan mutum ne Alƙur'ani yake buga mana misali da shi, da aka ba shi ilimi da sani, ta yadda ya kamata ya yi amfani da su a cikin rayuwarsa. Amma, sai ya zubar da waɗannan sannai gefe ɗaya, ya bi son zuciya, da biyan buƙatar rayuwarsa na nan take. Ba kuma wani abu ya ja shi ga haka ba sai irin yadda ya nutse a cikin jin daɗi, har ya kai matakin da bai iya yanke wa kansa ingantaccen hukunci. *(A'araf :175,176).*

Alƙur'ani, a kowane lokaci da kowace irin dama, yana kiran mutum zuwa ga yin amfani da hankalinsa, da tambaya, da nazari, da tunani, da izna game da halittar rai da duniya da sauran halittu ba tare da gindaya wasu sharuɗɗa, ko dabaibayi da maruruwa ba.

Iyakar abin da Alƙur'ani yake sauna shi ne, wannan tambaya da tunani su kasance daga mutumin da tun farko bai shirya karɓa da yarda da sakamakonsu ba a cikin ransa. Shi addini, in dai na gaskiya ne, to kuwa daga Allah yake, wanda ya halicci mutum, tare da taskar hankali a cikinsa. Saboda haka kuwa ba yadda za a yi hankali, a matsayinsa na halittar Allah, ya saɓa ma addinin Allah, wanda ya zaɓar ma mutane a matsayin hanyar rayuwa. Idan haka ne kuwa, ai babu wani fargaba idan wannan tambaya da aiki da hankali za su zama kai tsaye ba tare da wani mugun nufi ba. Ko ƙaƙa? Allah Ta'alah na cewa: *"Ku saurara! Halitta da al'amari nasa ne, Allah Ubangijin talikai ya ɗaukaka." (A'araf:54)*

Alƙur'ani, a kowane lokaci da kowace irin dama, yana kiran mutum zuwa ga yin amfani da hankalinsa, da tambaya, da nazari, da tunani, da izna game da halittar rai da duniya da sauran halittu ba tare da gindaya wasu sharuɗɗa, ko dabaibayi da maruruwa ba.



# Musulunci Addinin Zaman Lafiya

Wasu mutane za su yi mamaki sakamakon abin da yake gudana a kafafen watsa labarai, idan suka ji cewa ‘zaman lafiya’ yana da kyakkyawan tanadi a Musulunci. Wanda, hakan ta sa kowane Musulmi yake maimaita kalimar zaman lafiya barkatai a kowace rana, tare da sanin ma’anoninta.

Ga shi kuma kalimar ta *‘assalámu’* daya ce daga cikin sunayen Allah. Gidan Aljanna da ya yi tanadi kuma a Lahira sunansa *‘darus-salam.’* Gaisuwar Musulmi kuma tana farawa ne da kalimar *‘assalam.’* Haka kuma sallarsu, alamar ƙarewarta ita ce maimaita kalimar *‘assalamu’* har sau biyu. Ƙarewa da ƙarau ma, shi addinin kansa sunansa *‘Al-islamu’* wanda a cikin sa akwai samar da kowane irin aminci da natsuwa da kwanciyar hankali.



To, idan kuwa har Musulunci yana kira zuwa ga ‘aminci’ da mutunta haƙƙin mafi raunin dabbobi da ƙaranci iya kare kai, wanda har Manzo Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya labarta mana cewa: *“Za a shigar da wata mata a wuta gobe Kiyama saboda tsare wata kyanwa da ta yi, ba tare da ta ba ta abinci, ko abin sha ba, ba ta sake ta don ta je ta yi farautar wasu ƙwari ta ci ba, har yunwa ta kashe ta.” (Muslim:2242). “Za a kuma saka wata karuwa a Aljanna saboda shayar da kare ruwa da ta yi.” (Bukhari:3280).*



Annabi, a cikin waɗannan Hadisai, yana buga misalai ne masu matuƙar ban mamaki, a matsayin dokokin mutunta haƙƙi da ‘yancin mutane, da kuma yadda za a yi mu’amala da juna, duk da saɓanin da yake a tsakaninmu na addini ko tunani, wanda har Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya sha alwashin cewa, duk wanda ya zalunci wanda ba Musulmi ba, ko ya cutar da shi, ko ya ɗora masa aikin da ya fi ƙarfinsa, cewa shi Annabi, *sallallahu alaihi wa sallam*, da kansa zai zama abokin faɗan sa ranar Kiyama. *(Abu dawud:3052)*.

> Annabi Muhammadu, *sallallahu alaihi wa sallam*, kuma ya yi wa duk wanda ya zalunci wanda ba muslmi ba, ko ya cutar da shi, ko ya ɗora masa abin da ya fi karfinsa, alƙawalin cewa, ya shirya shar’ah da shi, Manzon Allah kansa a ranar Alkiyama.

Sai dai a kula, wannan kira da Musulunci yake yi zuwa ga zaman lafiya tsakanin Musulmi da waɗanda ba su ba, yana nufin tantagaryar zaman lafiya ne irin na adalci, da yake ba wa duk mai hakki, haƙƙinsa, ya kuma hana azzalumi zalunci, mai ƙwace kuma ƙwace, ba irin wancan zaman lafiya na zalunci da yaudara ba, da yake mallaka ma ɓarawo abin da ya sata, mai doki kuma ya koma kuturi.

Ba zaman lafiya irin wanda ba shi da kai, ba shi da gindi ba, wanda da sunansa aka mayar da kafafen watsa labarai, dandalin da waɗansu shafaffi da mai, suke tallata manufofi da akidojinsu, ta hanyar aika wa kowace nahiya abin da zai biya buƙatunsu a can. Ga shi kuma kaɗan ne daga cikin mutane, suke iya haƙurin bincike da ƙoƙarin gane gaskiyar al’amurra, ya kuma ƙalubalanci waɗannan kafafe ya tantance farfagandarsu ta hanyar komawa ga tushe, sa’annan ya yanke ma lamarin hukunci bisa adalci da kaifin basira.

**Ga wasu tabbataccin abubuwan da suka faru, za mu baje su a gabanka don ka yi nazarinsu da kyau:**





## Musulunci Shi Ne Addini Mafi Saurin Yaduwa A Yau:

A yau Musulunci yana yaɗuwa da sauri irin mai matuƙar ban mamaki a sassan duniya, tun daga Amurka zuwa Turai, da Afirka da Asia, kamar yadda cibiyar binciken addinai ta PEW ta faɗa (pewresearch.org). Hakan kuma tana faruwa ne, tattare da ƙarancin kayan aiki, da raunin Musulmi, da mamayewar da kafafen sadarwa na duniya suka yi, don ɓata sunansa ta hanyar yaɗa farfagandar ƙarya, da bayar da mugun hoto game da Musulunci, wanda sam-sam-sam ba shi da alaka da shi. To, wannan yaɗuwa da yake ki, za a ce ta kasance ne sakamaon tilasta wa mutane, ko bisa gamsuwa da zaɓin ransu?

A fili yake ƙuru- ƙuru ga duk mai lura cewa, rungumar da Musulmi suka yi da kula da ‘yancin masu biyar wasu addinai, da kare mutunci, da al’adunsu, ya yi matuƙar tasiri a zukatan mutanen, suka yi ta kwarara suna shiga cikin addinin. Ba wai kuma wani ƙwazo ne na Musulmi suka yi na ƙashin kansu ba. Sun yi ƙokarin tabbatar da wata muhimmiyar ka’ida da doka ne, wadda Allah ya tabbatar a cikin Alƙur’ani ƙuru-ƙuru cewa: *{Babu tilastawa a addini. Lalle shiriya ta bayyana daga ɓata.} (Baƙara :256).*

## Ko Gaskiya Ne Tilastawa Mutane Shiga Musulunci Aka Yi?


Sau da yawa mutun kan yi amfani da ƙarfi don tilasta yarda da ra’ayinsa, da tabbatar maslaharsa. Tarihi cike yake da misalai game da haka, na masu bin wasu addinai da mazhabobin rayuwa daban-daban.

Alal-misali, tarihi ya tabbatar da cewa, firgitaccen kisan kare-dangin da ya faru ga asalin ‘yan-gari, a lokacin da masu bincike da ‘yan kama-wuri-zauna ga sabuwar duniya suka isa gari, kamar yadda babban Fada ɗan kasar Spain Bartolomede de Las Casas ya faɗa, bayan ya ga yadda aka yi layya da ‘yan-gari, cewa: “Haƙika ‘yan kama-wuri-zauna ba su yi ma ‘yan-garin da suka tarar kallon mutane, sai dai suna mai da su dabbobi ma sun fi su.”

Wannan bayani ya zo a cikin Littafi mai suna: *“A Brief Account of The Destruction of The Indies” na Bartolome de las Casas (Jan 1, 2009)*

## Me Musulmi Suka Aikata Lokacin da Suka Kama Sabbin Garuruwa?

## Musulmai Sun Mulki Ƙasar Andalus Tsawon Karni 8:



Musulmi sun mulki ƙasar Andalus (spain) tsawon shekaru 781, daga 711M zuwa 1492Miladiyyah, har ta zama cibiyar wayewar kan duniya, amma babu kiristan da aka tilasta wa shiga Musulunci, sai ma kiyaye musu haƙƙokinsu, da bunƙasa kasuwancinsu, da cibiyoyinsu na ƙasa da aka yi. Sa'annan kuma Musulmi suka kawar da zaluncin da ake yi ma Yahudawa a can kafin Musulunci ya buɗa ƙasar. Tarihi a cike yake da waɗannan tabbatattun abubuwa da suka faru.

Amma, a lokacin da Izabilawa da Farnandizawa suka yi nasara a kan Musulman Andalus, sai suka hana bayyana duk wata alama ta Musulunci, suka kuma kafa hukumomin bincike da leƙen asiri, don azabtar da duk wanda aka tabbatar yana cigaba da zama Musulmi, ko da kuwa a ɓoye ne.

Ƙarshe aka ɗaiɗaita Musulmi aka raba su da gidajensu. To, abu mafi ban mamaki ma, duk bai fi irin yadda aka kori Yahudawa ba tare da Musulmin, kuma daga ƙarshe Yahudawan suka nemi mafakar siyasa a sauran ƙasashen Musulunci, inda suka samu makoma, da aminci, da rayuwar mutunci da karimci.

## Musulmi Sun Mulki Ƙasar Masar Fiye Da Shekara 1400, Sun Kuma Kiyaye Wa Kibdawa Matsayinsu :




Tarihi ya tabbatar da irin yadda Musulmi suka mulki ƙasar Masar a farkon Musulunci, lokacin da Amru ɗan Ási, ɗaya daga cikin Sahabban Manzon Allah, *sallallahu alaihi wa sallam*, ya buɗa ta. Bai tsaya ga kare mutuncin addinai da manufofinsu ba kawai, har ma ceton su suka yi daga zalunci, da wulaƙanci, da azabar da Rumawa suke ɗanɗana musu, saboda saɓanin Mazhaba da ke tsakaninsu, tattare da cewa addini ɗaya suke a kai. Sa'annan kuma suka mayar wa Kibɗawa 'yancin gudanar da addini da ibadojinsu a wannan lokaci, wanda adadinsu a lokacin ya zarta miliyan biyar a kididdiga.

## Musulmi Sun Mulki Ƙasar Indiya Kusan Shekaru Dubu, Alhali 80% Na Mazaunan Ƙasar Ba Musulmai Ba Ne:



Musulmi sun mulki ƙasar Indiya na tsawon shekaru kusan dubu, amma suka kiyaye wa masu wasu addinai haƙƙoki, da ibadojinsu, sauran addinan da ba su da saƙat kuma, suka cece su. gaba ɗayan Masana tarihi sun bayar da tabbacin cewa, ba da kaifin takobi, Musulunci ya yaɗu ba, babu kuma wanda aka tilasta shigarsa.

## Mafi Girman Garin Da Musulunci Ya Shiga Ba Da Yaƙi Ko Runduna Ya Shige Shi Ba:



Ƙasar Indonesiya, ƙasa ɗaya a duniya, da Musulmi suka fi cincirindo a ciki, domin tana da yawan mutane miliyan 250, kashi 87% Musulumi ne. Musulunci ya samu shiga wannan ƙasar ne ta hanyar kyawawan halayen 'yankasuwa a ƙarni na shida bayan hijira; babu wata runduna ta Musulmi ɗaya, da ta kai wani ɗauki a can. Indonisiya ba ta san zubar da jini ba, sai lokacin da sojojin 'yan mulkin mallaka daga ƙasar Portugal, suka baƙunce ta, sannan Holland, sannan England.



# Tsakanin Musulunci Da Halayen Wasu Daga Musulmi na Yau

Wannan

Wannan wane irin tubka da war-wara ne mai ban takaici? Wannan ita ce kalmar da waɗanda sukan yi, bayan sun gane cewa shari'o'in Musulunci, suna kira ne zuwa ga kyawawan halaye da gina ƙasa, da amfanar da mutum, da yaɗa aminci tsakanin mutane, sannan suka duba gefensu, sai suka samu halayen wasu, da ke kiran kansu Musulmi sun sha ban-ban da abin da ya ƙunsa. Ko zai yiwu ace masu waɗannan halaye, da suka saɓa ma na Musulunci, su ne mabiya addinin, na gaskiya?

***Alal hakiƙa,* wannan lamari ne da ke haifar da ruɗani, da yake da buƙatar masu hankali su kalle shi da idon basira don samar da mafita.**

- Ba duk wanda yake karɓa sunan Musulunci, ko aka haife shi a cikin Musulunci ba, yake Musulmi tsantsa, da yake ƙanƙame Shari'o'insa. Akwai matuƙar ƙarancin fahimtar Musulunci da koyarwarsa da yawa a kewaye da mu. Daga cikin Musulmi akwai wanda bai san komai na Musulunci ba sai suna kawai.
- Ba zai yiwu ba, ta kowane hali, a jingina laifukan mutane ga addinansu ko mazhabobinsu. Ba kuma zai yiwu ba, ta kowane yanayi, a ce, zaluncin Hitler dalilin addininsa ne, ko a ce, addinin Kirista ya yarda da gallaza ma bil Adama, don kawai Hitler yana Kirista ba, ko a ce, aƙidar musun samuwar Allah, ta lazimta kisan mutane, domin Gojeif sterling ya kashe miliyoyin mutane, shi kuwa mulhidi ne. Duk waɗannan maganganu, inda za a yi su, to, ba su da tushe balle makama.
- Tarihi kuma cike da misalai, masu tsananin ƙayatarwa, da duk duniya ta shaida, da suke tabbatar da hakiƙanin Musulunci, da ruhinsa, da ilimi, da ci gaba, waɗanda suka cika shafukan tarihi a faɗin duniya, kama daga ƙasashen Indiya a gabas, da na Isbaniya a yamma. Har yau tasirin da ɓurɓushin waɗannan misalai bai gushe ba ana ganin su a kan mu. Su ne kuma suka zama wasu fitilun cigaban da muke da shi a yau, kamar yadda ake samun wasu ƙasashe, da suke yunƙurin kama ƙafar taragon cigaban zamani. Wannan, ba batun misalan ɗaiɗaiku ake yi ba, waɗanda suka yi fice a fannonan ilimi daban-daban a ƙasashen duniya mabambanta.
- Ba wanda zai iya jifa da binciken da ilmin likitancin zamani ya zo da shi, har ya hana ma kansa yin magani don kawai ya yi la'akari da miyagun likitocin da suke kewaye da shi. Babu kuma wanda zai ƙulla gaba da neman ilimi; ya hana 'ya'yansa zuwa Makaranta, don kawai ya san wasu Makarantu Malamansu sun tozarta wannan sana'a mai daraja. Ana lura ne da hakiƙanin abu ba da munanan misalai da aka jingina masa ba.

Amma, abin mamaki shi ne, tattare da irin miyagun hare-hare da ake kai wa Musulunci daga ɓangaren wasu da ke kiran kansu Musulmi, ko tantagaryar maƙiyansa. Har yau, wannan bai hana mafi yawan mutane iya hango Musulunci a matsayin wani tsaftataccen addini mai nagarta ba. Har yau kuma mutane, ba su daina yin tururuwa suna shiga wannan addini ba, daga gaba ɗayan ɓangaroran duniya.



> Babu wata hanya, da zai yiwu, a kama addini ko mazhabar da mutane ke bi, da laifin kurakuran da suke aikatawa.

> Babu watarana da za a wayi gari mutum ya haramta ma 'ya'yansa zuwa makaranta neman ilimi, wai don yana da masaniyar cewa, akwai wasu malamai da suka gurɓata wannan sana'a ta karantarwa. Ko akwai?

## Wata Sabuwar Farfajiya

Sau nawa kake kai wa da komowa wajen ɗaukar mataki, da amfani da wata dama don maslahar kanka. Amma, kuma har yanzu kana nan kana zargin kan naka a kan wannan kai wa da komowa.

Ko shakka babu, mafi girman mutuncin ɗan Adam, shi ne samun cikakkaen 'yancin fuskantar abin duk da ya tabbata yana da amfani a gare shi, ba tare da wani tsoro ko fargaba ba.

Idan tsayuwa ƙyam a cikin fuskantar wahalhalu da ƙalubalen rayuwa, ya zama wata jaruntaka da za a yabi wanda yayi a kuma kalle shi da wata ƙima. To, lalle jarumtakar ɗaukar mataki idan mutum ya ga maslaharsa a ciki, da jaruntakar amsa laifi idan gaskiya ta bayyna a fili, ta fi waccan girma sau da yawa. Domin, jaruntaka ce mai tunkarar son rai, mai cin nasara a kan ruɗi. Wanda ya yi ta zai ji alamar haka a ransa da jikinsa.

Kamar yadda ka yarda, ka ba wa kanka wannan dama, ta sanin ko meye Musulunci a taƙaice, ta hanyar maɓuɓɓugansa na asali. To, kar ka kasa yin cikakken tunani da nazari, da kaiwa da komowa a kan abin da ka karanta ɗin nan.

Idan tsarin wannan addini, da kyawunsa ya bayyana a gare ka. Amma, har yanzu ba ka gushe ba kana buƙatar ƙarin bincike, da tambaya game da haƙiƙanin Musulunci da darajojinsa. To, kana da cikakkiyar dama a gabanka, ta yin karatu da nazari da tattaunawa da tambaya. Sai dai farko abin da za ka yi, shi ne, ka buɗe wani sabon shafi a ranka, ka saka wannan karatu da ka yi, sa'annan ka ba zuciyarka cikakkiyar damar kallo da nazarinsa, ta fuskoki mabanbanta.







Muna godiya da alfahari, da jin daɗi a kan kulawarka, da karanta wannan littafi da ka yi. Muna kuma fatar ya hankaltar da kai, ta hanyar motsa waɗansu muhimman tambayoyi a cikin zuciyarka, ko ɗora harsashen wani tunani cikin ƙwaƙwalwarka, na yarda ko rashin yarda. Za mu kuma yi farin ciki, idan muka ji ra'ayinka, ko tambayarka, ko ƙalubalen da kake fuskanta. Muna kuma ba ka tabbacin za mu karɓi kowannensu da hannu bi-biyu, cikin jin daɗi da kulawa.

Don samun ƙarin wasu bayanai a kan Addinin Musulunci:

LAUNCHING CURiOSiTY JUST SCAN IT.!!

THISISLAM.net

Nuna Mana Abin Da Ka Sani

info@modern-guide.com

Hausa







- Ashe bai kamata a ce, ka damu da ka san addinin da aka fi yawan jayayya a kansa a kafafen yaɗa labarai da ke kusa da kai ba?..

- Ashe bai kamata a ce, ka ɗan tsaya kaɗan ba, don ka samu cikakkiyar masaniya kuma mai zurfin game da addinin da ya fi kowane addini, aka kuma fi yawan karɓarsa, kamar yadda ƙididdigar duniya ta nuna?..

- Ashe bai kamata a ce, kana jin wani irin daɗi ba, a duk lokacin da ka san wani abu game da ilimi, da wayewa, da al'adu, da falsafa da tsarin rayuwar wasu mutane da suke rayuwa tare da mu a wata duniya, da wani addini?

- Idan haka ne, me zai hana ka ɗan yi amfani da damar da kake da ita, ka karanta wannan littafi domin ka san tantagaryar abin da addinin Musulunci ya ƙunsa, na gaskiya, wanda aka cirato daga ingantattun tuwasu da asullansa. Sa'annan ka auna su da lafiyayyen hankali da tatacciyar basirarka. Me zai hana?

Idan kuma kana hangen haka ko akwai wani abu mai muhimmanci a cikinsa, ko mai ɗaukar hankali. To, wannan ko shakka babu wannan littafi zai ba ka agaji da gudunmawa ga biyan bukatarka.

9 786030 315055

LAUNCHING CURiOSiTY JUST SCAN IT.!!

MODERN GUIDE

THIS IS ISLAM

THISISLAM.info